# FARFAGANDA A WAQOQIN FIYANO NA HAUSA 2003-2013

**NA**

**ZAINAB ISAH**

**MA/ARTS/00533/2008-2009**

**Department of African Languages and Cultures,**

**Faculty of Arts,**

**Ahmadu Bello University, Zaria.**

**April, 2013**

# FARFAGANDA A WAQOQIN FIYANO NA HAUSA 2003-2013

**Na**

**ZAINAB ISAH**

**MA/ARTS/00533/2008-2009**

**A Thesis Submitted to the School of Post Graduate Studies, Ahmadu Bello University, Zaria.**

**In partial fulfillment of the requirements for the Award of Master of Arts**

**Degree in African Languages (Hausa)**

**Department of African Languages and Cultures,**

**Faculty of Arts,**

**Ahmadu Bello University, Zaria.**

**April, 2013**

## Dedication

I dedicate this work to my sweet mother, Hajiya Aishatu Ladan Baqi. May Allah, the Beneficent, the Merciful, the Exalted guide her throughout her lifetime. Words cannot express what you mean to me.

**Declaration**

I hereby declare that the work in this thesis titled "Farfaganda A Waqoqin Fiyano Na Hausa 2002-2013 (Propaganda In Contemporary Hausa Songs 2003-2013) was performed by me in the Department of African Languages and Cultures, under the supervision of Professor Xalhatu Muhammad And Dr. Muhammad Lawal Amin. The information derived from the literature has been duly acknowledged in the text and a list of references provided. No part of this work has been presented for another degree or diploma at any institution.

| --- | --- | --- |
| Zainab Isah | Signature | Date |

**Certification**

This thesis titled "(Farfaganda A Waqoqin Fiyano Na Hausa 2003-2013" Propaganda In Contemporary Hausa Poetry 2003-2013) meets the regulations governing the award of the degree of Masters of the Ahmadu Bello University, and is approved for its contribution to knowledge and literary presentation.

---------- ---------- ----------

Chairman, Supervisory Committee (Signature) (Date)
(Prof. Xalhatu Muhammad)

---------- ---------- ----------

Member, Supervisory Committee (Signature) (Date)
(Dr. Muhammad Lawal Amin)

---------- ---------- ----------

Head of Department (Signature) (Date)
(Dr. Balarabe Abdullahi)

---------- ---------- ----------

Dean, School of Post Graduate Studies (Signature) (Date)

(Prof. Adebayo A. Joshua)

# GODIYA

Kyakkyawar godiya ta tabbata ga Allah Maxaukakin Sarki, Wanda Ya yi rantsuwa da alqalami da abin da (marubuta) suke rubutawa. (Qur'an 68:1). Sannan Ya wajabta neman ilmi, kuma Ya samar da shi a vangarori da dama. Ya kuma xaukaka harshen Hausa har ake nazarinsa a wasu sassa na duniya. Tsira da amincin Allah su tabbata ga Manzonmu, Annabi Muhammad da Alayensa da Sahabbansa baki xaya.

Ina godiya ga mahaifiyata Hajiya Aishatu Ladan Baqi, saboda kulawa da xawainiya da haquri ba gazawa. Allah Ya yi mata sakayya da aljannar Firdausi, amin.

Kyakkyawar godiya ta musamman kuma kevantacciya ga malamaina abin alfaharina waxanda suka jagoranci duba wannan aiki, Farfesa Xalhatu Muhammad da Dr. Muhammad Lawal Amin. Sun bayar da cikakken lokacinsu, duk da hidimomin da ke gabansu, da shawarwari don ganin an yi wannan aiki cikin nasara ingantatta. Ina tinqaho da zama qarqashinsu. Na gode da qoqarinsu. Allah Ya yi masu sakayya da mafificin alheri.

Godiya da ba za ta qirgu ba zuwa ga Shugaban Sashen Harsuna da Al'adun Afirka kuma jagora Dr. Balarabe Abdullahi, shi ma ya taimaka matuqa. Allah ya biya shi. Godiya marar iyaka ga Dr. Shu'aibu Hassan saboda rashin qosawa da ni. Ya taimaka mani matuqa, jazakallah. Malam Abubakar Ayuba shi ma ya taimaka, na gode qwarai.

Godiya ta musamman ga malaman Sashen Harsuna Da Al'adun Afirka. Malam Adamu Malumfashi, Dr. M.Y. Tsoho, Dr. Salisu Kargi, Farfesa Munir, Dr. Bello Alhassan, malam Sarki, malam Tahir, malama Hauwa Bugaje da Malama Halima Kabir Daura da malam Shu'aibu Abdulmumin. Sauran malamai gaba xaya, na gode da yabawarsu.

Godiya ga abokanan aikina na Jami'ar UMYU Katsina irin su Shugaban Sashen Harsunan Nijeriya Farfesa Sabry Salama, Dr. Bashir Sallau (Sarkin Aska), malama Salima Sulaiman Isa, malam Sirajo Ibrahim, malam Mustafa Shu'aibu, Dr. Aminu Vatagarawa, AbdulRazaq Sulaiman da Dr. Aminu Muri na Sashen Tarihi. Farfesa Abdulqadir Xangambo shi ma ya taimaka.

Ba za ni manta da abokan karatuna ba kamar su Hadiza Alqasim, Binta Musa Hassan, Abdulqadir Xan Alhaji, Garba Lawal, Sufiyanu Bayero, Kuta, da Murtala Adamu. Su ma agaishe su. Mawaqan da aka yi nazarin waqoqinsu kamar su Aminu Ala da Haruna Ningi da Jibrin Jalatu da AbdulAziz Ningi da Muhammad Sani Aliyu. Na gode da lokacin da suka bayar, har aka yi hira da su. Allah Ya qara fasaha da balaga a rera wasu waqoqin don bunqasa adabin Hausa.

'Yan'uwan irin su Sada, Asiya, Bello, Amina, Anty Gaje da Muhammad, Halimatu, da Khalifa su ma na yaba da kulawarsu. Allah ya saka masu da alhairinsa, amin. Sauran 'yan uwa da abokan arziqi, na gode qwarai.

QUMSHIYA

Title Page Shafi

Cover Page----------i

Cover Page----------ii

Dedication----------iii

Declaration----------iv

Certification----------v

Godiya----------vi-vii

Qumshiya----------viii-xi

Abstract----------xii

Tsakure----------xiii

Babi Na Xaya: Shimfixa----------1

1.0 Gabatarwa----------1-6

1.1 Manufar Bincike----------6-7

1.2 Dalilin Bincike----------8-10

1.3 Muhimmancin Bincike---------- -11-13

1.4 Hasashen Bincike----------13-14

1.5 Iyakacin Bincike----------14-15

1.6 Kammalawa----------16

Babi Na Biyu: Waiwaye----------17

2.0 Gabatarwa----------17

2.1 Kundayen Bincike----------17-37

2.2 Muqalu----------38-65

2.3 Bugaggun Littattafai---------- 65-85

2.4 Waqoqin Farfaganda---------- 86

2.5 Samuwar Waqoqin Fiyano Na Hausa---------- 87-89

2.5.1 Kixan Fiyano---------- 89-91

2.5.2 Asalin Kixan Fiyano---------- 92

2.5.3 Nau'in Kidan Fiyano---------- 92

2.5.3.1 Rap Ko Rapping---------- 92-93

2.5.3.2 Reggae---------- 93

2.5.3.3 Hip Hop ---------- 94

2.6 Muhallan Da Ake Waqoqin Fiyano Na Hausa---------- 94

2.6.1 Fina-Finan Hausa---------- 94-96

2.6.2 Tarukan Siyasa ---------- 96-99

2.6.3 Bukukuwa ---------- 99

2.6.4 Bukukuwan Aure Da Na Raxin Suna ---------- 100

2.6.5 Bukukuwan Addini ---------- 100-101

2.6.6 Majalisi ---------- 102

2.6.7 Tallace-Tallace---------- 102-103

2.6.8 Kafofin Yaxa Labarai ---------- 103-104

2.7 Mawaqan Hausa Masu Amfani Da Fiyano---------- 104-105

2.8 Waqoqin Hausa Na Fiyano ---------- 106

2.9 Gudunmuwar Waqoqin Fiyano Na Hausa ---------- 107

2.10 Kammalawa ---------- 107

Babi Na Uku: Hanyoyin Gudanar Da Bincike---------- 108

3.0 Gabatarwa---------- 108

3.1 Garuruwan qasar Hausa Da Aka Ziyarta Don Nemo Bayanai A kan Wannan Aiki--- 108-109

3.2 Mawaqa Masu Amfani Da Fiyano A qasar Hausa---------- 109-111

3.3 Maqasudin Zabo Mawaqan Da Aka Yi Amfani da Waqoqinsu---------- 112-114

3.4 Shekarun Da Aka Aiwatar Da Waqoqin---------- 114

3.5 Hanyoyin Da Aka Bi Aka Samo Waqoqin---------- 115-117

3.5.1 Ziyartar Sitidiyo---------- 117-119

3.5.2 Gidajen Yada Labarai---------- 119

3.5.3 Mutanen da aka Yi Hira da su ---------- 120

3.5.4 Dakunan Karatu Da Aka Ziyarta---------- 121-122

3.6 Muhawar Masana Dangane da Matsayin Waqoqin Hausa a Yanzu da Ra'in da aka Dora Bincike a Kai---------- 122-130

3.6.1 Matsayin Waqoqin ga Masu yin su---------- 131-133

3.6.2 Ra'in Bincike----------133-135

3.7 Yadda aka Gudanar da Aikin bisa Tsari---------- 135-136

3.8 Kammalawa---------- 136

Babi Na Hudu: Farfaganda A Waqoqin Fiyano Na Hausa---------- 137

4.0 Gabatarwa---------- 137-139

4.1 Tarihin Aminu Ladan Abubakar Ala---------- 139-140

4.1.1 Dalilin Rubuta Waqar Baubawan Burmi Da Bubukuwa Da Xaurin Gwarmai------- 140-143

4.2 Tarihin Jibrin Muhammad Jalatu---------- 144

4.2.1 Dalilin Rubuta Waqar Mafarkin Mulki I Da II da Ku Yi Hakuri---------- 144-146

4.3 Tarihin Haruna Aliyu Ningi---------- 147

4.3.1 Dalilin Rubuta Wakar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba da Kada Mu Dauki Siyasa Da Zafi Da Hawaye----------147-150

4.4 Tarihin Abdulaziz Abdullahi Ningi----------150

4.4.1 Dalilin Rubuta Waqar Rigar 'Yanci----------151

4.5 Tarihin Muhammad Sani Aliyu----------151-152

4.6 Takaitaccen Tarihin Siyasa A Nijeriya----------153-156

4.7 Samuwar Waqoqin Farfaganda Na Fiyano----------157-159

4.8 Me Ya Sa Aka Kira Su Wakokin Farfaganda----------159-160

4.9 Farfaganda A Waqoqin Fiyano na Hausa----------160-170

4.10 Waqoqin A Inuwar Farar Farfaganda----------170-172

4.11 Yanayin Gudanar da Mulki----------173-220

4.12 Addini----------220-237

4.13 Tattalin Arziki----------237-245

4.14 Zamantakewa----------245-262

4.15 Kammalawa----------263-264

Babi Na Biyar: Nadewa

5.0 Gabatarwa----------265

5.1 Takaitawa----------265-266

5.2 Kammala----------266-274

5.3 Shawarwari----------274-276

Manazarta----------277-290

Rataye----------291-398

Abstract

This research examines the theme of propaganda in some of the contemporary Hausa songs which are composed with foreign musical instruments such as piano or guitar are inclined towards political propaganda. The songs are not concerned with political parties on their own merit but on the conduct of governance generally. The songs play a role in educating and enlightening people on how they are being governed or how they are supposed to be governed. They also tend to incite people to violence in protest against bad governance. The songs nowadays are being composed increasingly around the themes of governance, religion, economic development and inter-group relations in Nigeria. To this end, the research attempts to examine the songs with a view to show how they influence the attitude of people in relation to their political choices. Chapter one is the general introduction, it outlines the aims, the purpose, the significance, the hypothesis and the scope of the study. Chapter two focuses on the literature review related to the study. The third chapter is the research methodology. The fourth chapter examines the theme of governance, religion, economic development and inter-group relations in Nigeria. Chapter five is the concluding part and summarizes the whole work. It comprises summary, recommendations, references and appendix.

## Tsakure

Wasu daga cikin waqoqin da ake yi na zamani, wanda ake aiwatarwa da kayan kixa na zamani irin fiyano da jita, waqoqi ne na farfaganda ta siyasa. Waqoqin ba su maganar jam'iyyu amma suna magana kan yadda ake gudanar da mulki. Waqoqin suna taka muhimmiyar rawa wajen faxakar da mutane kan yanayin yadda ake mulkinsu. Don waqoqin na qoqarin sauya tunanin jama'a, suna kira zuwa ga bore da tawaye ga shuwagabanni. Waqoqin farfaganda da ake yi a siyasance sun jivanci wasu manyan rassa guda huxu, yanayin yadda ake gudanar da mulki, da addini, sai tattalin arziqi da zamantakewa. Don haka, wannan bincike ya yi nazarin irin waxannan waqoqi don ganin yadda suke isar da saqonsu. Babi na xaya ya qunshi gabatarwa, sai manufar bincike, da dalilin bincike da kuma muhimmancinsa. Sai hashashen bincike da iyakacin bincike. Babi na biyu, bita ne a kan ayyukan da suka gabata, masu alaqa da wannan aiki. An waiwayi waqoqin farfaganda xin. An duba samuwar waqoqin *fiyano* na Hausa. Babi na uku, dabaru da hanyoyin gudanar da bincike. Sai babi na huxu aka kawo taqaitaccen tarihin mawaqan tare da bayanin abin da ya haifar da samuwar waqoqi na farfaganda, tare da dalilin da ya sa aka kira su waqoqin farfaganda. An yi maganar manyan rassa huxu da waqoqin nan suka yi magana a kai. An kawo yadda waqoqin suka yi maganar yanayin gudanar da mulki da addini, an yi bayanin tattalin arziqi da yanayin zamantakewar 'yan Nijeriya. Babi na biyar ya naxe aikin duka, ya qunshi shawarwari da manazarta da rataye.

## BABI NA XAYA

## SHIMFIXA

### 1.0 Gabatarwa

Siyasa na da muhimmancin gaske ga rayuwar al'umma baki xaya, musamman idan aka lura cewa wata aba ce wadda take bai wa jama'a wata dama ta walwala da ma samun 'yanci, idan aka kwatanta ta da mulkin soja. Siyasa na da matsayi mai girma ga kowace al'umma, saboda irin wannan matsayi nata, sai mutane suka riqa yi mata hidima iri-iri. Daga cikin hidimomin da ake wa siyasa a qasar Hausa akwai waqa, wadda za a iya cewa ta fi alfanu kuma da ake yi da manufofi kala-kala. Waqa na da muhimmanci sosai a fagen siyasa, don alfanunta da tasirinta ba zai misaltu ba, domin wata hanya ce ta isar da saqo cikin sauqi, mutane sukan zave ta domin cimma burinsu na ilmantarwa da faxakarwa da nishaxantarwa da sauran makamantan haka.

Farfaganda wani shiri ko tsari ne da ake yi da nufin canza ko sauya tunani ko wata aqida ta jama'a. A yaxa wasu labaru na gaskiya ko jita-jita domin a samu tasiri kan tunanin al'umma. Wata tsararriyar hanya ce ta yaxa ko baza wata aqida ko manufa da nufin canza tunanin jama'a kan wata manufa ko aqida.

An daxe ana amfani da waqa domin a isar da saqo da kuma yaxa manufofi a qasar Hausa. Waqa ta samu musamman rubutatta sanadiyar yaxa manufa ta addinin Musulunci. Ma'ana waqoqin qarni na sha-tara, da aka yi don yaxa addinin Musulunci. Waqoqin masu jihadi da suka yi don kira zuwa ga tafarkin Allah. Funtua (2011) ya bayyana cewa su Xangambo (2007) da Yahaya (1988) sun jaddada cewa waqoqin siyasa na Hausa sun fara samuwa tun lokacin jihadin Shehu XanFodio, misali idan aka dubi waqar *Murnar Cin Birnin Alqalawa* da waqar *Yaqin*

*Kalambaina* na Abdullahi Fodio. Baya ga waxannan waqar *Tsarin Mulkin Musulunci* ta Abdullahi Bn Fodio, waqa ce siyasa da ta warware komai dangane da yadda tsarin mulkin Musulunci yake.

Baya ga waqoqin qarni na sha-tara, a qarni a ashirin an yi wasu. Kafin haka, akwai waqar *Zuwan Annasara Qasar Hausa* ta sarkin Musulmi Attahiru Amadu, da ya yi a farkon qarni na ashirin. Har wasu malamai na kiranta da kadarkon waqoqin qarni na sha tara da ashirin. Ita ma waqa ce da aka yi da nufin canza tunanin jama'a, don jawo hankalin mabiya kada a amince da zuwan Nasara qasar Hausa.

A lokacin Turawan mulkin mallaka, an yi farfaganda sosai, don a cimma wasu manufofi. A jaridu an rubuta waqoqi na farfaganda don a nuna muhimmancin noman gyaxa, da haqar kuza, don lokacin babu maganar fetur.

An ci gaba da hidimomin siyasa, an kakkafa jam'iyyun siyasa wanda aka riqa gudanarwa yadda ya kamata. A qoqarin tabbatar da haka, an yi waqoqin farfaganda ana isar da wasu manufofi kala-kala da al'ummar qasa, musammam a lokacin yaqin neman 'yancin kai. A lokacin an rubuta waqoqi ana wayar da kan mutane kan irin nau'in mulkin da ya kamata a yi. Su ne waqoqin su Sa'adu Zungur kamar waqar *Arewa Jumhuriya Ko Mulukiya*. Wasu waqoqin an yi su ne a kan zuwan Turawa da abin da suka zo da shi. Wasu waqoqin na nuna a guje wa Turawa. Wasu waqoqin kuma na'am suka yi da sabon sauyin da aka samu. Haka dai aka ci gaba da rubuce-rubuce na waqoqin farfaganda a kan jam'iyyun siyasa da sauran manufofi iri-iri.

A qasar Hausa, waqa  wata hanya ce ta isar da saqo, don Hausawa sun riqe ta tun zamani mai tsawo, suna amfani da ita, suna isar da manufofinsu da saqonninsu ga jama'a. Har ya zuwa yanzu, wato lokacin nan da aka kaxa kugen siyasa, waqa abar yabo ce domin an lura cewa siyasa ba ta armashi, sai an haxa ta da waqa. Wato dai a ce waqa wata makamashi ce ta siyasa. Wasu mawaqan siyasar, suna rubuta waqoqin ne domin tallata jam'iyya da kwarzanta xan takara, yayin da wasu zambo da habaici kan zama jigogin waqoqin nasu. Wasu kuwa, yanayin da ake gudanar da mulkin ne bai gamshe su ba,  sai su rubuta waqoqi na farfaganda suna ilmantar da mutane da kuma faxakar da su, kan yadda ake gudanar da mulki.

Ganin cewa waqoqin da ake yi a yanzu, waqoqi ne da zamani ya kawo waxanda ake amfani da kayan kixa na zamani irin su jita da fiyano da tasoshi wajen aiwatar da su. Sannan, waqoqi ne da suka samu karvuwa a qasar Hausa, musammam a wajen matasa, samari da 'yan mata. Haka kuma, waqoqi ne masu mabambantan jigogi don wasu daga cikinsu suna magana ne kan soyayya, wasu yabon Annabi da sauran jigogi da dama. A irin haka ne, aka rinqa yin wasu waqoqi na farfaganda a fakaice, ana ankarar da mutane da su lura, su san in da kansu ke yi masu ciwo a kan irin nau'in mulki da ake yi. Sannan waqoqin suna bijire wa gwamnati matsawar dai ba za a yi riqo da gaskiya ba.  Irin waxannan waqoqi sun yi kama da waqoqin mazan jiya, waqoqin su Sa'adu Zungur da ke farfaganda, suna faxakar da mutane kan yanayin yadda ake gudanar da mulki a wancan lokacin.

A zamanin da ake ciki, an yi waqoqi waxanda ba na jam'iyyun siyasa ba, amma kuma waqoqin suna magana kan siyasar qasa wato yadda ake tafiyar da rayuwar al'umma, yadda ake mulkin

jama'a cikin gadara ba tare da bin haqqinsu ba. Irin waqoqin suna bore da tawaye da bijire wa tsarin mulkin qasar nan. Su ne waqoqin da ake yi na farfaganda.

Irin waqoqin farfaganda da ake yi yanzu, sun xan sha bamban da waxanda suka gabata. Waxanda ake yi a da, sun fi maganar siyasa dangane da addini. Na yanzu sun fi mayar da hankali kan tattalin arziqi, da qabilanci, da yanayin zamantakewa, da addini.

Farfaganda wani fage ne wanda ba a cika ba shi muhimmanci sosai ba, ko ma a ce aikin da aka yi a kansa bai taka kara ya karya ba. Ga shi irin waxannan waqoqi na farfaganda, waqoqi ne masu muhimmancin gaske. Marubutan sukan yi nazarin abin da ke faruwa a tsakanin al'umma, sai su nuna qyamarsu, wasu kuma hanyar tafiyar da mulkin ne suke ganin ba daidai ba. Sai su rubuta waqa a kan haka, suna ankarar da mutane tare da cusa ra'ayi don a guji wannan gwamnati.

Bugu da qari, wannan bincike ya yi nazarin farfaganda a waqoqin fiyano na Hausa, waqoqin da ake yi da abin kixa irin su fiyano, da jita da wanda ba su da alaqa da jam'iyyun siyasa, amma suna magana kan siyasar qasa, masu farfaganda suna nuna tawaye ga shuwagabanni.

Daxin daxawa, ganin yadda waqa ke da muhimmanci a wajen Hausawa, shi ya sa maza da mata, yara da manya a fagen ilmi suke ta karakaina wajen nazarinta, amma nazarin waqoqi irin na farfaganda ba su samu gata ba sosai a wajen manazarta, saboda haka, a iya cewa wannan bincike

yana xaya daga cikin bincike na farko farko a wannan layi. Don haka za a yi qoqarin nazarin waqoqin don qara fito da muhimmancin da ke tattare da su.

## 1.1 Manufar Bincike

An yi wasu waqoqi na zamani, waqoqin an yi su ne don farfaganda zuwa ga al'umma, ana wayar masu da kai kan yanayin yadda ake mulki a qasa. Saboda haka, binciken zai zaqulo ire-iren waxannan waqoqi na farfaganda, ya yi nazarinsu dalla-dalla, kamar yadda al'adar nazari ta tanada.

i. Manufar wannan bincike, don a nazarci hoton siyasar Nijeriya da tattalin arziqin qasa da kuma zamantakewa da addini kamar yadda suka bayyana a cikin waqoqin. Har wayau, binciken zai ayyana matsalolin da Nijeriya take fuskanta ta vangaren tattalin arziqi, zamantakewa da siyasa da maslahan da marubutan suka kawo cikin waqoqin, domin 'yan Nijeriya su farga, ko su ci gaba da yin varnar ko kuma su gyara kamar yadda wasu waqoqin suka kawo mafita.
ii. Manufar wannan bincike shi ne tabbatar da qaulin nan da ke cewa adabi matsokaci ne na rayuwar al'umma, domin mawaqan na tsokaci ne a kan abin da ya shafi rayuwarsu da ta sauran jama'a.
iii. Yana daga cikin manufar wannan bincike, fito da matsayin waqa a qoqarin ta na wayar da kan jama'a musamman a kan harkokin siyasa.
iv. Kamar yadda manazarta adabi suke cewa, adabi madubi ne na rayuwar al'umma, don haka duk wani aiki da aka yi na adabi, zai zama wani tsani na binciko wani abu na wannan al'ummar da aka yi aikin a kanta. Don haka, yana xaya daga cikin manufar wannan aiki, gano manufar mawaqan da suka yi waqoqin.

v. Manufar wannan bincike ne gano abin da ya haifar da samuwar waxannan waqoqi na farfaganda a wannan zamani. Watakila mutane sun fara farga da abin da ke faruwa a qasa kuma sun rasa hanyar da za su bi domin ganin an samu sauyi, shi ne suke amfani da waqa suna yaxa manufofinsu, suna tunzura jama'a da nufin su yi tawaye ga shuwagabanni.

vi. Wata manufar kuma, domin a fito da wasu abubuwa ginshiqai a cikin waqoqin da ta yiwu ba a san su ba, ko an san su watakila ba a fahimce su yadda ya kamata ba, misali kamar sanin arziqin qasa don haka ne jama'a za su san inda aka tsaya, inda za a tashi ta haka ne za su gane inda aka dosa a kan sha'anin mulki.

vii. Har wayau, manufar ita ce domin a fito da irin gudunmuwar da marubutan suke bayarwa wajen wayar da kan jama'a. Ganin yadda waqoqin suke samun karvuwa, watakila, saqon nasu ma yana samun gamsuwa ga jama'a.

**1.2 Dalilin Bincike**

Babu shakka! A duk lokacin da aka yi niyyar gudanar da wani abu, alal haqiqa akwai dalili ko dalilai da suka tunzurar da maniyyaci a kan aikin da ya yi niyyar yi. Yana daga cikin dalilaina cewa:

i. Ganin irin yadda ake ta samun yawaitar waxannan waqoqi na zamani a kullum. Kuma an fahimci cewa, waqoqin na taimakawa qwarai wajen ci gaban dimokraxiyya a Nijeriya. Shi ya sa aka yi nazarin wasu, don a fito da saqon da suke qoqarin isarwa.

ii. An yi nazarce-nazarce dama a kan waqoqin siyasa, sai aka lura cewa an watsar da wannan fanni na farfaganda kuma da wuya a yi harkar siyasa a gama ba tare da yaxa wata manufa ba, wato da wuya a yi siyasa a gama ba tare da an yi farfaganda ba. Shi ya sa aka ga ya dace a yi nazarin farfaganda a vangaren da ta dace, wato vangaren siyasa.

iii. Yawancin waqoqin siyasa da a kan yi, za a tarar cewa an fi yabon jam'iyya da muqarrabanta sai kushe ga abokanan hamayya. Wato ba a cika faxakar da mutane ba kan yanayin yadda ake gudanar da mulki wanda kuma shi ne muhimmi a lokacin nan da ake ciki. Inda kuma aka iske an yi haka, to kuwa a kan manufofin jam'iyya ne. Sai aka lura cewa an fi irin wannan faxakarwar a waqoqin siyasa da ba na jam'iyya ba, irin waqoqin da aka yi nazarinsu, kuma irin waqoqin suna tavo kowane vangare na harkokin qasa, kamar zamantakewa da tattalin arziqin qasa, da addini. Waqoqin za su taimaka wajen wayar da kan jama'a.

iv. Haka nan kuma, xalibai manazarta ba a cika kallon matsalolin da ke faruwa a qasar nan ba, a ce za a yi zuzzurfan nazari a kai da nufin shawo kan matsalolin. Sai dai alal misali, a xauki salo a yi nazarinsa, ko a xauki wani mawaqi da wasu waqoqinsa ko nazarin nahawu da kwatanta na harshen Hausa da na wani harshe da sauran makamantan haka, inda kuwa aka samu an yi nazarin waqoqi, sai a tarar da cewa yanaye-yanayensu aka fi dubawa. Bincike irin wannan wanda ya shafi rayuwar al'umma, yana da matuqar amfani sosai, domin zai tsuma xalibai kai har ma da malamai wajen ganin an samu canji a yanayin mulkin qasa.

v. An lura kuma cewa, yanzu an daina yaqi da makami sai da alqalami, wannan yaqin da ake yi da alqalami yana nan tattare da waxannan waqoqi masu bore da tawaye da kuma bijire wa mulkin Nijeriya da masu yinsa. Nazarin waqoqin zai taimaka sosai wajen ilmantar da jama'a.

vi. Yana da kyau a taskace irin waqoqin domin ta hanyar nazarinsu ne zai sa ba za a manta da su ba. Har wayau kuma, binciken zai bai wa waxanda ba su san su ba, damar fahimtar su, waxanda suka fahimce su kuma, za su qara tunawa da su.

vii. An zavi a yi nazarin waqoqin siyasa na zamani wanda ba na jam'iyya ba, saboda yadda suke da tasiri a zukatan jama'a da irin karvuwar da suka samu wato dai ana ganin cewa sun fi bayar da gudummuwa fiye da waqoqin siyasa na jam'iyya. Su na jam'iyyun siyasa, alal haqiqa, ba ya ga nishaxantarwa, sun fi ta'allaqa wajen yabo da zambo, inda su kuwa irin waxannan da ake nazari suke qoqarin ilmantarwa. Duk da dai wani lokaci ba za a rasa yabo da zambo a cikinsu ba.

viii. Waxannan mawaqa da aka zava domin a yi nazarin waqoqinsu, kusan za a iya cewa suna daga cikin shahararrun mawaqan zamani ta fuskar balaga da zalaqa da ma fasaha ta shirya waxannan waqoqi. Mawaqan da aka zava domin nazarin waqoqinsu su ne: Aminu Ladan Abubakar (Ala) da Haruna Aliyu Ningi da Jibrin Muhammad Jalatu da AbdulAziz Abdullahi Ningi da Muhammad Sani Aliyu. Kuma sun rayu a mabambantan wurare. A lokacin da wasu mawaqan suka mayar da hankali a kan wasu fagage, su sai suka mayar da hankali wajen faxakarwa, suna yaxa manufofinsu da zummar jan hankali. Haka kuma, waqoqin sun yi fice a qasar Hausa ta irin saqon da suke isar wa har a kan sanya su a gidajen rediyo domin irin farfagandar da suka qunsa.

### 1.3 Muhimmancin Bincike

Kamar kowane bincike da ake yi, a kan yi shi ne domin zaqulo wasu abubuwan masu muhimmanci da ta yiwu ba a sani ba da farko, idan kuwa an sani, watakila ba a gane ba sosai da sosai. A don haka, muhimmancin wannan bincike shi ne:

i. Don a fito da matsayi da muhimmancin waqa wajen havvaka mulkin dimokraxiyya.

ii. Ana fatan wannan bincike ya zama mai amfani ga masu nazarin Kimiyyar Siyasa. Don za a samu jituwa tsakanin fagagen. Binciken zai qara haskaka jituwa tsakanin manazarta adabi da kimiyyar siyasa. Manazarta adabi su nazarci abubuwa da za su gina al'umma. Masu nazarin kimiyyar siyasa su nazarci abin day a shafi adabi.

iii. Ana kuma fatan wannan aiki zai zama mai fa'ida ga manazarta Tarihi, wato ta yadda aka samu canji a yanayin siyasar Nijeriya, har ya haifar da samuwar waqoqin shi ma zai shiga cikin tarihin Nijeriya. Wannan zai qara taimakawa wajen adana tarihi.

iv. Su ma manazarta Addini, ana kyautata zaton zai zama mai inganci a wurinsu, don sanin hanyar da ta fi dacewa wajen kyautata wa al'umma.

v. Manazarta adabi, su ma za su ci gajiyar wannan aiki, don aikin ya tavo wani ginshiqin sashe na adabi, wato waqa. Ko a cikin rabe-raben adabi, manazartan suna ji da waqa, don a iya cewa, an fi yi mata hidima fiye da sauran dangoginta. Sannan kuma, yadda aka samu cakuxuwar nau'o'in waqoqin Hausa a wuri xaya, shi ma wani ci gaban adabi ne.

vi. Ga Hukuma ma, wannan aiki ya zama mai fa'ida, domin ta irin waxannan nazarce-nazarce ne Hukuma za ta san yadda jama'a ke kallonta, wato yadda take gudanar da harkokin mulki. Ana kuma sa ran samun canji da taimakon ire-iren waxannan bincike.

vii. Ga manazarta al'ada kuwa, wannan bincike ya zama mai daxi a gare su, yadda aka samu sauyin xabi'un Hausawa, musamman yadda Hausawa suke yin waqoqin

nan na farfaganda suna bijire wa gwamnati, bayan an san Hausawa da kawaici da kunya.

viii. Ana sa ran wannan bincike zai zama jagora ga marubuta masu son wannan fanni da su qara qoqari wajen binciken abubuwa da suka danganci siyasa domin inganta mulkin dimokraxiyya a qasa.

ix. Wata fa'idar ita ce, domin irin rawar da waqoqin da mawaqan ke takawa wajen wayar da kan jama'a cikin ruwan sanyi. Yana da muhimmanci a yi nazarin waqoqin domin irin gagarumin yaqin da suke yi wanda da wuya a samu wata hanya mai fa'ida irin wannan.

x. Ga sauran jama'a, ana sa ran binciken ya zama mai tarin albarka.

## 1.4 Hasashen Bincike

Waxannan waqoqi da aka yi nazari a kansu na farfaganda, waqoqi ne da ake aiwatarwa da kayan kixa na zamani kamar jita da fiyano. Don haka, hasashen wannan bincike shi ne:

Bincike ya nuna cewa haqiqa jama'a na matuqar qaunar waxannan waqoqi. Hasali ma dai waxannan waqoqi za su zaburar da jama'a da tsuma su game da siyasa. Watakila ma su kangarar da su, don an yi waqoqin ne don a jawo hankalin jama'a su hankaltu, su san inda aka dosa a yanayin mulkin Nijeriya. Don haka ake fatan samun sauyi a siyasar Nijeriya. An yi waqoqin domin a tsuma mutane, don haka waqoqin na kira da a yi bore da tawaye da bijire wa shuwagabannin Nijeriya matsawar ba za a yi riqo da gaskiya ba.

Binciken zai haifar da kyakkyawar rayuwa ga al'ummar Nijeriya, don ana sa ran a samu canji da taimakon ire-iren waxannan bincike. Binciken zai taimaka wa jama'a sosai idan an samu sauyi da canji a siyasar Nijeriya. Waqoqin a kullum sai qara yawaita da havaka suke yi. Mutane na fahimtar abin da ke faruwa a rayuwa, musamman ta siyasa, kuma sun ci gaba da yin irin waxannan waqoqi na farfaganda. Abin da ke faruwa a siyasar Nijeriya yana qara sa jama'a su rubuta irin waxannan waqoqi, ta haka ne waqoqin ke qara kangarar da jama'a don suna tunkarar al'amurra kai tsaye.

Ta haka ne jama'a za su san 'yancinsu, da qoqarin ganin an samu canji da gaugawa. A kuma samu kyakkyawan shugabanci a Nijeriya.

Nazarin zai taimaka wa hukuma, don ta haka ne hukuma za ta san yadda jama'a ke kallonta. Da fatan samun gyara a yanayin mulkin Nijeriya.

### 1.5 Iyakacin Bincike

A farfajiyar wannan bincike, an yi nazarin waqoqin farfaganda na Hausa. Waqoqin da ake yi da kayan kixa na zamani irin fiyano da jita masu alaqa da farfaganda wato waqoqin da ba su da alaqa da jam'iyyun siyasa, amma suna magana kan siyasar qasa. Masu qoqarin sauya tunani da ra'ayin al'umma zuwa ga bore da tawaye ga gwamnati kan yanayin yadda ake gudanar da mulki. An aiwatar da wannan bincike kawai a kan ire-iren waxannan waqoqi. Wato dai a ce an nazarci farfaganda a waqoqin fiyano na Hausa. Gusau (2008) ya nuna cewa a shekarar 1982 zuwa1984

irin waxannan waqoqi suka fara kankama, daga nan waqoqin suka xan fara bazuwa. An ci gaba da samun irin waxannan waqoqi, a kai a kai, har zuwa shekarar 2000, inda jama'a suka fara sabawa da waxannnan kaxe-kaxe na fiyano da ake tsarmawa a cikin fina-finai.

A wannan aiki mai suna *Farfaganda A Waqoqin Fiyano Na Hausa* an yi nazarin waqoqi kamar haka:

i. Waqar *Baubawan Burmi* ta Aminu Ladan Abubakar (ALA)

ii. Waqar *Bubukuwa* ta Aminu Ladan Abubakar (ALA)

iii. Waqar *Xaurin Gwarmai* ta Aminu Ladan Abubukar (ALA)

iv. Waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* ta Haruna Aliyu Ningi

v. Waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi* ta Haruna Aliyu Ningi

vi. Waqar *Hawaye* ta Haruna Aliyu Ningi

vii. Waqar *Mafarkin Mulki I* ta Jibrin Muhammad Jalatu

viii. Waqar *Mafarkin Mulki II* ta Jibrin Muhammad Jalatu

ix. Waqar *Ku Yi Haquri* ta Jibrin Muhammad Jalatu

x. Waqar *Rigar 'Yanci* ta AbdulAziz Abdullahi Ningi

xi. Waqar *Almajiri* ta Muhammad Sani Aliyu

**1.6 Kammalawa**

A wannan babi, an yi bakandamiyar shimfixa da ta shafi dukkan abin da za a duba a aikin. Sai manufar bincike, wato inda aikin ya dosa. An kawo dalilan da suka haifar da wannan bincike. An zayyana muhummancin binciken, wanda ake sa rai zai amfana ga kowa da kowa. An kawo hasashen bincike wanda ake fatan zai haifar da kayakkyawar rayuwa ga jama'a. Sai iyakacin

bincike, mai nuna iya inda bincike zai duba ko ya tsaya. Binciken iyakarsa ga waqoqin fiyano na Hausa, masu farfaganda wanda ba su maganar jam'iyyun siyasa amma suna maganar yanayin mulkin Nijeriya da tattalin arziqi da zamantakewa da addini. An zavo mawaqa guda biyar tare da waqoqi goma sha xaya aka yi nazari.

## BABI NA BIYU

## WAIWAYE

### 2.0 Gabatarwa

A babin da ya gabata an yi shimfixa kan muhimman abubuwan da suka danganci aikin. A wannan babin kamar yadda sunansa ya nuna, za a yi waiwaye da bitar ayyukan da malamai da manazarta suka yi, masu alaqa ta kusa da ta nesa da wannan aiki. Don waiwayen ya inganta, an duba kundayen digiri har da digirgir. Sai muqalu da bugaggun littattafai. An yi wannan waiwayen ne don ganin cewa aikin ya rataya kan abubuwan da aka waiwaya kuma waiwayen zai zama wata matashiya ga wanda zai ci karo da wannan aiki. An bayyana samuwar waxannan waqoqi na fiyano a qasar Hausa da asalin fiyano xin. Da fito da wuraren da aka yawaita amfani da fiyano ana rera waqoqi a qasar Hausa. Sai masu yin waqoqin fiyano da waqoqin da aka yi da fiyano.

### 2.1 Kundayen Bincike

Hausawa kan ce “Komai nisan gari da wani garin a gabansa”, a don haka an yi aikace- aikace da dama da suka shafi wannan aiki. Wato dai a ce akwai nazarce- nazarce kan waqoqin siyasa masu kima, sai dai kowane manazarci da inda ya dosa. Wasu sukan xauki jam’iyyun siyasa ne su yi nazarinsu. Wasu mawaqan sukan xauka da ayyukansu, su naqalce su. Da dai sauran vangarori da a kan iya dubawa don nazartar waqa.

Uchi (1973) da Mashi ( 1986) Birniwa (1987) da Abba (2000) da Yahaya (2000) da Lubabatu (2009) duk sun yi magana kan jam'iyyun siyasa a Nijeriya. Su kuma su Birniwa (1987) da Xiso ( 1997) da Binta ( 1997) da Muhammad (2003) da Musa (2007) sun duba adon harshe a waqoqin siyasa na Hausa. Birniwa (1987) da Ajiwa (1998) da Xanqwari ( 2000) da Xangulbi (2003) da Funtua (2003) da Auta (2008) da Xan'illela (2010) sun yi magana kan waqoqin siyasa dangane da Jumhuriya, wato wasu kevantattun lokutta da aka yi waqoqin.

Uchi (1973) da ya yi magana kan jam'iyyun siyasa, ya kawo jigogin jam'iyyun siyasa da irin ayyukan da suka yi a qasar Tiv. Jam'iyyun da ya yi maganar su, su ne UMBC da NPC. Ya kawo tarihin jam'iyyun siyasar da yadda suka gudana a qasar Tiv. Ya binciko rawar da jam'iyyar UMBC ta taka, wato irin farfagandar da ta yi.

Shi kuwa Mashi (1986) ya yi bayani kan tarihin kafuwar siyasa a qasar Hausa da kuma kafa jam'iyyun siyasar farko a Nijeriya irinsu NEPU da NPC, da NPN da PRP da GNPP. Ya tavo siyasa da ma'anoninta da manufofinta a lokacin Musulunci da lokacin zuwan Turawa.

Birniwa (1987) ya yi nazarin waqoqin jam'iyyun siyasar NEPU da NPC sai PRP da NPN a matsayin waqoqin farfaganda wanda ya nuna sun rayu a shekarar 1946 zuwa 1983. Ya nuna cewa a lokacin siyasar NEPU da NPC, sun bijiro da ra'ayin sauyi. Ya nuna manufar jam'iyyar NPC da yaqi da jahilci, lalaci da zalunci. Daga cikin muqarrabanta akwai su Malam Aminu Kano, Sa'adu Zungur, Tafawa Valewa da sauransu. Amma daga baya mutane kamar su Sa'adu

Zungur sun bar jam'iyyar da suka ga manufofin sun fara karkata zuwa ga Turawan Mulkin Mallaka. Ita kuwa jam'iyyar NEPU ta yi ta qoqarin yaxa manufofinta na neman sauyi. Shugabanta na farko shi ne Malam Raji Abdullahi, sauran 'yan jam'iyyar sun haxa da wasu daga cikin mutanen da suka baro jam'iyyar NPC kamar su Aminu Kano da Sa'adu Zungur. Sai ya kawo nagartaccen tarihin siyasar Nijeriya wadda ta fara tun daga sarautar gargajiya zuwa wadda aka samu sanadiyar zuwan Turawa. Ya tavo gudunmuwar mawaqan wajen yaqin neman zave.

Shi kuwa Abba (2000) ya kalli gudunmuwar da jam'iyyar NEPU ta bayar wajen havaka siyasar Nijeriya. Ya gudanar da binciken ta hanyar kawo tarihin kafa jam'iyyar NEPU a watan 08/08/1950, da rawar da jam'iyyar ta taka a siyasar Arewacin Nijeriya. Ya qara bayyana irin gumurzun da NEPU ta sha wajen neman 'yancin talakawan Arewacin Nijeriya. Abba (2000), ya ci gaba da bayyana taimakon da NEPU ta yi don ganin an tabbatar da zave a Arewacin Nijeriya. Sai kwatanta jam'iyyar NEPU da ya yi da sauran jam'iyyun siyasa musamman na Arewa. Da farko dai ya kwatanta NEPU da jam'iyyun siyasa uku da wanda suka kafa gwamnatocin siyasa a Arewa da Kudancin Nijeriya kamar jam'iyyun NPC, NCNC, AG da UMBC.

Da Yahaya (2000) da Lubabatu (2007) da suka duba jam'iyyun siyasa a Nijeriya, sai Yahaya (2000) ya xauko rubutattun waqoqin jam'iyyar PDP ya nazarce su, inda ya kawo tarihin kafuwar jam'iyyar ta PDP da irin gudunmuwar da waqoqin suke bayarwa. Sai ya nuna cewa jam'iyyar na da mawaqa na musamman masu yi mata waqoqi na musamman. Waxannan mawaqa su ne, su Haruna Aliyu Ningi da Shu'aibu  Zakari 'Yanmedi, Qaraye. Bai gushe ba, sai da ya kawo xan taqaitaccen tarihin mawaqan. Ita kuwa Lubabatu (2007) a nata binciken, waqoqin siyasa na

jam'iyyar ANPP ta xauko ta nazarce su. Ta yi wadataccen sharhi kan wasu waqoqin jam'iyyar ANPP. Ta yi sharhin sananniyar waqar nan mai suna *Nijeriya Riqo Sai Mai Gaskiya* ta Ibrahim Yahaya Hayin Banki, Kawo, Kaduna.

Ayyukan Uchi (1973) da Mashi (1986) da na Birniwa (1987) da na Yahaya (2000) har ma da na Lubabatu (2009) duk suna da alaqa da wannan aiki, domin sun yi magana kan jam'iyyun siyasa, inda wasu daga cikin su kamar Yahaya (2000) suka yi bayani kan waqoqin wasu jam'iyyu. Duk da dai waqoqin siyasa da aka nazarta a wannan aiki ba na jam'iyyu ba ne, hakan kuwa bai hana a nazarce su ba domin ai "Daga haka aka fara katuru ya ga mai qyasfi". Sannan kuma ayyukansu sun qara haske wajen sanin tarihin kafuwar siyasa a Nijeriya da kuma irin gudunmuwar da jam'iyyun siyasar suka bayar wajen havaka siyasar Nijeriya musamman ta Arewa. Da kuma yadda ake amfani da waqoqin wajen yaqin neman zave.

Waxanda suka kalli adon harshe a waqoqin siyasa sun haxa da Birniwa (1987) da Xiso (1997) da Binta (1997) da Muhammad (2003) da Musa (2003). Birniwa (1987) ya yi nazarin salo da harshe da tsarin waqoqin waxannan jam'iyyu da ya yi aiki a kansu, jam'iyyun su ne, NEPU da NPC sai PRP da NPN. Ya kawo tarihin marubuta waqoqin da ya yi aiki a kansu. Da ya tashi yin nazarin adon harshen, sai ya fara da waqoqin jam'iyyar NPC, inda ya xauko waqoqi da dama a jam'iyyar kamar waqar *Yabon Ahmadu Bello* ta Shekara Sa'ad, ya yi nazarin adon da ke tattare da waqar. A waqoqin jam'iyyar NEPU kuwa, ya ba da misali da waqar *Tauraron Zamani* ta Aqilu Aliyu. Haka ya yi wa NPN da PRP. Binciken ya nuna cewa, kusan a dukkan waqoqin akwai aron kalmomi daga harshen Larabci da su karin magana da sauran makamantansu. Xiso (1997) kuwa, zambo da yabo ya duba a rubutattun waqoqin siyasa na Hausa. Ya bayyana samuwar

siyasar jam'iyya da havakarta a Nijeriya. Sai samuwar waqoqin siyasa da bunqasarsu. Daga nan sai ya kawo zambo da yabo da dalilan da ke sa a yi su, tare da misalansu a cikin waqoqin baka da rubutattu na siyasa. Sai ya kallo zambo da yabo a waqoqin jam'iyyun siyasa, inda ya karkasa zamunnan siyasar har zuwa lokacin da ya gudanar da binciken.

Ita kuwa Binta (1997) a binciken nata, ta bayyana abin da ake kira harshen waqa. Ta kawo bambanci tsakanin abin da ake kira harshen waqa da harshen yau da kullum, har ta kawo ra'ayin masana irin su Leech (1969) na yadda yake kallon wannan bambanci. Ta nuna cewa harshen waqa ya shafi kaucewa daidaitacciyar qa'ida ta harshe, ta sake nuna cewa harshen waqa ya qunshi zavi na mawaqi na irin kalmomin da zai yi amfani da su wajen rera waqarsa. Ta qara da cewa harshen waqa dole ya zama harshe na qirqira. Sai kuma uwa uba adon harshe wanda ya fi shahara a matsayin harshen waqa.

Muhammad (2003) kamar Binta (1997) ya dubi salo a cikin aikinsa, inda ya kawo ababen da ke haddasa samuwar salo. Sai ra'ayin malamai dangane da ma'anar salo. Yayin da Binta (1997) da Muhammad (2003) suka yi nazarin salo a wasu waqoqi, shi kuwa Musa (2007) sai ya duba zambo da yabo a waqoqin Haruna Aliyu Ningi na siyasa. Da farko dai ya kalli Ningi a matsayin mawaqin siyasa, don haka ne ma ya kawo labarin haihuwarsa da tasowarsa. Ya sake kallonsa a fagen rubuta waqa da nau'o'in waqoqinsa. Sai ya fito da yabo da zambo a waqoqin na Ningi. Xiso (1997) da Binta (1997) duk sun yi magana kan salo a harshen waqa, inda Xiso ya yi bayani kan muhimmman abubuwan da yake ganin su ne ruhin rubutattun waqoqin siyasa, wato zambo

da yabo, wanda da irin harshen ne ake yaqin neman zave. Ita kuwa Binta sai ta dubi harshen waqa gaba xayansa, da irin lasisin da mawaqi yake da shi wajen tsara waqarsa.

Akwai dangantaka ta ququt tsakanin waxannan ayyuka da wannan, duk da sun yi magana kan salo a wasu waqoqin siyasa. Aikin Xiso (1997) ya taimaka sosai tunda ya yi bayani ne kan yabo da zambo, wanda da wuya a rasa irin wannan salalen a irin waqoqin aka yi nazari. Duk da dai wannan ba zai duba salo ba. Amma a iya cewa zambo da yabo suna taka rawar gani a waqoqin siyasa. Na Binta (1997) kuwa, dangantakarsa da wannan ta fito inda nata zai qara wa nawa haske wajen gane harshen waqa, watakila a samu ko harshen waqa yana canzawa dangane da lokaci. Binciken Muhammad (2003) ya taimaka wajen qara fahimtar Aliyu Ningi da wasu waqoqinsa, don wannan bincike ya yi nazarin wasu waqoqin siyasa na farfaganda na Haruna Aliyu Ningi.

An yi aikace-aikace kan waqoqin siyasa dangane da Jumhuriya, wato dangane da lokacin da aka aiwatar da su. An dubi siyasa ta fuskar sauyin da ake samu a lokutta mabambanta. Daga cikin waxanda suka bayar da irin wannan gudunmuwa akwai, Birniwa (1987) da Ajiwa (1998) da Xanqwari (2000) da Xangulbi (2003) da Funtua (2003) da Auta (2008) da kuma Xan'illela (2010).

Har wayau, Birniwa (1987) a aikin nasa, ya yi tsokaci kan waqoqin siyasa na Jumhuriya ta xaya da ta biyu, wato aikin kacokam yana magana ne kan waqoqin da aka yi a wanxannan zanguna mabambanta, inda ya kamanta tsakanin waqoqin jam'iyyun NEPU da NPC, sai NPN da PRP. Ya

nuna cewa jam'iyyun da suka rayu a mabambantan lokutta, gyauron juna. Sai Ajiwa (1998) da ya tofa albarkacin bakinsa kan samuwar siyasa a Nijeriya da gudunmuwar marubuta waqoqin, tare da muhimmancin rubutattun waqoqin a harkar siyasa. Ya yi magana kan Jumhuriya ta farko zuwa ta biyu da irin yunqurin da aka yi wajen kafa Jumhuriya ta uku, tare da kawo yanayin waqoqin. Sai waqoqin da aka yi don nuna fa'idar miqa mulki a hannun farar hula, irin waqoqin su Sambo Wali, da Bello Zurmi, da sauransu.

A aikin da Xanqwari (2000) ya gudanar, bai duba waqoqin ta fuskar Jumhuriya ba, sai ya duba waqoqin farko farko a qasar Hausa. Sannan ya leqa waqa a qarni na sha tara, tare da kawo samuwar waqoqin da dalilin da ya sa aka rinqa yin su. Sai ya karkato wajen waqoqin da aka yi a zamanin Turawan Mulkin Mallaka, wato ya fito da sauyin jigogin da aka samu a lokuttan, inda ya kawo misali da waqar *Zuwan Annasara Qasar Hausa* ta sarkin musulmi Attahirun Amadu. Ya bayyana waqoqin da aka samu bayan zuwan Turawa, wanda ya haifar da waqoqi na yanayin zamantakewa, har aka samu waqoqin siyasa, da sauran jigogi da suka shafi rayuwar al'umma.

Da Xangulbi (2003) da Funtua (2003) duk sun yi bincikensu ne a kan waqoqin siyasa a wasu Jumhuriya ta uku da ta huxu. Sai dai shi Xangulbi (2003) ya fi mayar da hankali kan waqoqin siyasa na Jumhuriya ta huxu, inda ya kawo rabe-raben waqoqin, tare da jigoginsu, irin su faxakarwa, yabo, da zambo. Sai kwatancen salon wasu waqoqin jam'iyyun siyasa da wasu, misali salon waqoqin PDP da na ANPP.

Funtua (2003) a nasa qoqarin, aiki ya yi kan waqoqin siyasa na Hausa a Jumhuriya ta uku, inda ya duba sigogin waqoqin da yanaye-yanayensu. Ya bayyana yadda siyasa ta gudana a Arewaci

da Kudancin Nijeriya. Ya tavo Gwamnatocin siyasa tun daga Jumhuriya ta xaya, har zuwa ta uku. Sai mawaqa da waqoqin na Jumhuriya ta uku. Ya duba yanayin mawaqan ta fuskar ilmi, shiga da kuma halayya. Ya rattabo wasu sigogi da jigogin waqoqin Jumhuriya ta uku.

Shi kuwa Auta (2008) da ya yi nazarinsa kan rubutattun waqoqin Hausa, sai ya kalli wasu daga cikin waqoqin qarni na ashirin a matsayin waqoqin faxakarwa. Ya nuna cewa an yi waqoqi da dama a sha'anoni na rayuwa daban-daban a qarni na ashirin (Q20). Wanda dalilai da yawa suka haifar da su kamar samuwar ilmin boko, da aikace-aikacen gwamnati ga siyasa da sauransu. Daga cikin jigogin waxannan waqoqi ne, ya zavi masu jigon faxakarwa, inda ya nuna cewa faxakarwa ta qunshi jawo hankalin mutane zuwa ga wani muhimmin abu wanda mutane suka sani, amma sai suke watsi da wannan abu. Ya sake bayyana cewa, a waqoqin faxakarwa ne ake yin kira ga jama'a da kuma ankarar da su zuwa ga aikata abin alheri da kuma guje wa marasa kyau. Kamar yadda ya ce irin wannan faxakarwar ita ke kawo ci gaban al'umma.

Binciken Auta (2008) na nuna cewa, akwai jigogi masu yawa a rubutattun waqoqi da za a iya kira na faxakarwa, kamar jigon faxakar da al'umma kan muhimmancin ilmi da gyaran hali, kishin kai da sauransu. Ya kawo ra'ayin Bargery (1933:288) da ya bayyana faxakarwa da cewa kalmar "Faxakarwa ta samu ne daga 'faxakad da', yayin da faxakarwa ke nufin abin da ke ta da tsumin mutum". Sai jigogin waqoqin da ya yi magana kamar su kishin ilmi, gyaran hali, kishin al'adu da sauransu. Auta ya tavo sigogin waqoqin na faxakarwa, sai kuma sharhin wasu waqoqin da ya yi kamar, waqar *Munin Zina* ta Ibrahim Halilu da waqar *Sutura Ita Ce Mutum* ta Rabi'u Ahmed.

Duk da cewa Auta (2008) bai yi magana kai tsaye kan waqoqin siyasa ba, amma aikinsa na da alaqa da nawa, domin faxakarwa wata siga ce ta yin farfaganda, domin ana neman a wayar da kan mutane kan wani abu.

Amma Xan'illela (2010) ya fi karkata kan rubutattun waqoqin siyasa a wasu Jihohin Arewa kamar Sokoto da Kebbi da kuma Zamfara. Xan'illela ya yi tsokaci kan Jihohin da bunqasarsu ta wajen mulki da siyasa, ya kawo yadda jam'iyyun siyasa suka sami kafuwa a Jihohin. Sai ya fuskanto jam'iyyun siyasa tun daga Jumhuriya ta xaya har zuwa ta huxu, tare da bayyana ire-iren rubutattun waqoqin siyasa a waxannan Jihohi da yanayin marubuta waqoqin. Ya rattabo wasu waqoqin jam'iyyu, irin su ANPP da PDP da DPP, tare da gabatar da sharhin wasu waqoqin, har da ma fito da manufofi da qudurorin jam'iyyun, kamar neman taimako ga Allah, yin kashedi ga jama'a da sauransu.

Duka waxannan ayyuka suna da dangantaka da juna, kuma suna da alaqa da wannan aiki, domin sun yi magana kan waqoqin siyasa da aka yi dangane da Jumhuriyoyi mabambanta, don kowane akwai inda ya fi ba da qarfi. Birniwa (1987) ya kalli waqoqin siyasa a Jumhuriya ta xaya da ta biyu. Ajiwa (1998) kuwa, sai ya yi nazarinsa kan rubutattun siyasa a wani taqaitaccen zango tare da kawo muhimmanci da gudunmuwar waqoqin a harkar siyasa. Shi kuwa Xanqwari (2000) ya fi mayar da hankali kan tarihin samuwar waqoqi a qasar Hausa, wanda ta kai shi har zuwa samuwar waqoqin siyasa a qasar Hausa. Yayin da Xangulbi (2003) ya duba waqoqin siyasa a

Jumhuriya ta huxu, sai Funtua (2003) ya duba waqoqin siyasa Jumhuriya ta uku. Xan'illela (2010) ya yi nazarin waqoqin siyasa a wasu Jihohi na musamman.

Hadiza (2000) da Yahaya (2000) da Husaini (2007) da Idris (2010) sun duba abin da ya shafi mawaqa da waqoqinsu. Sai dai Hadiza (2000) ta yi magana kan dangantakar da ke tsakanin waqa da yaqi, inda ta nuna cewa suna da alaqa ta wani vangare, domin ai faruwar wani abu ne na rayuwar al'umma shi mawaqan ke dubawa, har su rubuta waqa a kai. Sannan ta nuna cewa Yaqin Duniya Na Xaya da na Biyu, da sauran yaqe-yaqen da aka yi a nahiyar Afirka, da ma wanda aka yi a Nijeriya duk sun taimaka wajen samar da adabi a lokuttansu. Ta rattabo mawaqan Yaqin Duniya na Xaya irin su Dupert Brookes. Sai mawaqan Yaqin Duniya na Biyu irin su Henry Reed da Allen Lewis. Ta bayyana yadda kowanensu ya shirya waqarsa dangane da yadda ya tsinci kansa a fagen fama.

Shi kuma Yahaya (2000) ya yi aikinsa a kan waqoqin PDP da irin muhimmancin waqoqin wajen wayar da kan jama'a. Ya yi maganar wasu fitattun mawaqan PDP, irin su Ningi, har da nuna su a matsayin jiga-jigan mawaqan PDP. Shi ma Husaini (2007) ya yi cikakken nazari kan Haruna Aliyu Ningi da wasu waqoqinsa. Husaini ya tattaro ayyukan Ningi na fasaha, wato waqoqin da ya yi, da yin nagartaccen sharhinsu. Kusan duk waqoqin Ningi na siyasa sai da Husaini ya kawo su, tare da nazarinsu. Yayin da Idris (2010) ya yi nazarin waqoqin Emmanuel Wise Mai Molo. Nazarin nasa ya karkata kan waqoqin addini na Mai Molo, amma masu jivi da siyasa. Ya yi nazarin waqar *Rikicin Zangon Kataf*. Ya fito da dangantakar ta addini da siyasa.

Alaqar ayyukan nan da wannan aiki ta bayyana ta inda na Hadiza (2000) ya taimaki wannan domin duk irinsu xaya, wato duk waqoqi muke magana a kai, inda ta duba waqoqin yaqi, wannan kuwa zai duba waqoqin farfaganda, tunda farfagandar ma ai wani yaqi ne na ceto al'umma. Aikin Yahaya (2000) ya qara wa wannan haske wajen sanin waqoqin siyasa na jam'iyyar PDP, da kuma sanin gudunmuwar wasu mawaqan wajen havaka harkokin siyasa. Babban kusancin aikin Husaini (2007) da wannan, shi ne kasancewar Aliyu Haruna Ningi marubucin waqoqi ne, musamman na siyasa, wanda waxannan waqoqi ne suka sa ya yi fice, ballantana ga waqarsa ta *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* wadda tana xaya daga cikin waqoqin da aka nazarta. A don haka, aikin ya taimaki wannan domin ya tattara wasu waqoqi na siyasa na zamani masu yin farfaganda. Na Idris (2010) kuwa, ya qara haske don ya tavo siyasa.

Jumare (2007) da Mannura (2008) sun yi aiki a kan farfaganda, sai dai kowane da yadda ya kalle ta. Jumare (2007) ya yi aikinsa kan farfaganda amma a tallar 'yan siyasa na gidajen rediyo. Ya kawo qwarya-qwaryan tsokaci kan farfaganda, inda ya tavo ta, ta ko'ina. Ya bayyana ra'ayin masana dangane da ma'anar farfaganda, har ya kawo nasa ra'ayin ya ce " Farfaganda hanya ce ta jawo hankalin jama'a domin yin na'am da wani sabon abu, ko kuma qarin karvuwa ga wani abu da dama can aka sani ko kuma nuna qyama ga wani abu". Ita kuwa Mannura (2008) farfaganda ta duba a wasan kwaikwayo na rediyo. Ta fito da yadda ake amfani da wasan kwaikwayo wajen yaxa manufofi a wasu gidajen rediyo, wato ana amfani da wasannin ana yin farfaganda ga Gwamnati da sauran jama'a. Ta kawo wasu wasanni da ke da wannan jigo na farfaganda, kamar wasan *Gata Nan Gata Nanku*, wanda BBC world service Trust Nigeria suke shiryawa. Wasan kamar yadda ta nuna, ya qunshi abubuwa da suka shafi ayyukan gwamnati da zamantakewar jama'a. Sai wasan *Qauna* na gidan rediyon jihar Kaduna, da ake yi don wayar da kan al'umma

kan ayyukan gwamnati. Ta kawo ma'anar farfaganda da tushenta daga kundayen *Encyclopedia* da sauransu.

Kusan a iya cewa aikin Jumare (2007) da na Mannura (2008) tagwaye ne da wannan aiki, domin shi Jumare (2007) ya duba farfaganda da yadda take aukuwa a tallar 'yan siyasa, ita Mannura (2008) magana ta yi kan farfaganda a wasan kwaikwayo na rediyo. Wannan aiki kuwa, ya kalli waqoqin fiyano na Hausa na farfaganda, ba tallar shuwagabannnin ba. Amma duk da haka, aikinmu ya yi kama sosai, don dukkansu suna maganar farfaganda.

Muhammad (2006) da Adu'a (2007) sun yi nazarce-nazarce kan waqa, sai dai kowane allazi da nasa amanu. Da Imran (2008) da Hamza (2011) sun yi aiki kan Aminu Ala tare da nazarin wasu waqoqinsa. Muhammad (2006) ya dubi waqa a matsayin wani makami na canza xabi'un al'umma. Ya nuna ana amfani da waqa don a jawo hankulan mutane zuwa ga aikata ayyukan qwarai. Sannan kuma a yi amfani da ita a tsoratar da hani ga munanan ayyuka. Ya yi maganar xabi'un da ake amfani da waqa wajen canza su kamar auren dole, amfani da tufafin gargajiya, zaman banza da sauransu. Shi kuwa Adu'a (2007) fa'idoji da illolin waqoqin siyasa ya duba. Ya bayyana fa'idojin waqoqin siyasa cewa yadda waqoqin ke nuna muhimmancin siyasa da yadda ya kamata a yi mulkin dimokraxiyya. Sannan suna faxakar da jama'a kan irin mahukuntan da ya kamata su zava da sauransu. Illolin waqoqin siyasa, ya zayyana su cewa sukan kawo gaba tsakanin al'umma baki xaya, wato tsakanin shuwagabanni da mabiya, ga haddasa ta'addanci da sauransu. Dukkan ayyukansu, suna da alaqa ta kusa da wannan aiki, shi aikin Muhammad (2006) ya haskaka don ya yi maganar waqa da matsayinta na canza xabi'u, su ma waqoqin nan na farfaganda suna qoqari sauya tunanin mutane ne, har ma da canza masu xabi'u. Saboda haka,

suna da alaqa ta kusa don sun yi maganar waqa da yaqin da take yin a sauya al'amuran jama'a. Na Adu'a (2007) kuwa ya taimaka duk da dai wannan ba magana ya yi kan fa'idoji da illolin waqoqin, amma suna da dangantaka, don sun yi magana kan siyasa.

Imran (2008) ya yi nazarin jigo da salon waqoqin Aminu Ala. Ya kawo tarihin rayuwarsa, tun daga haihuwarsa, matsayin karatunsa na boko da addini. Ya bayyana cewa Ala ya yi firamare da sakandare. Ya kuma wuce gaba da sakandare, inda ya samu takardar difloma. Baya ga waqa, Ala ya rubuta littattafai, kuma yana daga cikin wasu qungiyoyi na marubuta na qasa. Ya yi 'yan tafiye-tafiye a cikin Nijeriya da wajenta. Ya kuma nuna cewa Ala ya fara tsara waqa tun yana xan Islamiyya, lokacin da suke rera waqoqin Maulidi. Daga nan ya fara tunanin ya rubuta waqa ta kansa. Haka kuma, yana tsara waqa a duk lokacin da ya kevanta, ko kuma ya shiga wani yanayi na damuwa ko akasin haka. Daga haka waqa ke zo masa. Ya kawo ire-iren jigon waqoqinsa kamar na wa'azi irinsu waqar *Sakarkari* na madahu *Angara*, sai na ilmi kamar *Tirgaxen Rayuwa* da sauransu.

Ya kawo yanayin waqoqinsa da ya bayyana suna da ruwa biyu. Wato waqoqi ne rubutattu, kuma suna kama da waqar baka. Haka ya duba yanayin waqoqinsa ta tsarin baitoci da amsa-amo. Ya kwatanta waqoqinsa da waqoqin mandiri. Ya kuma kwatanta su da waqoqin fina-finan Hausa. Ya yi bayanin matsayin waqoqinsa. Ya nuna yadda waqoqin suka xaukaka shi sosai. Kamar yadda ya ce "Haqiqa Aminu Ala ya samu xaukakar da samun mai irinta sai an tona a cikin mawaqa. Domin tauraruwarsa kullum daxa haskawa take". A kafafen yaxa labarai na rediyo da talabijin duk ana amfani da waqoqinsa. Ya nuna yadda jama'a ke son waqoqinsa.

Ya yi sharhin wasu daga cikin waqoqinsa da suke da alaqa da wannan aiki ta kusa ba ta nesa ba. Alal misali, ya yi tsokaci kan waqar *Baubawan Burmi* da *Bubukuwa* da *Xaurin Gwarmai*.

Waqar *Baubawan Burmi* cewa ya yi " Wannan waqa tana wayar da kan al'umma, tare da faxakar da su, a kan mulkin danniya da kama-karya da qasar nan ta faxa a cikinsa. A yanzu idon jama'a ya rufe wajen zaven shugabanni. Ba sa duba cancantar mutum, sai dai wanda zai ba su kuxi, shi za su zava". Wannan ne dalilin da ya sa Ala ya rubuta waqar. Ya bayyana jigon waqar da faxakarwa kan irin nau'in shugabanninsu da kuma waxanda ya kamata su zava. Sai salon waqar ya duba abuntawa. Da kuma zubi da tsarin waqar.

Ita kuwa waqar *Bubukuwa* ya ce "Aminu Ala ya rubuta wannan waqar ne saboda yadda aka yi watsi da tsarin mulki, tare da hukunci (Shari'a). Shari'a tana aiki a kan talaka da marasa galihu". Jigon waqar shi ne nuna qyamar mulkin zalunci, tare da nasiha ga al'umma, kamar yadda ya bayyana. Ya yi maganar amfani da aron kalmomi daga Ingilishi. Ya yi maganar salon dabbantarwa.

Waqar *Xaurin Gwarmai* cewa ya yi "Duk da Allah Ya yi wa Nijeriya albarkatun qasa masu yawa, da kuma yawan jama'ar qasa. Amma qasar ta gaza ci gaba, ta kuma rasa adalan shuwagabanni." Wannan ne dalilin da ya sa Ala ya rubuta waqar. Jigon waqar shi ne addu'a, don ya kai kukansa ga Allah. Ya yi maganar salon waqar akwai kamance. Sai aron kalmomi daga Ingilishi, da zubin waqar.

Hamza (2011) ya yi nazarin salon sarrafa harshe a wasu waqoqin Aminu Ala. Ya yi nazarin karin magana da salon magana da kirari a wasu daga cikin waqoqinsa. Ya fito da karin magana a cikin waqar *Wanzami* a baiti na 21 da 24. Haka a waqar *Bara A Kufai* a baiti na 8, da sauransu. Sai

salon magana da ya fito a waqar *Jami'a* baiti na 9, sai kirari a waqar *Bakan Dabo* a baiti na xaya da sauransu.

Babu tantama, wannan aiki na Imran (2008) yana da makusanciyar dangantaka da wannan aiki. Alaqar ta fito ya yadda aikinsa ya yi maganar wasu muhimman waqoqi guda uku da wannan aiki ya yi maganarsu. Ya kawo tarihin marubucin waqoqin, dalilin rubuta su, wanda wannan aiki ma ya yi haka. Ya yi qoqarin daddale waqoqin daidai gwargwado. Wanda wannan ma ya daddale inda ya fuskanta. Ya yi maganar yanayin waqoqin, a matsayin masu fuska biyu. Shi ma wannan bincike ya yi qoqarin maganar matsayin waqoqin, na baka ne, ko rubutattu. Inda aka ji ta bakin masu waqoqin don qarin haske. Sai salo da zubin waqoqin da ya zayyana, duk da dai cewa wannan bincike ba zai duba su ta wannan fuska ba, amma sun taimaka wajen fito da surorin waqoqin.

Aikin Hamza (2011) ma yana da dangantaka sosai da wannan, don ya yi maganar waqoqin Aminu Ala, wannan aikin ma, zai dubi wasu daga cikin waqoqin na Aminu Ala.

Binta (2011) ta yi magana kan tasirin kayan kixan zamani a kan kaxe-kaxen Hausawa na gargajiya. Ta kawo yadda zuwan baqin al'ummu a qasar Hausa ya haifar canji kan kayan kixan Hausawa. Ta nuna cewa kafin zuwan baqin al'ummu, Hausawa na da kixansu na gargajiya wanda suke yi na asali. Amma bayan zuwan Musulunci, Larabci ya yi jirwaye sosai ga adabin Hausa na gargajiya musammman a kan waqoqi da kixa. Ta nuna cewa bayan zuwan Musulunci

ne aka samu waqoqin tashe da sauransu. Haka kuma, ta nuna cewa bayan zuwan Turawa, kaxe-kaxen Hausawa na gargajiya ya canza domin Hausawa sun aamfani da harshen Turanci, ana kuma amfani da kayan kixan Turawa wajen rera waqoqin Hausa. Ta kawo yanayin kaxe-kaxen Larabawa wanda suke yi da wasu kayan kixa kamar *Al-ud* da *Rabab* da *Al-nafeer*.

Ta bayyana kixa a wajen Larabawa yana da muhimmancin gaske domin an fara shi tun lokacin Jahiliyya. Domin suna amfani da kixa don kariya ga al'umma da nishaxi. Ta fito da nau'o'in kixan Larabawa cewa ya kasu biyu, akwai na gargajiya da na zamani. Na gargajiya ya qunshi *Al-jawza* da *Al-shabbabe* da sauransu. Kixan zamani ya qunshi kixan *Andalusian* da kixan *Berber* da kixan *Chaabi (pop)* da kixan *Sayidi*. Sai nason kixan Larabawa a kan na Hausawa wanda ya samu sanadiyar cuxanya ta hanyar kasuwanci da yaxa addinin Musulunci. Ta kawo misali da kixan Sudan da ake yi ana furta kalmomin Hausa. Ta yi maganar kixan Indiyawa wanda ya samo asali daga wasu abubuwa na bautarsu na addinin maguzanci. Ta kawo kixan Indiyawa kashi huxu wanda ya qunshi kixan Indiyawa kamar *Hindustani* da kixan al'umma kamar *Bauls* da kixan zamani kamar *Indi-Pop music*. Da kuma nason kixansu a kan na Hausawa. Ta yi maganar kixan Turawa, tare da kawo tarihinsa. Sai rabe-rabensa wanda ya haxa da *Instrumental Music* da *Chamber Music* da *Church Music*. Sai nason kixansu a wajen Hausawa. Ta kawo nason kayan kixan zamani a kan Hausawa wanda ta kawo kixan fiyano da asalinsa da kuma yadda ya shigo wa Hausawa. Ta kawo kixan jita da kixan disko. Aikin Binta (2011) yana da dangantaka da wannan aiki domin ta yi maganar kixan fiyano da yadda ya shigo a wajen Hausawa, wanda wannan aiki ma ya yi haka.

Dukkan kundayen da aka yi maganar su, suna da alaqa da wannan aiki, sun taimaki wannan sosai da sosai wajen sanin tudun da aka dafa. Don Hausawa kan ce " Ba a hawa sama sai da tsani."

**2.2 Muqalu**

Domin inganta da kuma xaukaka darajar ilmi, ya sa manazarta suke ta rubuce-rubuce da bincike-bincike a kan fannonin ilmi daban daban. Wasu sukan gudanar da rubutun ne a muqaloli da mujallu na Jami'o'i da kamfanoni iri-iri domin amfanin al'umma. Akwai nazarce-nazarce da aka yi masu kima a vangaren siyasa da waqa a muqalu na Jami'o'i daban daban a faxin Nijeriya. Daga cikinsu akwai:

Muhammad (1978 da 1979 da 1981) duk ya duba waqar baka da rubutatta, inda ya yi zuzzurfan nazari wajen bambance su.

Birniwa (2004 da 2005) da Umma (2011) duba adon harshe suka yi a rubutattun waqoqin siyasa, musamman a Jumhuriya ta xaya da ta uku. Su kuwa su Mukhtar (2006) da Birniwa (2010) duba matsayi da muhimmancin waqoqin siyasa suka yi wajen havaka mulkin dimokraxiyya.

Muhammad (1978 da 1979 da 1981) ya duba abin da ya shafi waqoqin baka da rubutattu na Hausa. Sai dai kowace takarda da inda ta fi bayar da qarfi. Muhammad (1978) ya fito da wasu muhimman abubuwa a kan waqa. Ya gano cewa bayan amsa-amon harafi da ake samu a rubutattun waqoqin Hausa, akwai kuma amsa-amon kari da ake samu a nau'o'in waqoqin duka biyu, savanin amsa-amon harafi wanda babu shi a waqar baka. Amma ya gano cewa ana samun amsa-amon kari a waqoqin baka na Hausa. Ya kafa hujjjoji daga baitoci da xiyan waqoqi.

Muhammad (1979) kuma ya gano dangantakar da ke tsakanin waqoqin baka da rubutattu. Ya fito da inda suka yi kama, da inda suka sha bambanta da kuma nason xaya cikin xaya. Muhammad (1981) ya qara rarrabewa tsakanin waqar baka da rubutatta. Sai ya nazarci waqoqin cikin littafin *Magana Jari Ce*, inda ya nuna cewa ga su dai a rubuce suke, amma ba su da siffofi irin na rubutattar waqa. Ya kawo misalai da dama wanda ya kare kansa da su.

Birniwa (2004 da 2005) da Umma (2011) sun kalli adon harshe a rubutattun waqoqin siyasa a wasu Jumhuriyoyi. Birniwa (2004) ya bayyana yadda siffantawa ta fito a waqoqin siyasa na Jumhuriya ta xaya NEPU da NPC, da waqoqin siyasa na Jumhuriya ta biyu masu hamayya da juna NPN da PRP. Ya nuna cewa waqokin siyasa cike suke da kwalliyar harshe, domin ana amfani da kwalliya don a yabi jam'iyya, a kuma kushe abokanen hamayya. Ya kawo misalan baitoci masu nuna siffantawa a waqoqin jam'iyyun. Aikin nasa zai taimaka ta fuskar salo, duk da dai ba za a yi nazarin salo a wannan aiki ba. Amma da wuya a rasa nono a ruga wato, da wuya a raba waqoqin farfaganda da irin wannan salo, don da irinsu ne ake amfani wajen faxakar da jama'a da jawo hankalinsu.

Har wayau, Birniwa (2005) ya bayyana yadda ake samun karin magana a waqoqin siyasa, binciken ya nuna cewa wani lokaci mawaqan na amfani da karin maganar ne ba yadda aka saba faxa a Hausa ba. Ya kawo misalin wata waqa ta NPC mai suna *Waqar Yabon Sardauna* ta Muhammadu Bello. Kafin nan, sai da ya kawo ma'ana da muhimmancin karin magana. Ya fito da karin magana a cikin waqoqin siyasa daban daban. Ya sake nuna cewa waqoqin siyasa cike suke da karin magana, amma ba kasafai mutane ke ganewa ba. Wannan takarda ta Birniwa

(2005) ta taimaki wannan aiki matuqa domin an yi nazarin waqoqin farfaganda. Haka kuma, aikinsa ya agaza sosai ta yadda da an ci karo da karin magana farat xaya za a gane ta. Duk da dai ba za a yi nazarin karin magana tsantsa ba.

Ita kuwa Umma (2011) adon harshe ta kalla a rubutattun waqoqin siyasa na Jumhuriya ta uku. Ta nuna cewa an yi rubuce-rubucen waqoqi da dama, masu manufofi kala-kala a qarni na ashirin, wanda qarnin ya haifar da bijirowar abubuwa da ya sa marubuta suka rinqa rubutu a kai. Ta nuna cewa an yi waqoqin neman 'yancin kan Arewa, wato irin waqoqin su Sa'adu Zungur da Mudi Sipikin. Ta yi bayanin siyasar Jumhuriya ta farko, wadda ta haifar da samuwar jam'iyyun siyasa irin su NEPU da NPC da AG. Sai jam'iyyun siyasa na Jumhuriya ta biyu kamar su NPC da PRP. A wannan lokaci ma, ta nuna an samu waqoqin siyasa da dama. Ta rattabo mawaqa irin su Auwalu Isa Bunguxu da ya yi waqar *Rundunar Nasara PRP Mai Fitar Da Haqqin Talakawa*. A Jumhuriya ta uku ta zayyana jam'iyyun siyasa da aka kafa kamar su NPP, PDP da sauransu.

Da ta duba adon harshe, bayyana sa ta yi da cewa "Wata dabara ce ta qara wa magana armashi domin kawar da qosawar masu sauraro ko karatu". Ta fito da nau'o'in adon harshe irin su siffantawa, kamantawa da jinsintarwa tare da misalansu a wasu waqoqin Jumhuriya ta uku. Don haka, wannan aiki na Umma (2011) ya taimaka qwarai.

Da Mukhtar (2006) da Birniwa (2010) sun yi magana kan matsayi da muhimmancin waqoqin siyasa da irin gudunmuwar da suke bayar wa wajen havaka mulkin dimokraxiyya a qasa.

Mukhtar (2006) nuna yadda ake amfani da rubutattun waqoqin Hausa don taskace siyasa da al'amurranta a Nijeriya. Jawabin nasa ya fara ne tun daga siyasar Musulunci, wato waqoqin da aka samu a qarni na sha tara (Q19) irin su waqar *Tsarin Mulkin Musulunci*. Sai waqoqin da aka samu lokacin siyasar zuwan Turawa, su ne wasu daga cikin waqoqin qarni na ashirin (Q20). Aikin nasa, kamar yadda aka nuna , ya kalli siyasar Nijeriya jiya da yau. Inda wannan aiki ya kalli siyasar Nijeriya ta yau kawai, don haka, aikin nasa ya taimaki wannan wajen ganin tsanin da siyasar bara ta hau, don gane inda ta bana ta dosa.

Birniwa (2010) kamar yadda ya bayyana, babbar manufar jam'iyyar NPC ita ce "Kau da jahilci da lalaci da zalunci", a qoqarin tabbatar da haka, an yi wa jam'iyyar waqoqi da dama don yabo ga shugabanta Sardauna, da kuma kushen abokiyar adawa, wato jam'iyyar NEPU. Wannan fitaccen salo ne in ji Birniwa (2010). Jam'iyyar NEPU kuwa, babbar manufarta ita ce " Qwato wa talakawa haqqinsu daga hannun Turawa 'yan Mulkin Mallaka da sarakuna da sauran waxanda 'yan jam'iyyar suke ganin suna zaluntar su". An rubuta waqoqi da dama a inuwar wannan jam'iyya domin yaqin neman zave. Sai dai wani hanzari da gudu ba, su 'yan NEPU ba su cika yabo da salsala ba ga shuwagabanninsu, don suna ganin bai kamata salsala ta zama wata hanya ta fito da shugaba ba. Ya ci gaba da nuna cewa a Jumhuriya ta biyu, an samu jam'iyyun siyasa kamar su PRP da NPN da GNPP da UPN. A wannan zamanin siyasar ma kamar yadda ya nuna an samu waqoqi da yawa da aka rubuta domin yaqin neman zave. Wannan takarda ta Birniwa (2010) ta tallafa wa wannan, domin an yi amfani da ita wajen gano matsayin waqoqin siyasa da muhimmancinsu.

Amin (1992 da 1993 da 2001 da 2004) da Xandatti (2008) duk sun yi magana kan siyasa ne musamman a kan gwarzonsu malam Sa'adu Zungur. Sun duba Sa'adu da ayyukansa a fuskoki daban daban, misali Amin (1992) ya nuna rashin amincewarsa kan ra'ayin wasu malamai irinsu Birniwa (1987) da Hiskett da HS Ibrahim na yadda suke kallon Sa'adu Zungur. Kamar Birniwa (1987) yana kallonsa a matsayin mai ra'ayin riqau, shi kuwa Hiskett ke masa kallon wani shaihun malami. Irin waxannan batutuwa ne Amin (1992) ya kalla ya bijire masu, ya kawo nasa ra'ayin da hujjoji daga waqar *Arewa Jumhuriya Ko Mulukiya*.

Amma a wata muqalar, Amin (1993) ya kalli Zungur ne matsayin mai ra'ayin sauyi ba mai ra'ayin riqau ba, kamar yadda wasu manazarta suke xaukarsa. Kamar su Birniwa da Hiskett. Marubucin ya ci gaba da kawo hujjoji daga waqoqin Zungur da suke nuna ra'ayinsa na sauyi kamar yadda Amin (1993) ya hango abin. Idan dai har muka xauki Sa'adu a matsayin mai ra'ayin sauyi, to sauyin nan da yake kira da yi ko a samu ba ji ba gani, ba komai ba ne illa farfaganda, inda yake neman cusa wa jama'a ra'ayi da faxakar da su. A don haka, wannan muqala ta taimaka wajen gano hanyoyin da ake bi a yi farfaganda don cimma manufa.

A nan ma dai, Amin (2001 da 2004) ya kalli Zungur ne a matsayin mai kishin qasa inda ya kawo hujjojinsa daga mashahuran waqoqinsa guda biyu. Dukkan muqalolin nan da Amin ya rubuta, bisa dukkan alamu xoriyar tarke ne daga aikin da su Birniwa (1987) da Hiskett suka yi kan Sa'adu Zungur.

Shi kuwa Xandatti (2008) ya yi aikinsa kan Sa'adu Zungur, inda ya kawo tarihinsa da kuma aikace-aikacen da ya yi a lokacinsa. Da farko ya fara da gabatar da tarihin rubutacciyar waqa a qasar Hausa. Yadda su Shehu suka rubuta waqoqi na wa'azi da ilmantarwa a cikin harshen Larabci, daga ba ya su Nana da Isa 'yayan Shehu suka riqa fassara su zuwa Hausa da Fillanci. Ya nuna cewa an samu sauyin marubuta waqoqin Hausa, wanda a wancan lokacin malaman addini suka fi rubuta waqoqin, amma a qarni na ashirin an samu marubuta wanxanda ba malaman addini ba, masu ilmin boko, da ma'aikatan gwamnati kamar su Na'ibi Sulaiman Wali, Mu'azu Haxeja da Sa'adu Zungur da sauransu. Ya bayyana tarihin Sa'adu tun daga iyayensa. Ya nuna mahaifin Sa'adu da shaihun malami kuma ya yi karatu a wurin mahaifinsa. Da dai cikakken tarihinsa sosai da sosai.

Bugu da qari, Amin (2000 da 2006) duk ya yi magana ne kan rubutattun waqoqi na Hausa, inda ya duba jigo. Amin (2000) ya bayyana cewa, bayan waqoqin wa'azu da aka yi a qarni na 19, ba a sake jin motsin wasu masu kama da su ba, sai a qarshen qarni na 20, inda aka samu waqoqi masu jigon jihadi. Kenan Amin (2000) yana na tare da Malumfashi (1984) da ya mayar da martani, ya nuna cewa ai waqoqi irin su Tabarqoqo masu jigon addini ne. Amin( 2006) ya yi tsokaci a kan waqoqin 'yan tajdidi, inda ya karkasa jigogin waqoqin kashi biyu, wanda ya haxa da jigon siyasa. Ya ci gaba da kafa hujjoji masu gamsarwa daga cikin waqoqin. Marubucin ya ruwaito mashahuran marubuta waqoqin tajdidi irinsu Aliyu Rabi'u Kurna, Kano, Abdulmumini Abubakar Bauchi da sauransu. Wannan muqala kamar saura, ita ma ta taimaka domin su ma 'yan

tajdidin ai farfaganda ta addini ce suke yi, tunda kira suke da a bi kwansutushan din Islama wato tsarin mulkin Musulunci.

Da Sa'id (1995) Adedimeji (2007) da Ibrahim (2009) sun yi bincike kan harkokin siyasa, inda da Adedimeji (2007) da Ibrahim (2009) suka fi mayar da hankali a kan harshen siyasa. Shi Sa'id (1995) ya fito da ra'ayoyin marubuta waqoqin Hausa a kan zuwan Turawa Nijeriya. Ya bayyana al'amarin ta fuska biyu, da farko ya nuna akwai masu kira da a guji baquncin na Nasara, da kuma masu na'am da samun canjin da ya samu sanadiyar zuwansu. Ya nuna cewa marubutan da suke nuni da a guji Turawa, yawancinsu marubuta ne da ba su da ilmin boko, suna amfani da abin da Musulunci ya zo da shi. Ya kawo misalan waqoqin irinsu waqar *Zuwan Annanasara Qasar Hausa* ta Sarkin Musulmi Attahirun Amadu sai waqar Mai Katuru wadda ya yi, yana kira da a guji amfani da duk wani abu da Turawa suka kawo kamar tawul, agogo da tocila. Sai waqoqin da aka yi domin nuna jin daxi da amincewa abin da Turawa suka zo da shi. Ya bayar da misali da waqar Malam Sa'id ta *Yabon Sarkin Ingila George V (1910-1935)* da waqar *Basikur* ta Aliyu Namangi, inda suka nuna jin daxinsu da maraba da zuwan Nasara.

Shi kuwa Adedimeji (2007) ya nazarci irin harshen da 'yan siyasa ke amfani da shi wajen yaxa manufofinsu don samun nasara ga siyasar da suka sa a gaba. Adedimeji (2007) ya gano cewa harshen 'yan siyasa cike yake da qarya da qarairayi, yaudara da kinaya, kambamawa da sauransu. Domin kafa hujja, ya kawo misalai daga maganganun 'yan siyasar Nijeriya. Lallai kuwa, aikin Adedimeji (2007) kusan wani ginshiqi ne aikina. Don irin maganganunsu na yaudara da qarya da suke yi, da rashin cika alqawari, suna jawo hankalin mutane da su zave su,

bayan an zave su, kuma su riqa yi wa mutane mulkin kama-karya. Irin abin da mawaqan da suka yinwaqoqin da aka yi nazari suka hango kenan, shi ne suke tunasar da jama'a da a fa lura da abin da ke faruwa. Saboda haka, takarda ta agaza sosai da sosai.

A takardar Ibrahim (2009) fito da irin zantukan da Sahabban Ma'aiki SAW suka yi lokacin Khalifancinsu. Ya kawo taqaitaccen bayani kansu tun daga Khalifancin Abubakar (RA) har zuwa Aliyu (RA) da irin yadda suka gudanar da mulki. A yayin gudanar da harkokin shugabancinsu, sun yi wasu maganganu da suka shafi sha'anin mulki wanda ya jivanci yin adalci da riqo da gaskiya da amana da sauransu. Sannan kuma, sukan nuna idan sun bi tafarkin Allah, to su ma a bi su, idan sun kauce, su ma a kauce masu. Ya kuma nuna yadda suke cika alqawurra da tsare haqqin mutanen lokacin, wato suna yin faxa da cikawa. Daga qarshe ya nuna yadda shuwagabanninmu Musulmai ba su koyi da riqo da abin da magabata suka yi. An yi amfani da muqalar wajen qara tantancewa.

Ibrahim (1982) da Wurma (1999) da Sarki (1999) da Junaidu (2001) da Bayero (2004) da Babanzara (2010) duk sun yi tsokaci kan rubutacciyar waqa, sai dai kowane da yadda ya dube ta. Ibrahim (1982) ya bayyana cewa an samu rubutattun waqoqin Hausa kafin bayyanar su Shehu Xanfodio, savanin ra'ayi da ake ganin cewa babu wasu waqoqi aka yi kafin bayyanar su Xanfodio, duk da dai ana tararrabin samuwar wasu waqoqin. Ya rattabo malamai da suka yi zamani kafin qarni na 19 da irin waqoqin da suka yi, har da taqaitaccen tarihin marubutan.

Sai Wurma (1999) ya kawo ginshiqan abubuwa da ake dubawa ko ake amfani wajen nazarin waqa rubutatta. Ya fito da abu guda biyar da ake dubawa wajen yin nazarin su ne: tarihin mawallafi, dalilin yin waqa, jigo da warwararsa, zubi da tsari sai salon sarrafa harshe. Abubuwan da ke vata ta kamar yadda ya nuna su ne: yawaita aron kalmomi, rashin amsa-amo da daidaituwarsa da sauransu.

Kamar yadda Wurma (1999) ya duba hanyoyin nazarin waqa rubutatta, shi kuwa Sarki (1999) ya yi qoqarin bayyana muhimmancin waqa rubutatta da yadda ake amfani da ita wajen wayar da kan jama'a don a canza xabi'unsu. Ya ci gaba da nuna cewa waqoqin na taka muhimmiyar rawa ga kowace al'umma ba ma Hausa kaxai ba wajen ilmantarwa da faxakarwa. Ya kawo tasirin rubutattar waqa kan al'ummar Hausawa. Ya sake nuna hukumomi da al'ummar duniya suna amfani da waqa wajen yaxa manufofinsu. Ya kawo misali daga waqoqinsu Shehu Xanfodio. Sai waqoqin da a ka yi lokacin samun mulkin kan Nijeriya ta Arewa. Sai kuma, ya nuna kafin jihadin Shehu har zuwa bayansa, an yi waqoqi da suka yi qoqarin canza xabi'un mutane. Haka kuma, sun taimaka wajen wayar da kan al'umma game da ayyukan gwamnati da manufofinta misali qidayar jama'a, juya tuqi zuwa hannun dama da makamantansu.

Yayin da Junaidu (2001) a wata takarda tasa, ya bayyana yadda malaman jihadi irin Xanfodio da mabiyansa suke amfani da harshen Larabci wajen rubuta waqa don wa'azi da faxakarwa. Sai ya nuna bayan Larabci, suna amfani da Fulfilde da kuma Hausa domin mabiyan Shehu a lokacin Hausawa ne da Fulani, don haka, aka fi amfani da harsunan wajen yaxa addinin Musulunci. Ya qara nuna cewa, sun fi amfani da harshen Larabci a matsayin hanyar sadarwa tsakaninsu da

maqwabtansu. Harshen Fulfilde da Hausa kuwa, suna amfani da su wajen wa'azi a qasashen Kebbi da Zamfara. Haka dai suka rinqa amfani da Harsunan Hausa da Fulfulde da Larabci wajen yaxa addinin Musulunci.

Bayan nan, sai Bayero (2004), qoqarin da marubucin ya yi shi ne, nuna cewa akwai waqoqin da za a iya cewa waqoqin nasiha ne duk da cewa suna iya zamowa cikin na wa'azi ta fuskar jigo. Ya kira su da waqoqin nasiha ne saboda irin salonsu. Ya ci gaba da zayyano salalen da yake ganin su ne za su iya sa wa a kira wasu waqoqin wa'azi da waqoqin nasiha, inda ya nuna cewa waqoqin wa'azi na gabatar da saqonsu cikin harshe mai tsoratarwa, su kuwa na nasiha, lallashi sukan yi, maimakon su razanar.

Daxin daxawa, Babanzara (2010) a tasa muqalar, da farko ya yi bayanin kowane ne mawaqi, ya bayar da ma'anar waqa da harshen waqa. Sannan ya ci gaba da kawo tarihin rayuwar waxannan marubuta waqoqi, inda ya fuskance su ta fuska biyu. Da mawaqan siyasa a Jumhuriya ta xaya irinsu Aqilu Aliyu da Gambo Hawaja, daga nan sai Jumhuriya ta biyu kamarsu Auwalu Isa Bunguxu, sai kuma Jumhuriya ta huxu mai mawaqa irinsu Ibrahim Aminu Xandago da Garba Gashuwa.

Ayyukansu sun taimaka, inda na Ibrahim (1982) ya qara haske wajen sanin salsala da asalin waqa. Shi na Wurma (1999) kuwa ya agaza ta wajen qara fito da waqa. Sai na Sarki (1999) a iya cewa, manazarcin yana qoqarin nazarin rubutattun waqoqi a matsayin wata hanya ta farfaganda,

domin ya nuna cewa ana amfani da waqoqin domin wayar da kan jama'a kan wani al'amari. Wato ana cusa wa jama'a ra'ayi savanin nasu. Na Junaidu (2001) ya taimaka wajen bayyana sanin asalin waqa musamman ta sanin harshen da aka fara rubuta ta da kuma yadda aka yi amfani da ita wajen wa'azi, don irin waqoqin su ma suna farfaganda ne amma ta Musulunci. Bayero (2010) da Baban Zara (2010) su ma nasu ba daga baya ba, don sun qara haske sosai.

Dambo (1999) da Aminu (1999) duk sun duba farfaganda ne a wasu vangarori na ilmi. Shi Dambo (1999) ya duba farfaganda a rubutattun waqoqin Hausa. Yayin da Aminu (1999) ya kalli farfaganda a matsayin jigo a *Wasan Marafa*. Dambo (1999) ya yi nazarin waqoqin qarni na 19, da wasu na qarni na 20, ya kalle su a matsayin waqoqin farfaganda. Manazarcin ya kafa hujjojin da ya sa ya kira waqoqin da na farfaganda. A waqoqin qarni na 19, ya nuna cewa Shehu da mabiyansa sun yi rubuce-rubucen waqoqi don jawo hankalin al'umma zuwa tafarkin Musulunci da barin wasu ayyuka da suka sava wa addini. Sun yi amfani da waqa a matsayin wata hanya ta isar da saqo. Saboda haka, ya nuna waqoqin a matsayin na farfaganda, domin ai suna qoqarin lallashi ne. A waqoqin qarni 20, ya nuna wasu da cewa na farfaganda ne, domin Hausawa sun samu sauyin rayuwa da samun canje-canjen abubuwa da dama, a irin haka ne, wasu suka rinqa rubuta waqoqi, suna nuna rashin amincewarsu kan wannan sabon sauyi. Ta haka ne, suka rinqa yin farfaganda, suna faxakar da mutane kan abin da suke ganin ba daidai ba ne.

Shi kuwa Aminu (1999) ya bayyana farfaganda a matsayin wani ginshiqin jigo a *Wasan Marafa*, savanin Skinner (1980) da ya ce jigogin wasan kwaikwayon Hausa sun ta'allaqa ne kan zaman iyali, wanda Malumfashi (1985) ya mayar da martani da nuna cewa ba haka abin yake ba. Akwai

wasan kwaikwayo da suke xauke da wasu jigogi daban, kamar wasan *Uwar Gulma* mai jigon "fafitikar kuxancewa ido rufe". A don haka ne, Aminu (1999) ya yi zuzzurfan nazari kan wannan wasa, ya gano cewa ai ba komai ba ne, illa farfaganda ta Turawa da suke son su nuna muhimmancin zuwa asibiti maimakon amfani da maganin gargajiya. Ya yi tsakure daga cikin Littafin don kafa hujjoji ingantattu. A ganina, farfaganda ce ta Turawa don a yi watsi da hanyar gargajiya a koma ta su kamar yadda Aminu (1999) ya bayyana.

Saboda haka, aikin nan ya qara ginuwa da ayyukan Dambo (1999) da Aminu (1999) domin ya amfana da hujjoji ba bayanai kan farfaganda, har da ma tudun da aka hau don leqo dalili da manufofin farfaganda da yadda kuma za a fuskance ta a wannan xan qwarya-qwaryan aiki.

Amin (2008 da 2008) da Xan'asabe da Wushishi (2008) da Bello ( 2009 da 2011) sun yi rubutu kan waqoqin zamani da ake yi da fiyano.

Amin (2008 da 2008) ya yi rubutu kan waqoqin nan na zamani. Amin (2008) ya yi magana kan waqoqin zamani da ake yi, masu nuna bore da tawaye da bijire wa mulkin qasa, wato waqoqin suna yin farfaganda ne matuqar ba za a yi mulkin gaskiya ba. Ya kawo misalai da wasu fitattun waqoqi guda biyu, da waqar *Ba Za Mu Bi Kwansitushan Ba* da kuma waqar *Baubawan Burmi* ta Aminu Ladan Abubakar. Tsintar dame a kala! Wannan aiki na Aminu (2008) ya taimaka qwarai, don kusan a iya cewa kamar wa da qane ne shi da nawa aikin. Ga shi kuma irin waqoqin da aka yi nazari ne, don haka, ba qaramar fa'ida aka samu ba a aikin Amin (2008). Ya haskaka wajen

qara fahimtar waqoqin, a matsayin waqoqin farfaganda. Har wayau, Amin (2008) ya yi wani bincike, inda ya yi tsokaci kan tasirin zamananci a cikin al'ummar Hausawa, musamman kan rubutaccen adabi. Ya nuna yadda zamananci ya yi kaka-gida cikin wannan nau'in adabi na Hausawa, ya duba nason zamananci a qagaggun labarai da wasan kwaikwayo da kuma waqa.

Xan'asabe da Wushishi (2008) sun yi magana kan muhimmancin mawaqa ga ci gaban siyasar Nijeriya, inda suka yi nazarin waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* ta Haruna Aliyu Ningi. Sun nuna muhimmancin waqa da mawaqa ga kowace al'umma wajen samar da siyasa mai kyau a Nijeriya. Domin waqoqin na faxakar da mutane, da ma ilmantar da su kowane al'amari na siyasa. Sun yi nazarin waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* a kan tasirin da waqar ta yi wajen dakushe burin shugaba Obasanjo da mataimakansa na nufin zarcewa a kashi na uku a kan mulki. Sun bayyana cewa, Haruna Aliyu Ningi ya rera waqar a shekarar 2006, kuma asalinsa xan jam'iyyar PDP ne, daga baya ya yi ridda. A matsayinsa na xan jam'iyya da ba ya goyon bayan ta zarce, sai ya rubuta waqar yana tunzura 'yan Nijeriya, yana qoqarin ya sauya tunaninsu, kada su amince da tsarin ta zarce.

Haka kuma, sun bayyana tasirin da waqar ta samu da cewa ta taimaka wajen saka qiyayya ga tsarin ta zarce a faxin Nijeriya gaba xaya, da kuma duk wani shugaba da ke da kusanci da Obasanjo a wancan lokaci. Haka ya nuna a amshin waqar da ya ce "Ku faxa wa Obasanjo, mu kam ba mu yarda ta zarce ba." Sun ci gaba da tsettsefe waqar dalla-dalla, suna nuna yadda Ningi ya yi qoqarin cusa wa 'yan Nijeriya qiyayyar ta zarce.

Bello (2009 da 2011) ya yi maganar wasu waqoqin farfaganda na fiyano, masu zayyana manufofin siyasa sosai. Bello (2009) ya yi nazarin waqar *Baubawan Burmi* ta Aminu Ala. Da farko ya kawo taqaitaccen tarihin marubucin waqar inda ya nuna cewa "An haifi Aminuddeen Ladan Abubakar ALA a shekarar 1973 a unguwar Yakasai da ke cikin birnin Kano…" Sannan ya bayyana asalin waqar ya cewa, mawaqin ya bayyana masa, abin da ya ja hankalinsa ya rubuta waqar, shi ne don ya sanar da jama'ar Nijeriya irin kura-kuren da ake tafkawa wajen zaven shuwagabanni, da yadda shugabannin ke aiwatar da mulki a hagunce, ba a bisa tsarin da ya dace ba. Ya rubuta waqar a shekarar 2007, a tudun Murtala, kwanar 'yan Ghana. Ya bayyana babban jigon waqar, shi ne faxakarwa kan yadda shuwagabanni ke yin mulkin kama-karya. Sannan waqar na xauke da qananan jigogi kamar nasiha da gargaxi ga mahukunta. Sai ya ci gaba da warwarar jigo, yana mai tantance waqar dalla-dalla. Ya yi maganar zubi da tsarin waqar, kamar mabuxi da marufin waqar, ya nuna an buxe waqar da addua', an kuma rufe ta da godiya. Sai yawan baitoci da qafiyar waqa. Bai tsaya nan ba, sai da ya yi maganar muhimmancin waqar, wato darussan da ta ke koyarwa cewa, tana nuna kowane shugaba ya yi adalci ga mulkinsa, ya guji zalunci. Su kuma matasa, su kasance masu gaskiya, a daina amfani da su, ana bangar siyasa. A daina sayar da quri'u da sauran abin da bai dace ba.

Bello (2011) kuma, ya yi magana kan gudunmuwar adabin Hausa a fagen ci gaban siyasa da tabbatar da dimokraxiyya a Nijeriya, inda ya yi nazarin waqar *Dimokraxiyya* ta Aminu Ala. Ya yi tsokaci kan waqar. Inda ya nuna yadda waqar ke jawo hankalin jama'a da nuna cewa sai kowa ya gyara halinsa tun daga mahukuntan har talakawan, sannan za a ci moriyar mulkin dimokraxiyya a Nijeriya. Jama'a su zavi wanda ya dace, su kuma waxanda aka zava, su yi wa qasa aikin da ya kamata. A nan ma, sai da ya kawo taqaitaccen tarihin mawaqin, sannan ya yi

maganar siyasa da dimokraxiyya. Ya kawo jigon waqar cewa don a ankarar da mutanen Nijeriya kan yanayin yadda ake tafiyar da siyasar qasar nan. Lokaci ya yi da jama'a da shuwagabanninsu, za su tafiyar da rayuwarsu kan tafarkin dimokraxiyya, wanda ya shafi zaven shugaba na gari. Ya ci gaba da warwarar jigo, yana bayyana saqonnin da waqar ke son ta isar ga jama'a, musamman ga shi an cika shekara hamsin da samun 'yancin kai, amma babu wani abin a zo a gani a qasar nan, komai sai lalacewa yake yi. Su mahukuntan kansu kawai suka sani, ba su kula ha haqqin jama'a. Haka dai ya yi ta tattauna matsalolin Nijeriya.

Ayyukansu Amin (2008 da 2008) da Xan'asabe da Wushishi (2008) da na Bello (2009 da 2011) duk sun taimaka wa wannan aiki matuqa. Ayyukansu suna da alaqa ta ququt da wannan, domin sun yi magana kan fitattun waqoqin siyasa na zamani masu nufin canza tunanin jama'a. Ayyukan Amin (2008 da 2008) ya haskaka wannan sosai. Haka ma nasu Xan'asabe da wushishi (2008) ya agaza domin sun yi nazarin waqar da wannan bincike zai duba, an yi amfani da shi domin a qara fahimtar waqar, da ma fito da tasirinta ga zukatan 'yan Nijeriya. Na Bello (2009 da 2011) ba daga baya ba, don shi ma ya yi aiki a kan wata waqar da wannan bincike ya duba, don haka, an amfana da shi matuqa, musamman wajen gano manufar mawaqin da bayyana abubuwan da waqar ta qunsa.

Gusau (2010 da 2010 da 2011 da 2011 da 2011 da 2013 da 2013) duk ya yi nazarce-nazarce a kan waqar baka da rubutacciya. Gusau (2010) ya yi magana kan rawar da ta kamata marubuta waqoqin Hausa su taka wajen kyautata rayuwar al'umma. Ya kawo dabaru da suka kamata a rinqa xora rubutattun waqoqi a kansu. Ya kawo wasu manyan hanyoyi guda uku wanda

marubuta waqoqi kan bi domin tsara waqoqinsu. Hanya ta farko ita ce wadda ake kira *jibiliyya*, hanya ce wadda Allah SWT Yake ba wa mutum baiwa ta tsara waqa. Hanya ta biyu ita ce ta koyo, wadda mutum zai koya daga wani mutum wanda ya iya rubuta waqa. Hanya ta uku, ita ce ta lalura misali son wani abu ko tsoronsa ko canje-canjen rayuwa na iya sa mutum ya yi waqa. Ya nuna sai mutum ya karkata ga xayan waxannan hanyoyi sannan zai iya zama marubucin waqa.

Ya rattabo zanguna na marubuta waqoqin Hausa tun daga qarni na sha tara wanda malamai ne yawancin marubuta waqoqin. Haka aka gangaro har zuwa qarni na ashirin zuwa lokacin da ake ciki. Ya nuna yadda ya kamata marubuci ya fahimci harkokin rayuwa na al'umma da buqatunsu, sai ya shirya waqa a kai. Shi ya sa waqoqin da aka rubuta a qarni na sha tara da ashirin suke xauke da manufofi da saqonni da suka shafi rayuwar jama'a. Matakan da suka kamata marubuci ya bi su ne saqonnin da ya kamata waqa ta qunsa, ya kuma gina waqa a kan ingantaccen saqo, shi ne zai sa ta zama mai amfani ga jama'a. Ya jero saqonni manya da qanana da ya kamata marubuta su rinqa waqa a kansu irin ayyukan ibada kamar tsarki, wanka alwalla. Sai faxakarwa da gargaxi da tunasarwa da wayar da kai. Daga cikin matakan akwai aiwatar da waqa don ana buqatar marubucin waqa ya zama mai tunani a kan rayuwa da hangen nesa da kuma iya zaven kalmomi. Ana son marubuci ya kaifafa tunaninsa, ya inganta zaven kalmomi, ya saqa tunani mai nauyi, ya kuma kiyaye furucinsa. Wani matakin kuma, shi ne na karin muryar waqa. Ya kamata waqa ta ginu bisa ingantaccen kari. Sai zubin saxaru na rubutacciyar waqa misali gwauruwa, 'yar tagwai da sauransu. Sai kwalliyar waqa wadda take da muhimmanci a waqa rubutatta. An so marubutan su zama masu amfani da dabaru don qayatarwa. Sai sadar da rubutattun waqoqi,

wanda yake da muhimmanci don ya qunshi inda waqa ta dosa, muhalli da lokaci da jama'ar da aka yi domin su. Aikin nasa yana da alaqa da wannan.

A wata takardar kuma, Gusau (2010) ya kawo hanyoyin nazarin waqar baka ta Hausa a taqaice. Ya zayyano wasu hanyoyi da ake amfani da su wajen nazarin waqar baka kamar gidajen rediyo da talabijin na yadda suke yi wa waqoqin baka hidima. Bayan an tattara waqoqin a fayafayai da kasakasai, sai su rinqa amfani da waqoqin baka cikin shirye-shiryensu, inda suke yin sharhi game da waqoqin baka na Hausa. Kamar yadda ya bayyana suna yin sharhin ne ta fuskar fassara wasu kalmomi na waqa, sannan su bayyana qananan saqonni, rayuwar makaxa da irin kayan kixan da yake amfani da su. Ya nuna makarantun soro ko na zaure suna taimakawa wajen nazarin waqoqin baka na Hausa. Ta yadda malaman kan yi amfani da wasu xiyan waqar baka ta Hausa domin su kafa hujja kan tarjamar da suke yi wa kalmomin Larabci zuwa Hausa. Makarantun soro wani zango ne na yi wa waqoqin baka hidima a kaikaice kamar yadda ya bayyana. Ya kawo yadda makarantun boko suke taimakawa wajen nazarin waqoqin baka na Hausa.

Bayan haka, ya kawo haxaxxiyar hanyar nazarin waqar baka ta Hausa. Ya nuna ayyukan da aka fara yi kan nazarin waqar baka ta Hausa an yi su ne ta bin wasu taqaitattun hanyoyi na fixar waqar baka kamar nazarin turke ko tsarin rerawa da sauransu. Amma daga baya Gusau (1993) ya yi wani aiki na tattara waxannan matakai a cikin littafinsa *Jagoran Nazarin Waqar Baka* (1993). An gwada waxannan azuzuwa a matakan digiri na xaya da na biyu da na uku. Daga baya a shekarar (2003) ya sake tsara wannan hanya zuwa muhimman matakai guda biyar. Wannan aikin nasa ya danganci wannan.

Gusau (2011) ya yi bitar littafin waqoqin Aminu Ladan Abubakar: Alan waqa na Muhammad Lawal Barista (2011). Da farko ya kawo taqaitaccen tarihin Aminu Ala. Ya nuna an haifi Ala a Kano a unguwar Yakasai. Ya yi karatun addini da na boko. Ya yi rubutun littattafai irinsu *Jirgi Xaya*. Ya shugabanci qungiya ta marubuta ta jihar Kano. Ya taso da sha'awar waqa har zuwa yanzu. Ya zayyana zubin waqoqin Ala cewa yana fara rubuta waqoqinsa, sannan ya rera su, tare da amfani da kayan kixa kamar fiyano. Ya nuna saboda yanayin rerawa da amfani da kayan kixa ya sa ake kiran waxannan mawaqa da makaxan baka na zamani. Amma wasu na ganin duk da salon rerawa ana iya kiransu rubutattun waqoqi. Ya kawo qumshiyar littafin yana xauke da waqoqi hamsin da biyar da aka zuba a cikin album har guda goma da aka raxawa sunaye da la'akari da saqonninsu. Waqoqin na xauke da darussa kan sha'anonin rayuwa kamar ilmi, shugabanci da sauransu. Aikin Gusau (2011) yana da alaqa da wannan aiki, don ya tavo waqoqin Aminu Ala tare da kawo taqaitaccen tarihinsa, wanda ma wannan aiki ya yi haka. Ya kuma yi maganar matsayin irin waqoqin wanda wannan aiki ma ya yi haka.

A wata muqala tasa Gusau (2011) ya hango wata mahanga ga mawaqa da makaxan Hausa, inda ya kawo yanayin waqoqin Hausa guda biyu, waqoqin Hausa na baka da kuma waqoqin Hausa rubutattu. Ya nuna waqoqin baka su ne Hausawa suka fara yi tun farkon rayuwa. Daga baya Hausawa suka iya karatu da rubutu. Sai aka samu marubuta waqoqi suna rerawa tare da kixa. Irin waxannan waqoqi a kan kira su da waqoqin baka domin rauji da rerawa da kixa. Daga haka ne aka samu waqoqin baka iri biyu, waqoqin baka na gargajiya da na zamani. Rubutattun waqoqin Hausa su ne ake rubutawa a cikin ajami da kuma boko a kan takardu. Ba a rera su da kixa, sai dai

amfani da qafiya da adadin layuka cikin baitoci. Sannan ya jero mahanga da ya kamata mawaqa da makaxan Hausa su yi la'akari da su wajen shirya waqoqinsu kamar aiwatar da waqoqin, saqonnninsu da sadarwa a cikinsu. Wannan aiki yana da alaqa da wannan don ya yi tsokaci kan matsayin irin waxannan waqoqi na Hausa na yanzu. Inda aikin ya nuna waqoqin a matsayin baka na zamani. Wannan aiki ma ya yi qoqarin tantance matsayin waqoqin daidai gwargwado.

A wata muqala ta Gusau (2011) ya yi taqaitaccen tarke kan waqar *Jami'a* ta Aminu Ladan Abubakar. Ya yi nazari a kan waqar *Jami'a* wadda ya nuna cewa an rera waqar ta amfani da kayan kixa na fiyano, tare da 'yan amshi. An rera waqar har kashi uku a lokutta daban-daban. Gusau ya bayyana cewa akwai kamanceceniya ta zubi a rerawa ta farko da ta biyu, sai dai kixansu ya sha bamban. Rerawa ta uku cikin hankali aka yi ta. Rerawa ta farko tana da xiya goma sha tara, ta biyu tara, sai ya uku tana da xiya goma sha biyu. Daga nan, sai ya kawo tarihin Aminu Alan waqa. Ya kawo bayanin mai waqa cewa ya yi wa Jami'ar Nijeriya waqa ne. Jami'a wuri ne da ake bayar da ilmi da tarbiyya ga al'umma. Fage ne na koyo da koyarwa da kaifafa tunani kamar yadda Gusau ya bayyana. Ya yi bayanin turken waqar na faxakarwa ne. Ya nuna cewa "Mawaqin nan, Alan waqa, ya shirya waqar ne domin ya yi faxakarwa da tuni kan ayyuka na Jami'a, tun ma ba waxanda suka shafi malamai da sauran ma'aikata ba, da darussa da take badawa da yadda mutane suke ci gaba saboda rabauta da ilminta". Sai tubalan da Ala ya yi amfani ya gina waqar kamar halaye na malamai masu kyau da munana, wasu ayyuka na jami'a, wasu al'adun Hausawa, addu'a da roqon Allah da sauransu. Ya kawo yawan saxaru a xiyan waqar, sai tsarin rerawa, da amsa-amon kari. Ya kawo salo da sarrafa harshe na waqar. Ita ma wannan takarda ta Gusau tana da dangantaka da wannan tunda ta yi magana kan waqar *Jami'a* Aminu Ala wadda aka aiwatar da abin kixa na fiyano duk da dai wannan aiki bai yi amfani da

waqar ba, amma aikin ya taimaka da qarin haske wajen nazarin waqoqin da ka yi aiki a kansu. Kuma waqoqin da aka yi nazarinsu an yi amfani abin kixan fiyano wajen aiwatar da su.

Gusau (2013) ya yi maganar hanyoyin aiwatar da waqoqin Hausa cewa waqoqi ne waxanda ake rerawa ta amfani da harshe mai zalaqa da karsashi, mai lugga da hikima. Ya nuna waqa na shiga kowane vangare na rayuwar al'umma. Mawaqan Hausa mutane masu hikima da azanci na shirya waqoqi don raya adabin Hausa. Ya ci gaba da kawo muhimmancin mawaqa da waqoqinsu.

A wata muqala tasa, Gusau (2013) ya kalli mizanin da ke tsakanin waqoqin Hausa na baka da rubutattu. Ya bayyana da kuma rarraba hanyoyin da ake aiwatar da tsara waqoqin baka da rubutattu da kuma irin saqon da kowace ke xauka ko ke zuwa da shi. Ya tattauna wuraren da waqoqin suka yi tarayya da kuma inda suka bambanta. Da farko ya kawo tarihin Hausawa a dunqule, sai waiwaye kan samuwar waqar baka da rubutatta. Ya kawo wasu matakai na rarrabe waqar baka da rubutatta ta vangaren sigoginsu. Inda ya kawo bambance-bambancen da ke tsakaninsu musamman bambanci na kixa da rauji da gindin waqa da ake samu kawai a waqoqin baka. Ya qara kawo hanyoyin aiwatarwa da tsarawa da sadarwa na waqoqin. Sai kuma ya zayyana bambanci da kamanci na waqoqin ta fuskar aiwatarwa da sadarwa. Ga kuma saqonnin da waqoqin suke qunsa. Ya bayyana wasu muhimman turaku da jigogin waqoqin Hausa. Ya jero kalmomin fannu na nazarin saqonnin waqoqin. Sai dabarun salo da sarrafa harshe a cikin waqar baka da rubutatta. Wannan takarda tana da alaqa da wannan aiki saboda ta yi qoqarin rarrabewa tsakanin waqar baka da rubutatta, duk da dai Gusau (2013) bai faxi matsayin waqoqin Hausa na yanzu ba, amma aikin ya taimaka sosai wajen rarrabewa tsakanin waqoqin biyu.

Duka ayyukan Gusau (2010 da 2010 da 2011 da 2011 da 2011 da 2013 da 2013) suna da dangantaka da wannan aiki domin sun yi maganar ruhin wannan aiki, wato waqa. Duk da dai kowace takarda da inda ta dosa, amma dukkansu sun taimaka wajen fito da qwarangwal xin waqa, ta yadda za a iya tantancewa tsakanin waqar baka da rubutatta. Ayyukan sun agaza qwarai.

Tsoho (2013) da Zainab (2013) sun yi rubuta a kan waqoqin fiyano na Hausa, sai dai kowa da inda ya fi karkata. Tsoho (2013) ya yi rubutu kan waqar *Shegiyar Uwa* ta Haruna Ningi, inda ya dube ta a matsayin waqar bijirewa ta siyasa. Ya nuna yadda mawaqa ke amfani da waqa a sha'anin siyasa, su nuna rashin amincewarsu na yadda ake tafiyar da siyasa. A muqalar ya fito da ra'ayin Ningi na bijire wa jam'iyyar PDP a lokacin. Ya kawo taqaitaccen tarihin Haruna Aliyu Ningi. Ya nuna cewa Ningi ya yi wannan waqa ta *Shegiyar Uwa* bayan ya yi wasu waqoqi na yabawa da kwarzanra jam'iyyar PDP da wasu jam''iyyu a Nijeriya. Haka ya tsettsefe waqar dalla-dalla yana nuna bijirewar mawaqin.

Ita kuwa Zainab (2013) ta fito da gudunmuwar mawaqan Hausa wajen farfaxo da arewacin Nijeriya, inda ta duba waqar *Ajanda* ta Haruna Aliyu Ningi. Ta bayyana yadda waqar ta tattauna matsalolin arewa, tare da fito da hanyoyin magance su. Mawaqan na jawo hankalin 'yan arewa su zama masu kishin kai da tabbatar da ganin an samu sauyi a yanayin zamantakewar arewa. Ta nuna cewa tun bayan shuxewar waqoqi irinsu *Arewa Jumhuriya Ko Mulukiya* ta Sa'adu Zungur, ba a sake jin motsin wasu waqoqi masu kira da a yi kishin arewa ba, sai yanzu aka samu waqoqi masu manufa irin tasu. Waqar ta yi maganar halin da arewa take ciki, inda mawaqin ya ta'allaqa laifin lalacewar ga shuwagabanninta. Ta kawo tarihin Haruna Aliyu Ningi. Ayyukansu suna da

dangantaka da wannan, don sun yi maganar shahararren mawaqi Ningi da irin gudunmuwar da yake bayarwa a fagen siyasa. Wannan aiki ma ya duba wasu waqoqi na Ningi. Tare da kawo taqaitaccen tarihinsa.

## 2.3 Bugaggun Litattafai

Akwai littattafai da dama, da aka buga masu dangantaka da wannan aiki. Wasu sun yi magana kan farfaganda, wasu kan waqa, inda wasu suka yi kan harkokin siyasa. Daga cikin litattafan da suka yi magana kan farfaganda akwai *Kundayen Encyclopedia America da Britannica, da Qamusoshi na Concise Oxford English Dictionary , Shorter Oxford, Chambers da New Book of knowledge* da sauran makamantansu.

A cikin Kundin *The 21st Century Websters International Encyclopedia* an bayyana farfaganda da cewa " Zavavvun bayanai, imma dai na gaskiya ko na gizo da aka tsara domin shawo kan mutane su amince da gasgata wani abu, xabi'a ko ummul aba'isin wani al'amari".

A Kundin *Britannica Concise Encyclopedia* an nuna cewa farfaganda na nufin "Juyar da akalar bayanai domin samun damar sauya ra'ayin mutane. Kalmar ta samo asali daga sunan wannan qungiya 'Congregatio de propaganda fide', (qungiyar haxin kai ta yaxa addinin Kirista). Wata qungiyar Mishan wadda shugaban jagoran addinin Kirista (pope) a shekarar 1622 ya qirqiro. Xan farfagandar ya ba da goyon bayan amfani da ire – iren bayanai da ba za su kawo matsala ba, ko fitar da waxanda ba za su yi daidai ba. A iya amfani da vatattun maganganu da qarairayi wajen samun damar gina tubalin da ake so a gina a cikin zukatan mutane masu sauraro. Lallava da

tallace – tallace da aikace aikacen Mishan duk wani nau'i ne na yaxa farfaganda. Amma dai an fi amfani da kalmar a harkokin siyasa.

A cikin Concise *Oxford English Dictionary* an kawo ma'anar farfaganda cewa "Labari ba ma kamar mai rikitarwa, ko ruxarwa da ake amfani da shi domin qara azarvavi kan manufofin siyasa. An bayar da asalin kalmar da cewa daga wani kwamiti ne na Roman Katolika da ke da alhakin kula da harkokin qasashen waje.

A cikin *Shorter Oxford English Dictionary On Historical Principles*, kalmar ta samo asali daga harshen Italiya 'congregation de propaganda fide', qungiyar haxin kai domin yaxa addinin Kirista. Wato wani Kwamitin manya – manyan 'yan Cocin Katolika da ke da alhakin kula da manufofin qasashen qetare wadda shugaba Gregory' xv, na sha biyar ya qirqiro. An fi sanin qungiyar da qungiyar farfaganda ko kwalejin farfaganda. An qara nuna cewa wata qungiya ce ta 'yan sintiri ko fafitika domin yaxa wata xariqa ko wata aqida da sauransu. An bayyana ma'anar farfaganda "Wata haxaxxiyar hanyar yaxa aqida ko wasu kevavvun bayanai domin havaka wata aqida, ra'ayi ko xabi'a da makamantansu. An sake bayar da ma'anar da cewa "Yaxa shawarwari ko wasu bayanai da kuma duk wani qoqari na jan hankali".

A cikin *Chambers 21st Century Dictionary* an ce farfaganda na nufin "Taron gangamin wata qungiya ta 'yan siyasa, domin a yaxa wata manufa ko bayani ko qarya ko saci- faxi ko wani ra'ayi da nufin canza tunanin mutane, faxakar da al'umma don kawo wani sauyi". Duk abin da aka yaxa ta wannan hanya, shi ne farfaganda.

A Qamusun *A Student's Dictionary* an nuna farfaganda cewa "Wani qoqari domin yaxa wata manufa".

Shi kuwa Qamusu mai suna *Random House Webster's College Dictionary* cewa ya yi farfaganda na nufin "Labarai ko wasu dabaru da ake yaxa su cikin hikima domin qara zafafa wutar rikici. An qara cewa farfaganda wata mazahaba ce ko qa'idoji da wata qungiya ke yaxawa, qoqarin yaxa waxannan dabaru ne, ba tare da la'akari da abin da ka- je- ka- dawo, ba shi ne Farfaganda.

A cikin qamusu mai suna *The New International Webster's Comprehensive Dictionary Of The English Language* an rattabo farfaganda da "Ta samo asali daga wata qungiya ta manya- manyan Coci masu sa - ido a harkokin qasashen qetare. Kuma wani kwaleji ne na yaxa addinin Kirista wanda shugaban jagoran Kiristocin duniya Uban na 8, a 1627 ya qirqiro domin ilmantar da malaman Mishan. Kuma ana kiran qungiyar da Kwalejin Farfaganda.

A Littafin *The New Book Of Knowledge* cewa ka yi "Farfaganda na nufin duk wani qoqari domin yaxa wata manufa, wadda kan kasance ta fuskoki daban daban, tana iya zamowa wata tattaunawa tsakanin jama'a ko wani tsokaci a rubuce. Tana kuma iya zama a fina- finai ko waqe-waqe a gidajen rediyo, ko wasu hotuna. Kalmar farfaganda ta samo asali daga kalmar harshen Latin propagare, to propagate a Ingilishi, ma'ana a yaxa. Tana kuma nufin a watsa ko a isar daga wani zuwa wani. A ma'ana ta haqiqa, farfaganda na nufin duk wata dabara ta sadar da saqo, amma fa kalmar ta wuce a ce sadarwa kawai, har ta kai matsayin sauya tunani. A ma'anar bai xaya kuwa, tana nufin duk wani qoqari domin canza wa mutane tunani daga abin da yake gaskiyar al'amari. Farfaganda a wasu lokutta tana taimakawa wajen tunzura mutane ya zuwa xaukar mummunan mataki, saboda haka, sai ake xaukarta a matsayin wani abu marar kyau. Duk da haka, tana iya kasancewa mai kyau ko marar kyau, ya danganta da manufar da aka yi ta.

A *Encyclopedia Britannica* Bugu na 9 an kawo ma'anar farfaganda cewa "Watsa labarai ne na gaskiya ko qarya don a samu tasiri ga wani tunani na mutane. Ana amfani da abubuwa kamar zane, magana, tufafi da sauransu".

A Kundin *Encyclopedia Britannica* Bugu na 15 an bayyana farfaganda da cewa "Wani shiryayyen yunquri da a kan yi don juya ko don a samu tasiri a tunanin al'umma ko wani qoqarinsu ta yin amfani da wasu alamomi kamar rubutu, ko motsa jiki, ko kixa, ko ta yin amfani da tufafi, ko hoto da sauransu. Amfani da ake yi da qarya da yaudara a wajen yaxa farfaganda, shi ya bambanta ta da zance na yau da kullum. Mai farfaganda yana da wasu manufofi da qudiri da yake so ya cimmawa. Kafin ya cimma su sai ya bi ta wasu hanyoyi da shi yake ganin zai samu nasara. Don cimma manufa, yana iya qin gabatar da haqiqanin al'amari don ya janye hankalin mutane daga kowane tunani sai nasa. Haka kuma, yadda ake shirya farfaganda da zaven abin da za a yi amfani da shi wajen aiwatar da ita, ya bambanta ta da ilmi, saboda mai ilmi yana qoqarin kawo abin da yake daidai, tare da kawo alfanu ko rashin alfanun abu. Wani lokaci mai farfaganda na iya xaukar kansa wani mai yaxa ilmi, domin shi a wurinsa haqiqanin abu ne yake gabatarwa. Haka kuma, wanda ake yi wa farfaganda na iya xaukar ta wani ilmi".

A Qamus na *Encyclopedia Britannica* (1966:390) kalmar na nuna cewa hanya ce ta baza labari. Wannan labarin na iya tabbata gaskiya ko abin taqaddama ko jita-jita, ko mai alamun qamshin gaskiya ko ya zamana qarya ce tsabarta domin a jawo hankula ko ra'ayin jama'a. Amma kuma a Qamus na *International Encyclopedia Of The Social Sciences* (1968: 584) an nuna ma'anar kalmar farfaganda da cewa "Sassauqar hanya ce ta yin amfani da wasu fitattun alamomi, ko tuta ko mutum-mutumi na wani abu ko kaxe-kaxe da waqe-waqe". A cikin Qamus na *Turanci Da Hausa ( Hausa- English Dictionary)* an bayyana farfaganda da cewa " Baza ra'ayi don lallashin jama'a".

Dambo (1999) ya nuna farfaganda cewa " Farfaganda asalinta daga harshen Ingilishi take. Ya ci gaba da nuna cewa a qamus na *Encyclopedia Britannica* (1966:390), kalmar na nuna cewa wata hanya ce ta baza labari, wannan labari na iya tabbata gaskiya ko abin taqaddama ko jita-jita, ko mai alamun qamshin gaskiya ko ya zamana qarya ce tsabarta domin jawo hankula ko ra'ayin jama'a." Dambo (1999) ya ci gaba da nuna cewa "Amma qamus na *International Encyclopedia Of Social Sciences* (1968:583) an nuna ma'anar kalmar farfaganda da cewa 'Sassauqar hanya ce ta yin amfani da wasu fitattun alamomi, wato kamar irin mazaganun bebaye ko tuta ko mutum-mutumi na wani abu ko kaxe-kaxe ko waqe-waqe da sauransu." A nasa ra'ayin cewa ya yi " Farfaganda hanya ce ta baza ra'ayi domin lallashi da jawo hankalin jama'a domin isar da wani sabon tunani zuwa ga wani ra'ayi ko tunani nata, da a da ta riga ta runguma, kuma ake son yanzu a karvi sabon abin da aka zo da shi".

Jumare (2007) ya nuna farfaganda da cewa " Hanya ce ta jawo hankalin jama'a domin yin na'am da wani sabon abu ko kuma qarin karvuwa ga wani abu da dama can aka sani ko kuma nuna qyama ga wani abu."

Hassan (2011) kuwa cewa ya yi, " Farfaganda tana nufin yaxa manufofi ko tallata haja da muradin wata al'umma ko qasa ko tsari na siyasa ko tattalin arziqi ko tallata wata haja da nufin sauya tunanin al'umma ko karkato da hankalinsu kan abin da ake yaxawar ko tallatawar." An kasa farfaganda zuwa kashi uku:

- Farar Farfaganda (white propaganda)
- Baqar Farfaganda ( Black Propaganda)
- Jirwayen Farfaganda ( Grey propaganda)

**i. Farar Farfaganda**: Farfaganda ce wadda aka san haqiqanin gaskiyar tushenta ko asalinta. Farfaganda ce wadda aka fi sani, aka fi yi kuma akasari tana zuwa ko fitowa daga kafar da aka sani kuma aka shaida. Sannan ana amfani da sassauqar hanya domin a sauya tunanin jama'a ko a shawo kansu. Tana kuma bayyana haqiqanin gaskiyar al'amari. Ga maganar addini da vangaranci da tunkarar lamari kai tsaye don samun biyan buqata.

Jumare (2007) ya bayyana ma'anar farar farfaganda cewa "Wannan ita ce nau'i na farko a kashe-kashen farfaganda. Wannan wata farfaganda ce mai tsafta, mai kyau ta kowace fuska kuma babu qarya a cikin ta ko yaudara."

Mannura (2008) ta bayyana ma'anar farar farfaganda cewa "Daga jin sunanta, za a yarda da cewa tana da tsabta kuma ba qarya ko yaudara a cikinta ta ko'ina. Kuma masu yin wannan farfaganda na yi don jawo hankali ko faxakar da jama'a ga abu mai kyau."

Hassan (2011) cewa ya yi "Farar farfaganda ita ce farfaganda wadda ake sanin daga kafar da take fitowa. Takan zo cikin sassauqar hanya ko ta wajen amintattun hanyoyi da zummar jan hankali ko juya tunanin jama'a. Takan bi ayyanun hanyoyi na mu'amala tare da fuskantar lamari kai tsaye. Akan yi amfani da addini ko qabilanci ko vangaranci domin a cimma burin da ake buqata."

**ii. Baqar Farfaganda**: Farfaganda ce wadda ake yi don a muzanta abu, a kunya ta shi, kuma a vatar da tunanin jama'a, akasari an fi samun irin wannan farfagandar daga abokan gaba. Baqar farfaganda tana qoqarin ta rikita tunanin mai tunani domin hanyoyin gudanar da ita da hanyar da ta fito da alfanunta da abin da ta qunsa duka a lulluve suke. Haka nan kuma, a kasafai ake gane cewa ana qoqarin a samu tasiri akan jama'a ba.

Jumare (2007) cewa ya yi “Wannan farfaganda ce wadda ko da jin sunanta an san ba alheri a cikin ta domin kuwa irin wannan farfaganda, farfaganda ce ta qarya ko yaudara ko muzantawa da cin fuska da qasqanci da dai duk wata hanya ta wulaqanta mutum. Kuma ana yin ta domin cimma wani buri na siyasa ko na zamantakewa da sauransu.”

Mannura (2008) cewa ta yi “Wannan nau’i na farfaganda, da jin sunan ba sai an yi dogon bayani ba, an san cewa ba alheri a cikinta don ta qunshi qarya da yaudara da muzantawa da cin fuska da duk wani salo na qasqantar da mutum. Kuma galibi, zama ake yi a qirqiri abun da za a faxi ko yaxa, wanda idan aka yi bincike, za a gane cewa komai akasin abin da aka faxa ko aka yaxa ne.”

Hassan (2011) ya bayyana baqar farfaganda cewa “Farfaganda ce da kan yi shigar burtu, jama’a su kasa gane daga inda take fitowa. Ana yin hakan ne domin a voye ainihin sanin inda makamar zancen yake, daga wurin abokan gaba ne ko daga wata qungiya ce mai munanan manufofi?”

**iii. Jirwaye ko wake-waken Farfaganda**: Ita ce farfaganda wadda ba a gane daga inda ta fito ko su wa ke yin ta. Tana kama da gaskiya, wani lokaci kamar qarya. Tana juya tunanin jama’a a kasa gane haqiqanin gaskiyar al’amari.

Jumare (2007) ya ba da ma’anar jirwayen farfaganda cewa “Farfaganda ce mai ruwa biyu wato haxaka da gaskiya da qarya, ko gaskiya da yaudara domin qarawa abin da ake wa farfaganda armashi da tagomashi.”

Mannura (2008) cewa ta yi “Wannan nau’i na farfaganda ce ‘yan siyasa suka fi amfani da ita saboda ta qunshi fuska biyu, wato ta qarya da gaskiya ko gaskiya da yaudara, domin su qara wa abin da suke yi wa farfaganda armashi, don cimma burinsu.”

Hassan (2011) ya ayyana cewa “Farfaganda ce wadda ba a sanin daga inda ta fito ko wa yake yin ta, tamkar dai takan yi xad-da-bami ne. Akan jirkita tunanin mai tunani da ita. Takan yi kama da gaskiya-gaskiya, ta kuma yi qoqarin nisanta kanta da qarya kai tsaye. Takan sa jama’a cikin ruxu da kasa rarrabewa da gaskiyar lamari.”

Da Sarvi (2007) da Gusau (2008) da Xangambo (2008) duk sun yi nazari kan waqar baka da rubutattu, sai dai kowane akwai abin da ya fi ba da qarfi a kai. Shi Sarvi (2007) ya wallafa littafi kan yadda ake nazarin waqoqin Hausa. A ciki an yi bayanin ma’anar rubutacciyar waqa, inda ya nuna cewa babu wata sahihiyar ma’ana da masana suka bai wa waqa, abin da marubuta suka fi yi a cewarsa, sukan yi la’akari da abubuwan da waqa ta qunsa wajen bayar da ma’anarta. Ya bayyana nau’o’in waqoqin Hausa, kamar gwauruwa, qwar xaya da sauransu.. Ya duba ma’aunin waqa, mabuxi da marufi. Sai kuma nazarin jigo da ya yi , inda ya nuna yadda ake gane jigo a waqa, ya ce ko marubuci ya faxi jigo, wato manufar waqarsa ko kuma mai nazari ya yi la’akari da kalmomin fannu. Ya yi maganar salo da sarrafa harshe. Ya nuna yadda ake nazarin rubutacciyar waqa sosai da sosai. Wannan aiki na Sarvi (2007) ya qara wa wannan haske sosai, domin an yi nazarin waqoqin na farfaganda, sai dai a wata siffa daban.

A yayin da Gusau (2008) ya yi nazarin waqoqin baka na Hausa, inda ya duba yanaye-yanayensu da sigoginsu. Mawallafin ya yi zuzzurfan nazari kan waqoqin baka, sai dai alaqar aikinsa da nawa tana nan inda ya duba waqoqin baka na siyasa, duk da dai cewa wannan aiki ba a kan waqar baka ba ne, amma ya bayar da haske wajen qara fahimtar yanayin waqoqin siyasa. Gusau (2008) ya bayyana cewa waqoqin siyasa na baka su ne waqoqin da ake yi wa muqarraban siyasa da ita kanta jam'iyyar. Ya kawo misali da waqar Sarkin Taushin Katsina mai suna *Samun 'Yancin Nijeriya A 1960*. Wata dangantakar aikin Gusau (2008) da wannan, ta qara fitowa a inda malamin ya yi maganar waqoqin kixan fiyano. Ya bayyana kixan fiyano da sabon abu a wajen Hausawa, wanda suka suka samu sanadiyar cuxanya da Turawa. Ya yi wadataccen bayani kan samuwar irin waqoqin a qasar Hausa. Ya kuma bayyana ra'ayinsa dangane da matsayin waqoqin a yanzu, inda ra'ayin ya fi karkata kan cewa waqoqin baka ne.

Xangambo (2008) kamar Sarvi (2007), wallafar tasa ta shafi manyan hanyoyin nazarin waqa da sharhinta. Ya yi bayanin hanyar nazari ta gargajiya da ta zamani. Ya nuna hanyar nazari ta gargajiya da ba wata fitattar hanya ba ce wadda aka tsara . Ita kuwa hanyar nazari ta zamani, ya nuna cewa ta haxa da hanyar nazari ta gargajiya, ta Larabawa da kuma ta Turawa. Ya kawo abubuwa masu muhimmanci da ake dubawa wajen nazarin waqa, kamar su jigo, salo da zubi da tsari. Shi ma wannan littafi ya taimaka wajen sanin abin da waqa ta qunsa.

Yahaya (1988) da Furniss (1995) da (1996) duk sun wallafa litattafai a kan adabi, al'adu da wasu al'amura na Hausawa. Yahaya (1988) nasa rubutun bakandame ne, don kusan ya tavo komai na Hausawa. Ya yi maganar yadda aka samu ilmin karatu da rubutu a qasar Hausa. Ya tavo

rubutattar waqar Hausa, inda fara magana tun daga samuwar waqoqi a Qarni 18, wato irin waqoqin su malam Muhammadu na Birnin Gwari, Shitu Xan Abdul-Ra'ufu da sauransu. Daga nan ya gangaro zuwa Qarni na 19, wanda ya taimaka wajen havakar rubutattun waqoqi a Hausa. Dangantakar wannan aiki ta fito, a inda aka yi batun waqa, don aikin ya taimaka sanin asalin waqoqin Hausa gaba xayansu. Bayan dangantaka kan waqa, sanin tarihin rubuce-rubucen Hausa ya taimaka qwarai.

Furniss (1995) da (1996) duk ya yi magana kan waqoqin Hausa. Furniss (1995) ya nuna cewa an yi rubuce-rubuce na waqoqi da dama na farfaganda. Misali waqar *Nepu Sawaba* ta Aminu Abubakar Kurawa. Ya bayyana wannan waqa da xaya daga cikin waqoqin da 'yan NEPU suka yi na farfaganda a lokacin zave a shekarar 1964. A cikin waqar an nuna cewa Aminu Kano shi ne shugaba, sai taken jam'iyyar *sawaba*. Furnis (1996) alaqar ayyukan nasa da nawa ya fi fitowa a inda ya bayyana waqoqin Hausa da sigoginsu. Ya yi batun waqoqin siyasa, musamman na jam'iyya, wanda ya nuna waqoqin sun fi mayar da hankali wajen yabon 'yan takara. Haka kuma, ya yi nuna bambanci tsakanin waqar baka da rubutatta, inda ya qara jaddada ra'ayin Muhammad (1979) kan bambancin waqar baka da rubutatta, hakan kuma yana da dangantaka da wannan aiki.

Da Appadorai (1974) da Yakubu (1999) duk sun duba abin da ya shafi harkokin siyasa, sai dai shi Appadorai (1974) siyasa ya kalla a matsayin wani ginshiqin abu. Ya kawo ma'anar siyasa da cewa wani nazari ne na kimiyya da ya danganci al'amurran mutane na zamantakewa da tafi da rayuwa. Ya yi magana kan dangantakar Siyasa da Kimiyya, da ya nuna cewa shin ko akwai dangantaka tsakanin nazarin harkokin Siyasa da nazarin Kimiyya. Sai ya nuna cewa nazarin Kimiyyar Siyasa, ba daidai yake da nazarin Kimiyya na ainihi ba. Ya ce nazarin Kimiyya na

ainihi, nazari ne na haqiqa, wanda ya danganci Kimiyya sosai da sosai. Amma nazarin Kimiyyar Siyasa, nazari ne da ya shafi xan'adam da abin da ke tattare da shi. Ya duba alaqar da ke tsakanin siyasa da Tarihi da Tattalin Arziqi. Ya nuna dangantakar da cewa, kasancewar Tarihi ya qunshi abubuwan da suka shuxe, wato ya qunshi binciken abubuwan addini, tattalin arziqi da kuma siyasa. Ya rattabo dangogin siyasa kamar Kwansitushin, ra'o'in siyasa da sauransu.

Shi kuwa Yakubu (1999) Sa'adu Zungur ya kalla da irin gudunmuwar da ya bayar a Arewancin Nijeriya da ma Nijeriyar gaba xaya. Ya yi bayanin aikace-aikacensa, tun daga quruciyarsa da tasowarsa, har zuwa shigarsa harkokin siyasa gadan-gadan. Sai waqoqinsa kamar *Arewa Jumhuriya Ko Mulukiya, Addakari, Yaqi da Shaixan,* da sauransu.

Dukkan ayyukan na nasu, suna da alaqa da wannan, don sun tavo siyasa, musammam ma na Appadorai (1974) da yake wani ginshiqi na masu nazarin Kimiyyar siyasa, wanda ya taimaka sosai waje sanin makamar siyasa. Na Yakubu (1999) ma ya taimaka, duk cewa nazarinsa ya shafi mutum guda ne, shi ma gwarzon nasa ya yi wasu waqoqi na farfaganda, yana wayar da kan al'ummar Arewa da su san inda kansu ke masu ciwo wajen zaven nau'in mulkin da za a yi. Saboda haka, irin waqoqinsa sun taimaka wajen gano ire-iren waqoqin farfaganda na wannan lokaci. Duk da kusancin ayyukan, akwai kuma inda suka bambanta, inda shi Appadorai (1974) siyasar ce ya kalla tsura, Yakubu (1999) kuwa, nasa aikin abu xaya ya fuskanta, inda wannan ya yi nazarin irin farfagandar da ake yi kan harkokin siyasar.

Crowder (1962) da Kirk-Greene da Rimmer (1981) da su Falola (1991) da Falola da Heaton (2008) sun yi maganar tarihin Nijeriya da siyasa da abubuwan da suka faru tun lokacin kafuwar qasar. Da abubuwan da suka faru na daga harkar siyasa, tattalin arziqi da zamantakewar mutanen Nijeriya. Sun yi qoqarin fito da surar Nijeriya, ta hanyar bayyana tarihinta da yadda aka gudanar da duk wani sha'ani na siyasa don tafiyar da ita.

Crowder (1962) ya kawo tarihin Nijeriya, ya nuna yadda ta samu. Kuma tana xaya daga cikin qasashe masu yawan mutane a Afirka. Ya nuna Nijeriya ta samu bayan an samu damar haxa yankin Arewa da Kudancinta a shekarar 1914. Wanda Sir Frederick Lugard ya yi. Daga baya matarsa Flora Shaw ta ba da shawara a cikin mujallar *The Times* a raxa wa qasar sunan Nigeria. Ya yi maganar gwagwarmayar neman 'yanci, da yadda aka gudanar da zavuvvuka na jam'iyyin NPC da NCNC, da irin nasarorin da suka samu. Da sauran abubuwan da suka faru a siyasar Nijeriya.

Kirk-Greene da Rimmer (1981) sun yi maganar yadda Nijeriya ta samu kanta a Jumhuriya ta biyu. Sun tavo lokacin mulkin Gowon 1970-5. Sun yi maganar yaqin Biafra da aka yi har tsawon shekaru huxu. Sun yi maganar lokacin mulkin Murtala Muhammad daga 1975-6. Sai lokacin Obasanjo daga 1976-9. Sun nuna yadda aka sake kaxa kugen siyasa, da kakkafa jam'iyyu da aka yi irin su NPN da UPN da sauransu. Sun yi maganar tattalin arziqin Nijeriya tun daga 1970. Suka nuna cewa noma shi ne ginshiqin hanyar neman arziqi ta 'yan Nijeriya, da yadda aka yi amfani da arziqin noma, aka farfaxo da wasu muhimman abubuwa.

Su Falola (1991) sun tattauna muhimman abubuwa da suka faru a siyasar Nijeriya, tun daga zuwan Turawa Nijeriya, da suka kafa mulkinsu  a 1900-1914. Sun bayyana cewa Nijeriya ta faxa cikin mulkin mallaka a 1900. A wannan lokaci, Turawan sun yi amfani da qarfin tuwo don ganin sun mallaki Nijeriya da abin da ke cikinta. Sun yi amfani da wasu hanyoyi don cimma buri. Sun ayyana cewa kafin haka, Turawa sun fuskanci matsaloli, ma'ana sun samu tirjiya daga wajen sarakuna da mutane, inda suka nuna rashin amincewarsu ga Turawan. Sun kuma samu qarancin kuxi na tafiyar da harkokinsu, saboda yanayin arziqin na Nijeriya a lokacin bai inganta ba. Turawan sun samu tirjiya musamman a Arewacin Nijeriya. Sun yi maganar tasirin da 'yan mallakar suka samu ta fuskar siyasa. Sai tasirin da suka samu a vangaren tattalin arziqi da sauransu. Sun bayyana qoqarin wasu 'yan Nijeriya masu kishin kai da suka yi na gwagwarmayar neman 'yanci. Sun tattauna tarihin Nijeriya a Jumhuriya ta xaya da ta biyu.

Falola da Heaton (2008) a nan ma, sun kawo cikakken tarihin Nijeriya, tun daga farkon kafuwar Nijeriya da mutanenta zuwa farkon qarni na ashirin da xaya. Sun zayyana tarihin Nijeriya da ci gaban da ta samu zuwa yanzu. Sun yi qoqarin rattabo tarihin Nijeriya daki-daki kamar yadda ya wakana, tun daga samun 'yanci, siyasa, yanayin arziqi da sauransu. Dukkan ayyukansu suna da alaqa da wannan, tunda duk sun yi maganar siyasar Nijeriya, tun daga yaqin neman 'yanci da samunsa, da yadda aka kakkafa jam'iyyun siyasa, da irin nasarorin da suka samu. Sun yi maganar yanayin arziqin Nijeriya da yadda aka farfaxo da shi, da sauran abubuwan da suka jivanci siyasa. Anifowose da wasu sun yi maganganu kan harkokin siyasar Nijeriya.

Gusau (2003) da (2008) ya yi maganar waqar baka da hanyoyin nazarin adabin kansa. A (2003) ya kawo tarihin samuwar waqoqin baka na Hausa, inda ya kawo tarihin qasar Hausa da bayyana taswirarta. Ya bayyana tarihin waqar baka, ya nuna sanin asalin yadda aka fara waqar baka a al'ummun duniya yana da kamar wuya da kuma buqatar zuzzurfan nazari. Ya zayyana nau'o'in waqar baka, ya kuma karkasa su gida-gida, kamar waqar yara maza, waqar 'yan mata da sauransu. Ya kawo hanyoyin nazarin waqar baka, kamar salsalar waqa, tarihin makaxi a taqaice. A (2008) kuwa, nazarin adabin Hausa ya yi da na wasu al'ummu. Ya yi nazarin adabin Larabci da Ingilishi. Ya kawo tarihin yadda al'ummar Larabawa suka fara ayyukansu na adabi. Ya nuna sun fara tun lokacin zaman farko na jahiliyya, inda ayyukan adabin sun fi karkata akan waqoqin baka, labaru, bukukuwan al'ada da sauransu. Ya kawo hanyoyin fexe adabin Lababci, da tsohuwa da sabuwar hanyar nazari. Sai ya juya kan Turawa. Ya nuna sun fara sha'awar nazarin adabi tun a qarni na 16 Miladiyya, har zuwa lokacin da ake ciki. Ya fito da hanyoyin nazarin adabi na zamani. Ya kawo ra'ayin Dorson (1972) na hanyoyin nazarin adabi. Ya zayyana tarihin ginuwar adabin Hausa a zamunna mabanbanta. Ya rattabo lokacin zaman farko na maguzanci, da lokacin Musulunci, da lokacin zuwan Turawa. Ya bayyana hanyoyin nazarin adabin Hausa daga manazarta daban-daban. Ya kawo gudunmuwar Farfesa Xalhatu Muhammad da Farfesa M.K.M Galadanci da Farfesa Xandatti Abdulqadir da Farfesa Ibrahim Mukoshy da Farfesa Ibrahim Yaro Yahaya. Ayyukan nan na Gusau suna da alaqa da wannan aiki. Na (2003) ya taimaka wajen sanin yadda za a yin nazarin waqa, da tunkarar duk wani abu da ya shafi waqa. Na (2008) kuwa, ya agaza wajen sanin adabi, ba ma na Hausa kaxai ba, har da na wasu al'ummu. Da kuma sanin yadda waqa take a wurinsu. Wato, ya taimaka wajen sanin wasu muhimman abubuwa da suka danganci waqa.

Lasswell (1977) da Szanzo (1940) da Speier (1952) da Ofoegbu (1980) duk sun yi magana kan farfaganda a cikin littattafansu. Lasswell (1977) ya yi maganar farfaganda a matsayinta na wata hanya da ake amfani domin cimma burin a sauya tunanin jama'a. Sauye-sauyen kan zo ta fuskoki da dama, tana iya kasancewa a rubuce ko a waqe, ko hoto da sauransu. Ya nuna yadda kalmar ta samu karvuwa ga 'yan Roman Katolika da suka yi amfani da ita don yaxa aqidojin xariqarsu. Daga baya mazhabar Makisanci ta yi amfani da kalmar. Masu ra'ayin sauyi na amfani da farfaganda su yaxa aqidojinsu

Szanzo (1940) ya tattauna farfaganda sosai, ya kawo nau'o'inta guda biyu. Fara da baqa. Ya nuna cewa farar farfaganda ita ce wadda take a fili, a bayyane, da ke fitowa ma'aikatu da jami'in hulxa da jama'a. Ita kuwa baqar a lulluve take kuma wanda ake yi don shi ba ya gane cewa ana so a samu wani tasiri akan sa ne. Ya kuma nuna cewa waxannan nau'o'in farfaganda da kasafai ake amfani da su a tare ba, kowace na cin gashin kanta. Sau da yawa farar farfaganda na zama malulluvi na baqar farfaganda. Ya zayyana maqasudin farfaganda cewa don a jawo hankali, a samu canje-canje, ko kuma a haxe abubuwa. Speier (1952) ya yi maganar tarihi da ci gaba na bayyana ra'ayoyi da mutane ke yi. Bayyana ra'ayi ya qunshi abubuwa kan qasa ko gwamnati a buxe, a bayyane wanda jama'a ke yi don su nema wa kansu 'yanci. Suna amfani da ra'ayinsu don su samu tasiri kan wani tsari ko aikace-aikacen gwamnati. Neman 'yancin ana yin sa ne domin gwamnati ta bayyana wasu manufofinta ko wasu matakai, don jama'a su san abin da ake ciki, su tofa albarkacin bakinsu, don ci gaban qasa baki xaya.

Ofoegbu (1980) ya tattauna farfaganda, inda ya kawo ma'anarta cewa Brown (1968) ya bayyana farfaganda da wata hanya da ake bi don a samu tasiri da saita tunani, ra'ayi ko manufa ta wani al'amari.

Dukkan ayyukansu na da alaqa ta ququt da wannan aiki, domin sun yi maganar farfaganda, sun bayyana ta sosai. Don haka. Ayyukansu sun taimaka wajen gano yanaye-yanayen farfaganda da sigoginta.

Barista (2011) ya wallafa littafi kan waqoqin Aminu Ladan Abubakar Ala. Ya tatttaro wasu waqoqin Aminu Ala, ya haxa su a wuri xaya suka zama littafi. Wannan littafi yana xauke da wasu waqoqin Aminu Ala guda hamsin da biyar a cikin album goma. Misali akwai album xin *Angara* da *Fulfulde* da *Bubukuwa* da *Mulukiya* da sauransu. Aikin yana da alaqa da wannan domin ya tavo wasu waqoqin da aka yi nazari. Don haka, littafin ya qara haske wajen sanin wasu waqoqin Aminuddeen Ala.

## 2.4 Waqoqin Farfaganda

A zamanin da ake ciki, an yi waqoqi masu gargaxi da faxakarwa kan yanayin yadda ake gudanar da mulki a qasar nan. Waxannan waqoqi, suna magana kan mulki da irin yadda ake cusguna wa

mutanen Nijeriya. Ba a ba su haqqinsu na ‘yan qasa. Ga qasar da ma’adanai, amma ba a amfani da tattalin arziqin yadda ya dace. Irin waxannan waqoqi suna nan danqare a duniyar waqoqi, wasu an yi su a qarqashin inuwar wata jam’iyya, wasu kuwa haka nan aka yi su, don a nuna tsananin rashin jin daxi. Su ne waqoqin farfaganda amma ba wanda aka yi a qarqashin wata jam’iyya ba. Waqoqin su ne:

i. Waqar *Baubawan Burmi* ta Aminu Ala

ii. Waqar *Bubukuwa* ta Aminu Ala

iii. Waqar *Xaurin Gwarmai* ta Amini Ala

iv. Waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* ta Haruna Aliyu Ningi

v. Waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi* ta Haruna Aliyu Ningi

vi. Waqar *Hawaye* Ta Haruna Aliyu Ningi

vii. Waqar *Mafarkin Mulki I* ta Jibrin Muhammad Jalatu

viii. Waqar *Mafarkin Mulki II* ta Jibrin Muhammad Jalatu

ix. Waqar *Ku Yi Haquri* ta Jibrin Muhammad Jalatu

x. Waqar *Rigar ‘Yanci* ta AbdulAziz Abdullahi Ningi

xi. Waqar *Almajiri* ta Muhammad Sani Aliyu

## 2.5 Samuwar Waqoqin Fiyano na Hausa

Waqoqin Fiyano na Hausa su ne waqoqin da suka samu bayan Hausawa sun haxu da baqin al’ummu irin Larabawa da Turawa. Suka samu wasu nau’in kayan kixa daga wajen su musamman Turawa. Daga haka aka dinga yin waqoqin Hausa ana gwama su da kayan kixa na zamani irin su fiyano da jita. Savanin kayan kixa na gargajiya. Waqoqin fiyano na Hausa su ne waqoqin da ake aiwatarwa da kayan kixa na zamani, wanda suka samu sanadiyyar zuwan

Turawa qasar Hausa. Wato dai a ce tasirin baqin al'umma ya haifar da samuwar waqoqin fiyano na Hausa. Binta (2011:77) ta bayyana cewa "Shigowar kixan fiyano zuwa ga Hausawa yana da dangantaka da sha'awar kallo da sauraron kaxe-kaxen finafinan Indiya da Hausawa suka tsinci kansu a ciki. Domin kuwa waxannan finafinai na Indiya su ne suka zamanto fitilu masu haske ga yawancin masu shirya finafinan Hausa. Qoqarin kwaikwayon kaxe-kaxen waxannan finafinai ne ya sa Hausawa suka dinga amfani da kixan fiyano suna rera waqoqin Hausa suna sakawa a cikin finafinai da ake kira na Hausa. Ado Ahmad Gidan Dabino ya fito da fim xinsa mai suna *In Da So Da Qauna*, wanda aka yi kixan fiyano na farko a fim". Waqoqin fiyano na Hausa su ne waqoqin da suka samu canje-canje daga kayan kixa na gargajiya zuwa kayan kixa na zamani kamar fiyano da jita da sauransu.

Gusau (2011: 8) ya nuna cewa "Daga bisani, bayan Hausawa sun iya karatu da rubutu na ajami da kuma na boko, sai aka samu wasu mutane suna rubuta waqoqi, amma sai su xora musu rauji na karin murya, sa'an nan su rera su tare da amon kixa (sauti na kixa)…Har wayau, kayan kixan da ake amfani da su wajen rera waxannan waqoqi sun qunshi kayan kixa na zamani ne kamar mandiri da fiyano da jita da gangunan Turawa da makamantansu".

Samuwar waqoqin fiyano na Hausa ya kawo wani sabon al'amari ga manazarta waqoqin Hausa. Hakan kuwa ya faru ta yadda waqoqin suka zo da wata siga. Ga su kamar rubutattun waqoqi, amma sun yi kama da waqoqin baka. Har a kan jinjina kafin a iya rarrabewa tsakanin waqoqin na baka ko rubutattu. Wanda ya zama wani qalubale ga manazarta waqoqin Hausa. Domin kowa da

yadda yake kallonsu. Wasu na yi masu kallon waqoqin baka, wasu na cewa rubutattun waqoqi ne. Wasu kuwa sun kira su da waqoqin zamani.

Waqoqin fiyano na Hausa sun samu karvuwa sosai da sosai wajen mutane don waqoqin kullum sai qara bazuwa da karvuwa suke yi. Kuma suna samun masu saurare musamman matasa maza da mata. Haka kuma, kullum manazarta suna saurarensu, suna aiki a kansu. Yaxuwar waxannan waqoqi na fiyano ta nuna cewa sun samu karvuwa, kuma sun yi tasiri. Saboda duk abin da ba ka da sha'awa a kansa, ba za ka mayar da hankali akai ba. Don haka, yawan jin su a ko'ina, a wayoyin hannu, da motoci, da kantuna, da gidajen rediyo na gida da na waje ya nuna cewa sun samu karvuwa. Daxin daxawa, waqoqin a kullum qara yawaita suke yi, mawaqan na ta qara samun basirar rera waqoqin. Har ta kai sukan yi irin waxannan waqoqi a qungiyance.

### 2.5.1 Kixan Fiyano

Asalin kalmar fiyano ta Ingilishi ce *piano*, Hausawa suka aro zuwa harshensu, suka Hausantar da ita *fiyano*. *Pianoforte* shi ne cikakken sunan yanka na fiyano tun lokacin da aka qirqire ta a qarni na sha tara a qasar Italy. Ita ce nau'in fiyano na farko da aka fara samu. Mawaqi mai amfani da fiyano ana kiransa *pianist*. Akwai wasu abubuwa da suka haxu, suka tayar da fiyano kamar *strings* da *keys* da *pedal* da *pianostool*. Daga cikin nau'o'in fiyano akwai *grand piano* da *upright piano*. *Grand piano* ita ce wadda take da madannai guda tamanin da takwas (88). Hamsin da biyar (55) farare, baqaqe talatin da shidda (36). Ana latsa madannan tsawon inci 3/8 (9.6 mm). Ita *upright piano* tana da wasu vangarori na *grand piano,* sai dai akwai 'yan bambance bambance tsarinsu. (Enclyclopedia Americana da Concise English Dictionary).

Fiyano abin kixa ne da ake amfani da madannai fari da baqi (keyboard) wadda ke girke a kan tebur don samar da sautin kixa. Fiyano wata na'ura ce wadda ake amfani da madannai (keyboard) fari da baqi. Kowane yana aiki kuma da irin sautin kixa da yake bayarwa ko kixan da ake buqata. Fiyano tana amfani da wutar lantarki da kuma batir. Tana daga cikin sanannun kayan kixa na duniya. Gusau (2008:6) ya bayyana cewa "Fiyano wani abin kixa ne baqo ga Hausawa da suka samu ta hanyar hulxa ta Turawa". Gusau (2008:347) ya ayyana "Fiyano wata ala ce ta yin kixa wadda Hausawa suka samu daga Turawa. Sun sami wannan ala bayan yaqin basasar Nijeriya wajejen shekarun 1970 lokacin da wasu qabilun Kudancin Nijeriya suka fantsamo cikin Arewa. Fiyano abu ce wadda ake kaxawa ta bayar da amo nau'i-nau'i, mai diri ko mai zaqi ko mai kauri gwargwadon yadda ake buqata. Turawa sukan gwama masa jita da tasoshi da ganguna a lokacin kaxa shi. Fiyano abin kixa ne na Turawa wanda suke haxa shi da jita da wasu tasoshi da nau'o'in amo na jita da ganguna da kayan bushe-bushe da buge-buge da sauransu". Fiyano abin kixa ne mai girma wanda ake da madannai fari da baqi a jere. Ana buga fiyano a zauna a gabanta, sannan a latsa madannan.

Binta (2011:76) ya bayar da tata gudunmuwar cewa "Fiyano wata na'ura ce mai amfani da wutar lantarki wadda take bayar da amo na kixa iri daban-daban. Mutum xaya yana iya amfani da fiyano ya yi waqa kuma qungiyar makaxa ma suna yin amfani da fiyano domin rera waqoqinsu. Haka nan Kiristoci suna yin kixan fiyano a coci".

Akwai kixa kala-kala a har dubu bakwai da xari biyar (7,500) a cikin fiyano. Lokacin da Hausawa suka sami wannan abin kixa, sai suka cusa masa amon kixa na gargajiya kamar molo,

da ganga, da kotso, da shantu, da tafi, da busa, da kaca-kaura, da duma da sauransu. Fiyano yana da amon kixan zamani da na gargajiya. Ana xaukar fiyano a yi kixa da ita nan take (live performance). Fiyano koyon shi ake yi, sai a hankali ake fahimtarsa.

An ci gaba da amfani da fiyano ana aiwatar da waqoqin Hausa. Daga baya an samu kixan komfuta wanda ita ma tana da nata kaxe-kaxen. Kodayake asalin kaxe-kaxen nata daga fiyano ne. Ma'ana daga fiyano ake turawa a cikin komfuta. Ana tattara kixan fiyano a mayar da shi a komfuta. Ana amfani da waya (midi cable) wajen haxa fiyano da komfuta. Komfuta tana da abin da ake kira (softwares) kamar *Sonar*. Daga cikinsa ne ake qirqirar duk wani kixa. Akwai abin tace murya (cool edit) da (sound edit) a cikinsa.

### 2.5.2 Asalin Kixan Fiyano

A shekarar 1709, Bartolommeo Cristofori ya qirqiri wani abin kixa da ake kira *gravicembalo col piona e forte*. Wanda yake samar da sautin *piano* (soft) da forte (loud). Daga haka aka samu sunan *pianoforte* ko *fortepiano*. Daga haka aka gajerce sunan zuwa *piano*. (Encyclopedia Americana). Binta (2011:76) ta bayyana cewa " Ana jin mutumin da ya fara qirqiro fiyano, shi ne Bartolemo Cristofori xan qasar Italiya. Mawaqi kuma qwararre a kan sanin kayan kixa wanda kuma iyalan Medici suka riqe shi. Amma zuwa qarshen 1700, kixa da fiyano ya zamo abin zavi ga masu haxa kixa da kuma su kansu mawaqan.

### 2.5.3 Nau'in Kixan Fiyano

Kixan fiyano ya kasu kashi-kashi dangane da yanayin kixa. Akwai:

i. Raps ko Rapping

ii. Hip Hop

iii. Reggae

#### 2.5.3.1. Rap ko Rapping

Asalin kalmar *Raps* tana nufin "karatu da sauri ko magana da sauri". (Rapping-Wikipedia, the free Encyclopedia). *Raps* wani salon waqa ne wanda ake jin sautin magana a waqa a cikin sauri. Ana cikin waqa sai a ji salon *raps* ya shigo. Akwai kuma waqa da akan yi da salon *raps*. Akwai shahararrun mawaqan *raps* na Hausa akwai '2Drops' da 'Kboys' da 'Billy O.' da sauransu. Billy O. ya yi wata waqa mai suna *Koma Bayana* da *Raining Season* da salon *raps*.

#### 2.5.3.3 Reggae

*Reggae* wani salon kixa ne da aka fara samunsa a qasar Jamaica a shekarar 1960. Wani lokaci *Reggae* na xaukar ma'anar wani nau'in rawa da kixa na mutanen Jamaica. *Reggae* wani nau'in kixa ne da aka samu daga wasu tsofaffin nau'o'in kixa kamar *Ska* da *Rocksteady*. Kixan *Reggae* ya fi sauri a kan *Rocksteady* amma kuma ya fi kixan *Ska* tsauri. Asalin kalmar ta fara bayyana a cikin qamusun Ingilishi na Jamaica a shekarar 1967. (Reggae- Wikipedia, the free Encyclopedia). Waqar *Reggae* salonta yana fitar da damuwa a zuciya. Duk waqa da aka yi da wannan salo tana abin da ake kira *code*, wani nau'in kixa daban. Akwai wasu daga cikin mawaqa

masu amfani da fiyano da suka amfani da salon reggae suna rera waqoqinsu, misali akwai waqar *Da Na Sani* ta Rabi'u Dalle da ya rera da irin wannan salo.

### 2.5.3.2 Hip Hop

Wani salon kixa ne wanda ake yin *rap* a cikinsa. Salon waqar *Rap* da na *Hip Hop* suna da kamanci, suna maye gurbin juna a wasu lokuta.

## 2.6 Muhallan da ake Waqoqin Fiyano na Hausa

Muhallan da ake waqoqin Fiyano na Hausa su ne wuraren da mawaqan Hausa masu amfani da fiyano suke rera waqoqinsu. Kamar haka:

- Fina-finan Hausa
- Tarukan Siyasa
- Bukukuwa
- Majalisi
- Tallace-Tallace
- Kafofin Yaxa Labarai

### 2.6.1 Fina-Finan Hausa

Usman da wasu (2008) sun bayyana cewa " 'Yar Aduwa (2007:3) ya ce 'Fim wata hikima ce ta haxa hoto mai motsi da take xauke da mutane, wato hotunansu maza ko mata, yara da manya ko kuma ma wani mutum wanda aka xauka ta yin amfani da na'urar xaukar hoto ta musamman". Yakasai (2007) ya bayyana cewa " Fim na farko da aka fara shiryawa shi ne na *Baban Larai* mai auduga, wanda ya fito a hamshaqin mai kuxi saboda noma auduga da gyaxa. An shirya wasan kwaikwayo na Hausa na bidiyo a shekarar 1970 a lokacin da aka yi fim xin *Shaihu Umar*. Ya qara da cewa bunqasar fina-finan Hausa na bidiyo kuwa ya fara ne daga shekarar 1930 zuwa 1984 a kasuwar fina-finai ta Kano, inda wata qungiyar Kareti da ke unguwar Gyaranya a Kano ta shirya wani wasa."

Binta (2011:70) kuwa cewa ta yi " A 1994 Ado Ahmad Gidan Dabino ya fito da fim xinsa mai suna *In Da So Da Qauna*, wanda aka yi kixan fiyano na farko a fim. Wanda ya yi wannan kixa kuwa shi ne marigayi Nasiru Usman Ishaq Gwale (Adamu 2005:6). Daga nan sai a shekarar 1997 kamfanin Iyan-Tama Multimedia suka shirya fim mai suna *Badaqala* suka yi waqar Hausa tare da kixan fiyano." "Tasirin fina-finai na Indiya da kuma na qasar Sin (China) da kuma fina-finan Amurka da na Turawan Yamma, shi ma ya shimfixa harsashi na samuwar fina-finan Hausa". (Usman, 2008:6). Fina-finan Hausa sun taimaka qwarai wajen yaxa waqoqin fiyano na Hausa. Don ana hasashen cewa fina-finan Hausa su suka kawo bunqasa da yaxuwa da silar samuwar waqoqin fiyano na Hausa. Ma'ana daga gare su ne aka fara samun irin waxannan waqoqi. Daga baya, Hausawa suka yi na'am da baquncin irin waxannan waqoqi. An ci gaba da shirya fina-finai tare da yin amfani waqoqin Hausa na fiyano inda fina-finan suka samu karvuwa ainun saboda

waqoqin da ake tsarmawa a ciki. Hausawa sun ji daxin samuwar waqoqin fina-finai na Hausa sosai saboda sabawa da waqoqin fina-finan Indiya da suka yi. Saboda haka, waqoqin fina-finai da ake yi da fiyano suka samu karvuwa ainun. Haka aka rinqa amfani da waqoqin fiyano a fina-finan Hausa, har wasu waqoqin kan yi fice a ji jama'a na rera su da kansu. Har ta kai ga idan fim babu waqa a cikinsa, bai cika farin jini ba. Akwai mawaqa kamar su Musbahu M. Ahmad da Muddassir Qasim da Fantimoti da Maryam Sangandale da Aminu Mai Dawayya da Yakubu Muhammad da Mahmud Nagudu.

Haka kuma, ba a waqoqin kaxai ake amfani da fiyano ba, masu shirya fina-finan Hausa suna amfani da wasu sautuka na fiyano don inganta fina-finansu. Alal misali suna amfani sautin harbin bindiga, tafi, da take iri-iri duk daga cikin fiyano ake samu.

### 2.6.2 Tarukan Siyasa

Xalibai manazarta sun tofa albarkacin bakinsu kan ma'anar siyasa. Mashi (1986) ya ce siyasa na nufin "Shugabanci ko jagoranci." Sannan ya qara da cewa "Akan kira siyasa da sulhu ko sauqi, domin kasancewar yanayin siyasa na lallava da neman goyon baya. Ko a kira siyasa da cewa yaudara ko qarya, domin irin yadda 'yan siyasa kan tsara wani lamari na yaudara domin neman biyan buqata. Ko cin amana da butulci, wannan shi ne ma ya sanya da zaran an ambaci lamarin siyasa, sai dattawan mutane su zare jikinsu, domin kuwa, kishiyar dattako, ita ce siyasa." Ya qara da cewa akwai "Siyasar jam'iyya mai nufin wata qungiya mai wakiltar wani ra'ayi na neman mulkin al'umma."

Xiso (1997) ya bayyana cewa Ibrahim (1982) ya bayyana ma'anar siyasa a taqaice "Kyautata hanyar rayuwar mutane, koya wa shugabanni yadda za su yi adalci kuma su sanya wa mabiyansu misalan da za su yi koyi da su. Siyasa na nufin amfani da hankali, lafazi mai daxi, ko qoqarin bambanta kanmu da dabbobi dangane da halaye da ayyuka." Sai Xiso (1997) ya ba da nasa ra'ayin ya ce "Siyasa wani tsari ne da ake bi wajen qoqarin sarrafa al'ummar qasa da warware masu matsalolinsu na rayuwa da kuma qoqarin cusa masu waxansu ra'ayoyi."

Gaya (1998) ya ce "Siyasa na nufin jan ra'ayin jama'a ta hanyar lallami domin amincewa ta hanyar jefa quri'a da nufin cimma wata manufa ta musamman ko kuma domin kafa gwamnatin jama'a ta hanyar dimokraxiyya."

Funtua (2003) ya bayyana siyasa da cewa " Kalmar siyasa wadda take Balarabiya ce tana nufin sauqi ko rangwame ko jinqai. Ya ci gaba da cewa a da idan an ce mutum xan siyasa, ana nufin mutum mai jinqai, mai rangwame, mai nasiha, wato mutum mai yayyafi ga rayuwar al'umma."

Akwai dangantaka ta ququt tsakanin waqa da siyasa, domin da wuya a ce za a raba waqa da siyasa. Waqa ta samu karvuwa da farin jina a wajen Bahaushe, Saboda matsayin waqa a wajen Bahaushe, ya sa yake amfani da ita yana isar da manufofi da saqonninsa cikin sauki, don haka ne siyasa da waqa suke tare don isar da manufofin jam'iyya cikin sauqi.

An samu wanzuwar waqoqin Hausa a dalilin zuwan siyasar jam'iyyu, musamman rubutattun waqoqi da aka yi a zamanin siyasar farko da ma wasu daga cikin waqoqin baka. Kodayake masana irinsu Xangambo (2007) suna ganin cewa waqoqin siyasa na Hausa sun fara samuwa tun lokacin jihadin Shehu Xan Fodio. Bayan zuwan Turawa da ilmin zamani, an samu sauye-sauye da canje-canje a  fannoni da dama, inda aka samu siyasar jam'iyya da fara haifar da waqoqin siyasa na baka da rubutattu. Wanda daga baya aka samu cakuxuwar nau'o'in waqoqin wuri xaya a harkar siyasa.

Waqoqin siyasa sun taimaka qwarai wajen havaka da samuwar waqoqin fiyano na Hausa. An samu mawaqa da dama kuma fitattu daga qasashen Hausa musamman Kano da suke yi wa jam'iyya da muqarrabanta waqa ta amfani da fiyano da sauran kayan kixan zamani. Ta haka suka rinqa yin waqoqi na farfaganda ta siyasa suna ankarar da jama'a kan yanayin yadda ake gudanar da mulki a Nijeriya. Wasu daga cikin waxannan waqoqi ana gabatar da su a taron siyasa ko a gidajen rediyo. Mawaqan da ke yin waqoqin siyasa sun haxa Aminu Ala, Haruna Aliyu Ningi, Jibrin Jalatu da sauransu.

### 2.6.3 Bukukuwa

Biki yayan shagali, Bahaushe ya ce "Kowa ya raina ka, ba nasa ba ne". A *Qamusun Hausa* (2006:46) an bayyana cewa biki shi ne " Shagali na nuna farin ciki wajen aure, ko suna, ko naxin sarauta, ko salla, ko al'adun gargajiya". Biki wata al'ada ce da jama'a ke yi a wasu zavavvun lokuta wanda jama'a suke taruwa don yin shagali da nishaxi ta hanyar kaxe-kaxe da bushe-

bushe. Akwai bukukuwa iri-iri wanda mawaqan Hausa masu amfani da fiyano suke aiwatar da waqoqinsu. Daga ciki akwai:

### 2.6.4 Bukukuwan Aure da na Raxin Suna

*Qamusun Hausa* (2006:22) ya bayar da ma'anar aure cewa " Dangantaka tsakanin namiji da mace ta hanyar shari'a". A *Qamusun Hausa* (2006:401) an bayyana cewa suna na nufin " Bikin raxa wa jaririn da aka haifa da abin da za a riqa kiransa". A wajen bikin aure da na suna mawaqan Hausa masu amfani da fiyano, suna taka rawar gani don sukan yi wa amarya da ango waqoqi na musamman wanda za a rinqa kiran sunan amarya da angonta, tare da ambato wasu daga cikin da abokan amarya da na ango. Da kuma wasu dangin amarya da na ango. Haka kuma, sukan yi wasu waqoqin da aka yi a cikin fina-finan Hausa ko waxanda aka yi haka nan don nishaxi. Jama'a za su taru 'yan uwa da abokan arziqi mawaqan na rera waqoqin a gaban jama'a. Wani lokaci sukan zo da fiyano da sauran kayan kixa, su sa waqoqin, su rinqa bin su nan take. A kan yi irin wannan taro a lokaci na musamman. Bikin raxin suna shi ma kamar na aure, mawaqan kan shirya waqoqi don mai jego da angon jego da kuma jariri. A nan ma, a kan yi kara a rinqa ambaton sunayen wasu daga cikin 'yan uwa da abokan arziqi. Misalin mawaqan da ke waqoqin biki sun haxa da: Fati Niger, Fantimoti, Aminu Mai Dawayya, Ali Jita da sauransu.

### 2.6.5 Bukukuwan Addini

Mawaqan Hausa masu amfani da fiyano suna shirya waqoqi a wajen bukukuwan addini kamar bikin Maulud da Maukibi. Kalmar 'Maulud' kalma ce ta Larabci mai nufin 'Wanda aka haifa'. Idan aka ce Maulud ana nufin ranar haihuwa (birthday). A taqaice duk wani abu da za a yi domin haihuwar mutum ana iya kiransa Maulud. Murnar haihuwar Manzon Allah (S) ita ce babbar

murna wadda ta wuce kowace a Musulunci, har ma sauran addinai. Domin zuwansa ya kawo gyara a duniya baki xaya. Asalin Maulud na murnar haihuwar Annabi (S) Allah (T) Ne da Kansa ya fara kuma Ya ce a yi. A wajen taron Mauludi mawaqan Hausa masu amfani da fiyano sukan rera waqoqi domin murnar wannan rana mai daraja. A kan samu masu amfani da mandiri suna yin irin waxannan waqoqi. Kamar Malam Rabi'u Usman Baba da Bashir Xandago da sauransu. Ta haka ne aka samu mawaqan suna amfani da fiyano wajen rera waqoqinsu. Bincike ya nuna cewa Rabi'u Usman Baba shi ne mawaqi na farko da ya fara amfani da fiyano yana waqoqin addinin Musulunci a waqarsa ta *Rabbi Rabbi* . Ga wasu daga cikin waqoqin da aka yi da amfani da fiyano : Mahmud Nagudu waqar *Sayyadil Bashari* da Abubakar Sani waqar *Shugaban Halitta* da Ibrahim Ibrahim waqar *Summa Salatu*. Maukibi wani taro ne ake yi domin nuna murna da haihuwar Shehu AbdulQadir Jailani. Maukibi kamar Maulud ne ana kewaya gari, ana yabo ana farin ciki da nuna murna. Mawaqan suna amfani da fiyano wajen rera waqoqinsu.

### 2.6.6 Majalisi

Majalisi wata kalma ce ta Larabci mai nufin wurin zama kowane iri. Yana iya kasancewa wurin zama na kirki ko akasinsa. Amma Bahaushe yana kallonsa a matsayin zama a tattauna ko a yi wa'azi ko waqoqi ko makamantansu. Majalisi ta wani fanni ana ganinsa kamar ana yin sa ne idan an yi aure ko suna ko wata murna ta samu. Majalisi yana da tasiri mai yawa musamman ga masu yabon Manzo (S) da Alayensa da Sahabbansa baki xaya. Ma fi yawan masu wannan aiki ake kira da *Sha'irai* ko *Shu'ara'u*. Har ma suna da wata qungiya da ake kira *Shu'arul Islam* a qarqashin jagorancin babban shugaba na qasa Sharif Rabi'u Usman Baba, Kano. Majalisi yana da tushe da

asali da Musulunci. Wannan xabi'a ta majalisi ta ci gaba da yaxuwa a cikin harkokin Musulunci har zuwa yau. Ana yin majalisi na yabon Annabi da mandiri ko duffa ko makamantansu. Daga baya aka ci gaba da gabatar da majalisi, sai mawaqan suka fara amfani da fiyano suna aiwatar da waqoqinsu na yabon Annabi. Akwai waqar Malam Kabiru Dogarai ta Sayyidil Wujudi.

### 2.6.7 Tallace-Tallace

Isyaku (2007) ya bayar da ma'anar talla cewa "William F. Arcon da Countland L. Brooke a cikin littafinsu mai suna *Contemporary Advertising* talla hanyar sadarwa ce ga jama'a, amma ba ta hanyar bin su xaya bayan xaya ba. Kuma yawanci a kan biya lada kafin a yi. J.S Chandian da wasu suka ce " Talla na nufin dukkan wani tsararren yunquri da aka yi don gabatar wa jama'a wani ra'ayi ko haja ko aiki ba ta hanyar bin su xaya bayan xaya ba." Talla wata hanya ce da ake bi ana isar da saqo, a bayyana daraja da kimar wani abu da ake son a saya. Masu saye da sayarwa suna tallata hajarsu inda irin waxannan mawaqa masu amfani da fiyano suke yi masu waqoqi don qara xaukaka darajar abin da suke so a saya. Waxannan waqoqi ana yin su a gidajen rediyo inda mawaqa masu amfani da fiyano kan tallata abin sayarwa a waqe cikin zantukan hikima da jan hankali. Misalin mawaqa masu yin talla a gidan rediyo kamar Fati Niger da Ghali DZ Xanhajiya da Musbahu Ahmad.

### 2.6.8 Kafofin Yaxa Labarai

Kafofin yaxa labarai wasu kafofi ne ko hanyoyi na sadar da saqon faxakarwa ko nishaxantarwa ga jama'a. Kafofin yaxa labarai sun qunshi gidajen rediyo da na talabijin da jaridu. Isyaku (2007) ya bayyana cewa " Rediyo na xaya daga cikin manyan kafofin yaxa labarai. Kuma hanyar sadarwa ce da ta fi yawan mutane masu saurare. Kafa ce mai matuqar sauqi wajen isar da saqo.

Talabijin wata na'ura ce mai kama da akwati, mai xauke da wayoyi a cikinta. Wadda ake amfani da su domin rinqa ganin abin da ke wakana. Jarida kafa ce da ake amfani da ita wajen isar da saqo ga jama'a". Waxannan kafofi na watsa labarai suna taimakawa wajen xaukaka mawaqan Hausa masu amfani da fiyano. Da farko suna amfani da waqoqin fiyano wajen nishaxantarwa. Haka kuma sukan gabatar da shiri na musamman ta hanyar gayyato mawaqan da tattaunawa da su kan bin da ya shafe su. Misali a gidan rediyo FM Katsina suna gabatar da wani shiri *Daga Bakin Mai Ita* da suke gayyato mawaqan Hausa na fiyano suna tattaunawa da su. Haka gidan rediyon Freedom na gabatar da wani shiri mai suna *Adabi Madubin Rayuwa*.

### 2.6.9 Mawaqan Hausa Masu Amfani da Fiyano

Kusan a iya cewa da yawa daga cikin mawaqan Hausa babu wanda ba ya amfani da fiyano wajen aiwatar da waqoqinsa. Sukan yi waqoqin a kan mabambantan jigogi don yaxa manufa da saqonni ga jama'a. Wasu waqoqin na da jigon gargaxi, wasu faxakarwa, wasu yabo, wasu soyayya da sauran manufofi kala-kala. Ga wasu daga cikinsu:

i. Aminu Ladan Abubakar (Ala). Gusau (2011:2) ya ce " Wannan suna na Aminuddeen Ladan Abubakar ne aka taqaita cikin haruffa uku na farkon kowane suna [A] da [L] da [A] =ALA + N WAQA= ALAN WAQA. Sunan *Alan Waqa* a tsakanin al'umma, yawanci mutane, tun ma ba matasa ba, sun fi kiran Aminuddeen da shi".

ii. Haruna Aliyu Ningi

iii. Jibrin Muhammad Jalatu

iv. AbdulAziz Abdullahi Ningi

v. Muhammad Sani Aliyu

vi. Sanusi Anu

vii. Bashir Opera

viii. Ali Jita

ix. Musbahu Ahmad

x. Sadi Sidi Sharifai

xi. Rabi'u Dalle

xii. Ibrahim Ibrahim

xiii. Maryam Sangandale

xiv. Zuwaira Isa

xv. Bashir Opera

xvi. Adam A. Zango

xvii. Murja Baba

xviii. Fantimoti

xix. Aminu Mai Dawayya

xx. Maryam A. Baba

xxi. Mamuda Nagudu

xxii. Naziru Ahmad da sauransu.

### 2.6.10 Waqoqin Hausa na Fiyano

Yawancin waqoqin Hausa da ake yi na zamani ana amfani da fiyano a wajen rera su. Ga wasu daga cikin waqoqin:

i. Waqar *Baubawan Burmi*

ii. Waqar *Bubukuwa*

iii. Waqar *Xaurin Gwarmai*

iv. Waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*

v. Waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi*

vi. Waqar *Hawaye*

vii. Waqar *Mafarkin Mulki I*

*viii.* Waqar *Mafarkin Mulki II*

ix. Waqar *Ku Yi Haquri*

x. Waqar *Rigar 'Yanci*

xi. Waqar *Almajiri*

*xii.* Waqar *Garin So*

xiii. Waqar *Dawo Dawo*

xiv. Waqar *Mijina Ne*

xv. Waqar *Da Na Sani*

### 2.6.11 Gudunmuwar Waqoqin Fiyano na Hausa

- Ilmantarwa da faxakar da jama'a

- Qaruwar mawaqan Hausa na zamani

-Bunqasa adabin Hausa

## 2.7 Kammalawa

Wannan babi ya kammala bayan an yi kyakkyawan waiwaye kan ayyukan da suka gabata, ayyukan da masana da manazarta suka gudanar da suka shafi siyasa, farfaganda da kuma waqa masu dangantaka da wannan aiki, tun daga kundayen digiri na xaya da na biyu har na uku, sai muqalu da bugaggun littattafai. Sai dai a waiwayen kamar yadda ya gabata, nazarce-nazarcen da aka yi akan farfaganda, ba su taka kara sun karya ba. Manazarta sun watsar da wannan fage na farfaganda. Farfaganda kuma, ruhi ce ta siyasa. Sannan binciken da aka yi a kan waqoqin fiyano na Hausa su ma ba su wuce cikin cokali ba. Kodayake a kullum ana samun qaruwar irin waxannan waqoqi, watakila nan gaba bincike kansu ya fi na kowane vangare yawa. An ji faruwar waqoqin fiyano a Hausa da muhallai da ake rera waqoqin tare da mawaqan da waqoqin da aka yi da fiyano.

## BABI NA UKU

## HANYOYIN GUDANAR DA BINCIKE

### 3.0 Gabatarwa

Bincike kowane iri, musamman na ilmi ba zai faru haka nan ba, sai da bin wasu hanyoyi domin gudanar da shi da kuma inganta shi. Domin xaukaka darajar ilmi, ya sa ake ziyartar wasu wurare domin tattaro wasu muhimmam abubuwa da za su ciyar da aiki gaba. Wannan bincike an tsara shi domin a yi nazarin farfaganda a cikin waqoqin fiyano na Hausa. A binciko yadda mawaqan nan na farfaganda suka yaxa manufofinsu a zukatan jama'a. Don haka, a wannan babi aka yi bayanin hanyoyin da aka bi don tattaro bayanai da suka danganci wannan aiki. Wasu bayanan an samo su kai tsaye, wasu kuwa sai da aka bi ta wata hanya. Haka kuma, binciken ya kai ziyara duk inda ya dace tun daga xakunan karatu, wasu garuruwan qasar Hausa, sitidiyo, gidan yaxa labarai don binciko abubuwa da suka shafi aikin.

### 3.1 Garuruwan Qasar Hausa da aka Ziyarta don Nemo Bayanai a kan Wannan Aiki

An ziyarci wasu daga cikin garuruwan qasar Hausa, musamman wasu garuruwan da aka fi sani da 'Hausa Bakwai'. "…Qasashen Hausa na asali su ake kira "Hausa Bakwai" watau Daura da Kano da Katsina Da Zazzau da Gobir da Rano da Birom. A yanzu waxannan qasashe sun haxa da dukkanin jihar Kano, da arewacin jihar Sokoto, da arewacin jihar Kaduna da kuma wani vangare na jihar Bauchi, sannan da kudancin Jumhuriyar Niger…" Ibrahim MS (1978:94).

An ziyarci wasu garuruwan qasar Hausa da suke a Arewa maso Yammacin Nijeriya da Kudancinta "…Idan aka raba faxin Nijeriya gida huxu, Arewa ita ke da kaso uku. Arewa ba ta da gava da teku, amma za ta iya shigo ko aikawa da dukkanin kayanta daga qasashen maqwabta. Abin da Arewa take buqata zaman lafiya da haxin kai…" Tofa (2011:5). An ziyarci kasashen Hausa musamman Kano da Sokoto da Kaduna da Bauchi da Katsina da Zamfara don nemo bayanai a kan wannan aiki.

### 3.2 Mawaqa da aka Samo Masu Amfani da Fiyano a Qasar Hausa

Akwai mawaqa masu amfani da fiyano a qasashen Hausa masu tarin yawa musammam a waxannan garuruwa da aka ziyarta da ma waxanda ba a ziyarta ba. A iya cewa akwai kimanin mawaqa masu amfani da fiyano a wasu qasashen Hausa fiye da dubu xaya (1000).

A hira da aka yi da Sanusi Anu a studio xinsa mai suna *Sun An* a garin Katsina a ranar 18/04/2013 ya bayyana cewa akwai sitidiyo da dama a garin katsina, don haka a iya cewa akwai mawaqa masu amfani da fiyano kimanin xari biyu (200).

An tambayi Haruna Aliyu Ningi a ranar 21/04/2013 yawan mawaqa masu amfani da fiyano a garin Bauchi. Ya bayyana cewa " Gaskiya ba zan iya cewa ga adadinsu ba, amma a qungiyance muna da mutum xari xaya da sha takwas (118). Wanda mun yi imani babu wanda bai tava aiki da fiyano ba".

Jibrin Muhammad Jalatu a ranar 22/04/2013 ya bayyana cewa a garin Kaduna suna da fitattun mawaqa sama da ashirin, irin su Adam A. Zango, Kabiru Zango, Umar M. Sherif, Sani Xan Giwa da sauransu. Amma a qiyasce ya ce akwai mawaqa da za su kai guda xari takwas (800).

Shi kuwa Ibrahim Ibrahim da aka yi hira da shi a studio xinsa a Kano mai suna *Kano Musical Studio/ Double Sound* a ranar Talata 23/04/2013 ya nuna cewa abin ya kasu kusan kashi uku. Na farko akwai waxanda suke yin sha'awar waqa da Fiyano, za a zo sitidiyo, a biya kuxi don a yi waqa ta soyayya tsakanin saurayi da budurwa. A nan ba a xauke ta sana'a ba kenan. Na biyu, akwai waxanda suke zaune dindindin a studio. A nan suke zaune, kullum aka zo a nan za a same su. Nan ne wajen sana'arsu, har ma wasu su zauna a qarqashinsu. Na uku kuma, akwai masu zuwa daga qauyuka da jihohi waxanda a wajensu babu sitidiyo, saboda qwarewar 'yan Kano sai nan. Wasu kuma suna da sitidiyo xin, babu qwarewa ta kayan aiki, suna zuwa Kano a yi masu. A kullum ana samun sama da mutum xari (100). Ga masu waqoqin yabon Annabi, da suna amfani da mandiri, amma yanzu sun koma yi da fiyano, ga waqoqin 'yan Islamiyya da sauransu. Akwai mutane sama da dubu goma (10,000) suna amfana da wannan harka ta waqa da fiyano. A sauran jihohi akwai:

i. Zamfara – 100
ii. Sokoto – 150
iii. Jigawa – 100
iv. Kebbi – 100

Masu kixan fiyano sun kasu kashi – kashi dangane da nau'in kixan fiyano, misali akwai:

i. Rap ko Rapping

ii. Hip Hop

iii. Reggae

### 3.3 Maqasudin Zavo Mawaqan da aka yi Amfani da Waqoqinsu

Maqasudin zavo waxannan mawaqa da aka yi amfani da waqoqinsu shi ne:

i. Balaga

ii. Zalaqa

A *Qamusun Hausa* (2006:32:488) an bayyana ma'anar balaga " Ilmin gwanintar Harshe". Zalaqa an bayyana cewa " Kaifin fahimta". Don haka, dalilin zavo mawaqan da aka yi amfani da waqoqinsu a aikin nan shi ne, an dubi fasaha da balaga da kuma zalaqa ta mawaqan. Mawaqan da aka zavo don nazarin waqoqinsu sun shahara a garuruwansu ya hanyar fasaha da balaga ta shirya irin waxannan waqoqi na fiyano, ba a garuruwansu kaxai ba, sun yi fice da zarra a qasar Hausa baki xaya. Misali a garin Kano a iya cewa kowa ya san Aminu Ala bisa hazaqarsa da zalaqa ta shirya waqoqi, ba ma irin waxannan da aka yi nazari kaxai ba, da ma wasu jigogi da dama. Haka kuma, a garin Bauchi kowa ya san Haruna Aliyu Ningi don qwarewarsa da fasaha ta shirya waqoqi musamman na siyasa. Haruna Ningi shahararren mawaqin siyasa ne musamman kan waqarsa ta *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba,* wadda ta sa ya yi fice don tasirin da waqar ta yi na rushe shirin ta zarce.

AbdulAziz Abdullahi Ningi ma ba daga baya ba, shi ma gwani ne wajen shirya waqoqin siyasa ta amfani da hikima da fasaha. Jibrin Muhammad Jalatu ya himmatu wajen shirya waqoqin fiyano. Sananne ne a garin Kaduna don hazaqarsa ta shirya waqoqi.

A garin Katsina a iya cewa an san Muhammad Sani Aliyu don yana da zalaqa ta shirya waqoqi musamman na addini, na yabo ga Manzo SAW. Gwani ne a wajen shirya waqoqin addini.

Ba duka waqoqinsu aka xauko don nazari ba. An yi zaven ne ta yanayin jigo, wato saqon da waqoqin ke xauke da shi. Da yake nazarin ya shafi farfaganda, shi ya sa sai da aka tantance wajen zaven waqoqin, aka fito da masu wannan jigo na farfaganda, wanda ke qoqarin sauya tunanin jama'a da canza masu matsayi zuwa wani daban.

An yi hira da Hajiya Fantimoti a ranar Alhamis 18/04/2013 kan ko tana tava yi waqa mai xauke da wannan saqo. Ta bayyana cewa ba ta tava yin wata waqa mai irin wannan manufa ba. Ta nuna cewa irin waxannan waqoqi na jaruntaka ne, mata kuma an san su da rauni. Don haka, da wuya a samu irin wannan jigo a waqoqin mata. Wannan jigo sai dai a wasu waqoqin maza, mazan ma xaixaiku don ba kowa ne zai iya yi ba. Ta jaddada cewa ita ba ta tava yi ba. Maryam Sangandale a hira da aka yi da ita a ranar Laraba 24/04/2013 a Lafazi Entertainment da yake a bayan gidan Buhari, Habiba House, Zoo road, Kano ta bayyana cewa ita ma ba ta tava yin waqa mai irin wannan jigo ba.

Saboda haka, ba haka nan aka qi zavo mata masu  waqoqin fiyano ba a yi nazarin waqoqinsu a cikin wannan aiki ba. Matan ne ba su  yi waqoqi masu xauke da irin wannan manufa ba. Watakila sai nan gaba za a samu.

### 3.4 Shekarun da aka Aiwatar da Waqoqin

Bincike ya nuna cewa waqoqin nan da ake yi da kayan kixa na zamani, waxanda ake amfani da fiyano da jita wajen aiwatar da su, Hausawa sun same su bayan sun cuxanya da wasu baqin al'ummu kamar Turawa da Larabawa. Kafin wannan cuxanya, Hausawa suna da waqoqinsu na gargajiya. Zuwan Musulunci da zuwan Turawa ya yi matuqar tasiri ga kaxe-kaxen Hausawa. An samu waqoqi da nau'in abin kixa sanadiyar waxannan baqin al'umma a qasar Hausa. Waxannan waqoqi da aka zava, aka yi nazarinsu sun samu ne tsakanin shekarar 2003-2013.

### 3.5 Hanyoyin da aka bi aka Samo Waqoqin

An bi hanyoyi mabambanta wajen samo waqoqin da aka yi nazarinsu. Hanya ta farko ita ce:

An samu wasu waqoqin kai tsaye daga wajen mawaqan da kansu. Kamar Haruna Aliyu Ningi an samu duk waqoqinsa da aka yi nazari daga wajensa. Har ma da waxanda wannan nazari ba zai duba ba. Wato an yi hannu da hannu da shi . Wasu waqoqin an aiko su ta hanyar aikawa da saqo (email) kamar waqar AbdulAziz Abdullahi Ningi. An samu waqarsa kai tsaye daga wajensa ta hanyar email daga nan aka naxa abin aje saqo (flash), sannan aka juya a takarda. Hanya ta biyu

an samu a shagunan sayar da kaset da fai-fai na CD. An kai ziyara wajen sayar da CD na malam Nura da ke qofar Qaura, Katsina. Da CD plaza pompai, Kano.

Waqoqin Aminu Ala da aka yi nazarinsu an same su a shago a fai-fai na CD, sannan aka juya a takarda. Jibrin Jalatu an samun nasa a shago a fai-fai na CD, sannan aka rubuta a takarda. Waqar Muhammad Sani Aliyu ita ma san same ta a shago, a fai-fai na CD, sannan aka juya a takarda.

Duk waqoqin da aka yi nazarinsu an same su a waxanna hanyoyi gida biyu. An same su a fai-fai na CD daga baya aka rubuta a takarda sannan aka buga. Ba a samu waqoqin a rubuce ko a buge ba. An zavo waqoqi guda goma sha xaya aka yi nazarinsu. Uku daga Aminu Ala, uku daga Haruna Aliyu Ningi, uku daga Jibrin Jalatu. Xaya daga AbdulAziz Abdullahi Ningi, xaya daga Muhammad Sani Aliyu. Waqoqin su ne:

- Wakar *Baubawan Burmi* ta Aminu Ala
- Waqar *Xaurin Gwarmai* ta Aminu Ala
- Waqar *Bubukuwa* ta Aminu Ala
- Waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* ta Haruna Aliyu Ningi
-Waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi* ta Haruna Aliyu Ningi
-Waqar *Hawaye* ta Haruna Aliyu Ningi
-Waqar *Rigar 'Yanci* ta AbdulAziz Abdullahi Ningi
-Waqar *Mafarkin Mulki I* ta Jibrin Muhammad Jalatu
-Waqar *Mafarkin Mulki II* ta Jibrin Muhammad Jalatu
- Waqar *Ku Yi Haquri* ta Jibrin Muhammad Jalatu
- Waqar *Almajiri* ta Muhammad Sani Aliyu

Mawaqan da aka zavi waqoqinsu uku-uku, kusan a iya cewa sun fi shahara ta fuskar zalaqa, balaga da gogayya a fagen shiryawa da iya waqa. Kuma sun fi xaukaka da shahara a qasashen Hausa. Haka kuma, waqoqin da aka zava sun samu karvuwa a qasar Hausa, duk da dai ba don daxin waqoqin aka zave su ba, an yi zavin ne ta dubin irin saqo da manufofin waqoqin. Waqoqin an kira su da waqoqin farfaganda, kuma farfagandar suke yi, don haka ba kowace waqa take da irin wannan manufa ba. Shi ya sa aka zavi wasu, ba a zavi wasu ba.

### 3.5.1 Ziyartar Sitidiyo

Domin inganta wannan bincike, an ziyarci sitidiyo da dama don ganin yadda da inda mawaqan ke aiwatar da waqoqinsu. Gusau (2008) ya bayyana cewa “Sitidiyo wani xaki ne da aka shirya don samar da sauti inda a kan ajiye fiyano da jita da tasoshin kixa da ganguna kuma an rufe shi ruf, ba a barin wata kafa da iska za ta shiga. To, idan aka shiga xakin aka yi kixa, amon kixan zai fita sosai kuma raxau yadda ake buqata”. Sitidiyo wuri ne da mawaqa ke amfani da shi, suna ajiye kayan kixa don rera waqoqinsu. A nan ake ajiye fiyano da sauran kayan kixa. A ciki ne ake shiga a rera waqoqi. Daga nan sai a sarrafa waqoqin, a yi ‘yan gyare-gyare na musamman. Sai a mayar da waqoqin zuwa faifai na CD zuwa album. Gusau (2011:2) ya ce “ Album wani mazubi ne da ake iya xura wa waqoqi kama daga xaya har zuwa takwas ko ma fiye gwargwadon tsayi da yawan waqoqin”. A cikin sitidiyo na gani da idona yadda ake shiryawa da rera waqoqin fiyano na Hausa da kuma yadda ake amfani da fiyano don samar da sautin kixa da kuma ire-iren sautin da fiyano ke bayar wa na zamani da na gargajiya.

An kai ziyara a wasu sitidiyoyi musamman na a jihar Kano da Katsina da Bauchi da Kaduna kamar haka:

i. Kano musical studio, shy plaza, qofar Gadon qaya, Kano.
ii. Barewa multi media, shy plaza, qofar Gadon qaya, Kano.
iii. Mazeeqa sound studio, shy plaza, qofar Gadon qaya, Kano.
iv. Nasibi musical studio, shy plaza, qofar Gadon qaya, Kano.
v. Royal Studio, shy plaza, qafar Gadon qaya, Kano.
vi. Taskar Ala global Limited, Farm centre, Kano.
vii. Lafazi Entertainment, Habiba house, Zoo road, Kano.
viii. Walwala musical studio, Habiba house, Zoo road, Kano.
ix. Nagarta musical studio, Habiba house, Zoo road, Kano.
x. Kastiq media production, Habiba house, Zoo road, Kano.
xi. Hikima multi media, Zoo road, Kano.
xii. Sun An studio, layout Katsina.
xiii. Baushe media, Bauchi.
xiv. Aska media, Bauchi.
xv. Shukura media, Bauchi.
xvi. Prince Zango sound studio, Kaduna.
xvii. M.D.C studio, Kaduna.
xviii. L. Sharif studio, Kaduna.

Dukkan waxannan sitidiyoyi da aka zayyana a sama suna amfani da fiyano wajen aiwatar da waqoqinsu.

### 3.5.2 Gidajen Yaxa Labarai

An kai ziyara a wasu gidan rediyo don samo bayanai da suka danganci wannan aiki. Ziyartar gidan rediyo ya yi fa'ida sosai, domin ta kafar yaxa labarai ana samun muhimman abubuwa da suka shafi waqoqin fiyano. Don a kan ware wa mawaqan rana da lokaci don tattaunawa da su. Saboda haka, wasu waqoqin a gidajen rediyo ake jin su, har suka samu karvuwa wajen jama'a. An kai ziyara a gidan rediyo na jiha da masu zaman kansu. Kamar gidan rediyon Companion FM da ke Katsina da gidan rediyon jihar Katsina, da gidan rediyon Freedom, Kano da Nagarta rediyo da ke Kaduna. A gidan rediyon FM na Katsina ana gabatar da wani shiri mai suna *Daga Bakin Mai Ita*. A gina rediyon Freedom ana gabatar da wani shiri mai suna *Adabi Madubin Rayuwa* suna gabatar da shirye-shiryen ne kan mawaqan fiyano na Hausa.

### 3.5.3 Mutanen da aka yi Hira da Su

An yi hira da mawaqan da suka yi waxannan waqoqi don qara jin ta bakinsu kan bayanin salsalar waqoqin tare da taqaitaccen tarihin rayuwarsu. An yi da hira da wasu mawaqa a kan yawan mawaqa masu amfani da fiyano. Da hira da wasu masana kan matsayin waqoqin Hausa na fiyano a yanzu. Da sauran abubuwa da suka danganci wannan aiki. Hira da:

- Aminu Ladan Abuba
- kar ALA a ranar Juma'a 13/07/2012
- Jibrin Muhammad Jalatu a ranar Laraba 17/10/2012
- Haruna Aliyu Ningi a ranar Lahadi 15/07/2012 da ranar Juma'a 28/09/2012 da ranar Lahadi 21/04/2013
- AbdulAziz Abdullahi Ningi a ranar Alhamis 19/07/2012
- Muhammad Sani Aliyu a ranar Juma'a 28/09/2012

- Hajiya Fantimoti a ranar Alhamis 18/04/2013
- Sanusi Anu a ranar Alhamis 18/04/2013
- Farfesa Abdulqadir Xangambo a ranar Talata 23/04/2013
- Ibrahim Ibrahim a ranar Talata 23/04/2013
- Rabi'u Dalle a ranar Laraba 24/04/2013
- Maryam Sangandale a ranar Laraba 24/04/2013

### 3.5.4 Xakunan Karatu da aka Ziyarta

Domin kyautatawa da kuma inganta wannan bincike, an ziyarci xakunan karatu da dama don ganin an yi nasara. An ziyarci xakunan karatu na jami'o'i daban daban kamar xakin karatu na Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya da Kimiyya, Jami'ar Bayero, Kano. Da xakin karatu na Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Xanfodio, Sokoto. Da xakin karatu na sashen Harsunan Nijeriya Da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria. Da xakin karatu na Mumbayya, gidan malam Aminu Kano. Da xakin karatu na Sashen Hausa da ke Kwalejin Gwamnatin Tarayya da ke Katsina. Inda aka duba kundayen digiri waxanda da suka yi magana kan waqoqin fiyano na Hausa da waqoqin siyasa. Sai dai kundayen da suka yi magana kan waqoqin fiyano na Hausa, ba su taka kara sun karya ba. Kuma an gano cewa wasu kundayen sun yi nazarin waqoqin jam'iyyun siyasa ne dangane da Jumhuriya musamman a matakin digiri na biyu. Inda wasu ke qoqarin fito da gudummuwar waqoqin siyasa wajen kafa dimokraxiyya da sauran makamantan haka.

An duba muqalu da aka rubuta wanda suka tattauna wani abu a kan waqoqin siyasa. An lura cewa wasu muqalolin sun yi tsokaci kan matsayin waqoqin wajen yaqin neman zave, inda wasu kan xauki tsofaffin ‘yan siyasa su yi nazarin ayyukansu, wasu kuwa tsofaffin jam’iyyun siyasa suke nazari da sauran ire-iren haka. An duba kundayen *Encyclopeadia na Americana da Britannica da Book of knowledge* musamman wajen yaqin neman ma’anar farfaganda da tarihinta. An yi amfani da yanar gizo-gizo wajen binciko abubuwa da suka shafi farfaganda. An yi amfani da qamus qamus don binciko tantagaryar ma’anar farfaganda. An yi amfani da bugaggun littattafai.

### 3.6 Muhawarar Masana Dangane da Matsayin Waqoqin Hausa a Yanzu da Ra’in da aka Xora Bincike a Kai

Manazarta da masharhanta waqoqin Hausa suna ta tattauna matsayin waxannan nau’in waqoqi na fiyano na Hausa, abin da manazarta suka fi yi shi ne, hasashi- faxi dangane da matsayin waqoqin. Ma’ana kowa na faxin albarkacin bakinsa. Kafin zuwan wannan lokaci, masana da manazarta waqoqin Hausa, ba su bar mu haka nan ba. Sun yi bincike kan waqar baka da rubutatta, haka kuma, sun yi qoqarin bambance su dangane da sigoginsu. Daga cikin ire-iren waxannan bincike, akwai wanda Muhammad (1977) ya kawo bambancin waqar baka da rubutatta, in da faxa cewa, waqar baka ba ta da amsa-amo, akwai amfani da kayan kixa kuma da baki ake aiwatar da ita kuma a kan yi ta don kuxi. Ita kuwa rubutattar waqa ba ta da waxannan siffofi.

Haka kuma Muhammad (1978) Malamin ya fito da wani ilmi mai amfani, inda ya qara bambancewa tsakanin nau'o'in waqoqin, ya gano cewa akwai amsa-amo iri biyu a waqa Bahaushiya, da amsa-amon harafi da amsa-amon kari. Bayan amsa-amon harafi, wanda ake samunsa a rubutattar waqa amma a waqar baka babu. Ya gano cewa akwai amsa-amon kari wanda ake samun sa a dukkan nau'o'in waqoqin biyu. Ya qara kawo misali daga wasu rubutattun waqoqi wanda ba su da amsa-amon harafi amma suna da amsa-amon kari, su ne irinsu waqar *Gangar Wa'azu* da waqar *'Yargagara* ta Aqilu Aliyu.

Har wayau, Muhammad (1979) Ya qara qwanqwancewa tsakanin waqar baka da rubutatta. Ya nuna inda suka yi tarayya, da inda suka bambanta, ya kuma fito da tasirin da kowace waqa take da shi a kan 'yar uwarta.

Muhammad (1981) a wannan karon ya daxa fayyace mana bambanci tsakanin waqar baka da rubutatta. Ya nuna inda nau'in waqoqin suka yi tarayya cewa kasancewarsu duk waqoqi ne, qwaqwalwa ko zuciya ita ce asalinsu, magana ce ta fasaha mai rauji wadda ake rerawa. Ta vangaren bambancinsu, ya nuna cewa waqar baka ta riga rubutatta samuwa a qasar Hausa. Ya kawo bambancin ta fuskar tsarawa, da jigo, da salon tsari da sauransu. Ya kawo misali daga waqoqin *Magana Jari Ce,* ya nuna cewa kamar yadda suke a rubuce a littafin, amma ba su da siffar rubutattar waqa. Wato sun fi kama da waqar baka. Malamin ya kawo hujjoji ta fuskar tsari, jigo da karin waqoqin.

Furniss (1995 da 1996) Duk ya qara jaddada ra'ayin Muhammad da Greenberge (1949) kan yadda suka rarrabe tsakanin waqar baka da rubutatta. Amin (2008) ya yi maganar rubutattun waqoqin Hausa da kuma nuna tasirin zamani tattare da su, har ya yi tsokaci kan ra'ayin Muhammad (1979) da ya kawo siffofin waqa rubutatta, amma an samu waqoqi na yanzu masu kama da rubutattun waqoqi, amma ana haxa su da kayan kixa kamar jita da fiyano, da kuma haxuwar mawaqa maza da mata. Ya daxa nuna cewa, waqoqin na yanzu suna da tsarin baiti da amsa-amo. Amma kash! Amin (2008) bai bayyana ra'ayinsa ba dangane da matsayin waqoqin, sai dai kawai ya nuna cewa an samu 'yan canje-canje.

Hausawa sun ci gaba da nazarce-nazarce da rubuce-rubuce kan waqar baka da rubutatta. A wannan qarni da muke ciki, an samu sauyi da canje-canje a duniyar waqa. An riqa cakuxa nau'o'in waqoqin nan biyu a wuri xaya ana amfani da kayan kixa na zamani kamar su fiyano da jita wajen aiwatar da waqoqin, har da wuya a iya tantance wa na baka ne ko rubutattu. Duk da haka, an samu wani aiki da Gusau (2008) ya bayyana samuwar irin waxannan waqoqi na zamani inda ya ce "…Abin kixa na fiyano sabon abu ne a wajen Hausawa kuma sun same shi ne a sakamakon cuxanya da Turawa. Fiyano abin kixa ne na Turawa wanda suke haxa shi da jita da wasu tasoshi da ganguna su dinga yin kixa".

"A qasar Hausa an sami wasu mutane waxanda suka dinga amfani da kayan kixa na Turawa suna yin waqoqin Hausa. Makaxa Bala Miller yana daga cikin mutane na farko da suka fara wannan al'amari…A tsakanin shekara ta 1982 zuwa 1984 kuma aka sami mawaqiya Fumi Adams ta yi wasu waqoqin Hausa ta amfani da kayan kixan Turawa da suka haxa da jita da

fiyano da tasoshi da kuma ganguna. Haka kuma an sami wasu makaxa da suka biyo sahun waxannan da suka gabata kamar Sa'adu Bori da Garba Gashuwa. A shekara ta 1990 an sami wani wanda ake kira Nasiru Ustaz wanda ya fara yin kixa da fiyano a Gidan Xan Hausa, Kano, yana kaxa take daban-daban na gargajiyar Hausawa. Ya kuma yi wannan kixa ne a matsayi na sha'awa. Nasiru Ustaz ne ya koya wa Muntari Kwanzuma da Ali Baba Yakasai da sauransu kixan fiyano….A hankali a hankali, wannan nau'in kixa na fiyano ya dinga sace zukatan matasa, yana kuma daxa jan hankalin mutane sosai.

A shekarar 1998, Kamfanin Iyantama Multi Media ya fara yin kixa na fiyano yana gwama shi da waqoqin soyayya da na amarya da ango da sauransu…. Aka dinga gwama waqoqin Hausa da kixan fiyano ana jefa su a cikin fina-finan Hausa. Zuwa shekara ta (2000) jama'a ta fara sabawa da waxannan kaxe-kaxe na fiyano da ake tsarmawa a cikin finafinai. Kixan fiyano ya sami karvuwa ainun a wajen matasa, maza da mata, ba lalle sai a cikin fim ba, a kan shirya waqoqin soyayya da yabo da gargaxi da nasiha a rera su ta amfani da kixa na fiyano. Kamar yadda Gusau ya bayyana.

Dangane da matsayin waqoqin Hausa a yanzu. Akwai masu da'awar cewa waqoqin nan na zamani rubutattun waqoqi ne, ba waqoqin baka ba. Domin wai asalin waqoqin a rubuce suke, wato mawaqan suna rubutawa kafin su rera. Masu wannan ra'ayi suna kafa hujja da cewa, wai idan na so a gane darajar abu, to asalinsa ake dubawa, wato dai asalin abu, shi ne abu.

Daxin daxawa, akwai masu da'awar cewa waqoqin zamanin nan dai rubutattu ne, kawai ana sa kixa ne don nishaxi. Masu wannan ra'ayi, suna kafa hujja ta fuskar yadda ake nazarin waqoqin. Suna nuna cewa idan aka rera waqoqin, aka aza su kan mizanin auna waqa, za a tarar cewa suna da tsarin waqa rubutatta ne.

Gusau (2008) a nasa ra'ayin kan matsayin waxannan waqoqi, ya nuna cewa "Dangane da yanaye-yanaye na waxannan waqoqi da wasu daga cikin sigoginsu an lura suna da waxannan abubuwa kamar haka:

- Waqoqi ne waxanda suke hawa karin murya da rauji nasu na kansu daidai da qa'idoji na waqar baka ta Hausa;
- Waqoqi ne waxanda ake yawaita aro tare da kwaikwayon zubi da awon baka na waqoqin makaxan baka na Hausa;
- Waqoqi ne waxanda a kan yi musu ginduna da tsarin rerawa irin na waqoqin baka;
- Waqoqi ne waxanda ake kwaikwayon karuruwa na waqoqi baqi, kamar kare-karen waqoqin Indiya da ire-iren rauji nasu;
- waqoqi ne waxanda ake qoqarin a xora su bisa tsari na layukan rubutattun waqoqin Hausa, amma sai dai yawancinsu idan aka bi karinsu da raujinsu sosai da sosai za a ga sun kauce wa wannan doka, sun koma wa doka ta saxaru a tsarin waqoqin baka.
- Ashe kenan, idan an dubi waxannan waqoqi da aka yi ta gwamawa da kixan fiyano, za a ga yawanci, suna hawa ne bisa tsarin waqoqin baka na Hausa, tun kuwa daga yanayi na rera waqe-waqen gaxa da na wasannin dandali, har zuwa ga yanayi na rera waqoqi na makaxan baka na Hausa bisa kuma rukunoninsu mabanbanta. Haka kuma duk da kasancewar masu yin waqoqin samari ne, maza da mata, waxanda, bisa yawanci, suka iya karatu da rubutu na boko ko na Larabci, yawancin waqoqin nasu ba su hawa qa'idojin rubutattun waqoqi xari bisa xari amma kuma mafi yawa na waqoqin suna bin tsari da dokokin waqoqin baka fitattu".

Har wayau a cikin wasu rubuce-rubucensa Gusau (2011 da 2011) yana jaddada cewa waqoqin Hausa na fiyano, waqoqin baka ne ba rubutattun waqoqi ba. Gusau (2011) ya bayyana cewa:

> Yanayin rerawa da karin murya da gwama su da kixan fiyano ko wani nau'i na abin kixa baqo suka janyo a sanya ire-iren waxannan mawaqa a sahu na makaxan baka na zamani. Hatta ma haxa rubutattun waqoqi da sauti na kixa tare da samar da rauji mai sadarwa al'amari ne baqo a wajen marubuta waqaqin Hausa. Alal-misali, mawaqa Larabawa, tun ma ba mutanen Sudan ba, idan marubuci ya rubuta wata waqa, kuma ba a rera ta da kixa ba, tana nan a matsayin *qasida* ko *shi'ir* ko *nazmu* da sauransu. Amma idan aka rera ta amon kixa (sautin kixa), to, waqar za ta koma ta baka, kuma irin ta ake kira *ugniya* (tilo) ko *agani* (jam'i), kuma mai rera ta a kira shi *al-Muganni* ko *al-Mixrab* wato *makaxi* (Gusau, 2011:6).

Haka kuma a wani rubutunsa Gusau (2011) ya qara bayyana cewa:

> Daga bisani bayan da Hausawa suka iya rubutu da karatu na ajami da kuma boko, sai aka sami wasu mutane suna rubuta waqoqi, amma sai su xora musu rauji na karin murya, sa'an nan su rera su tare da amon kixa (sauti na kixa). To, ire-iren waxannan waqoqi sukan bi sahun waqoqin baka ne domin rauji da rerawa da kixa sun mayar da su bisa dokokin waqoqin baka. Ta haka ne aka samu wani sabon rukuni na waqoqin baka na zamani. Har wayau, kayan kixa da ake amfani da su a wajen rera waxannan waqoqi sun qunshi kayan kixa na zamani ne kamar mandiri da fiyano da jita da gangunan Turawa da makamantansu. Daga wannan lokaci ne aka sami waqoqin baka na Hausa iri biyu, waqoqin baka na gargajiya wanda ake yin su da kayan kixa na gargajiya da kuma waqoqin baka na zamani waxanda ake rubutawa kuma a rera su da kayan kixa na zamani (Gusau, 2011:8)

A hira da aka yi Farfesa Abdulqadir Xangambo kan matsayin waqoqin. Ya bayyana cewa waxannan waqoqi suna tsakanin rubutattun waqoqi da waqoqin baka. Amma mafi yawa waqoqin baka ne, amma akwai kaxan da za a iya cewa rubutattu ne. A ra'ayinsa akwai nau'in waqa uku yanzu a Hausa.

i. Waqoqin baka na gargajiya wanda ake amfani da kayan kixa na gargajiya.

ii. Rubutattun waqoqi wanda ake rubutawa a takarda.

iii. Waqoqin zamani na fina-finai.

Ya qara bayyana cewa akwai wani shiri da suke gabatarwa a gidan rediyon *Freedom* inda suke gayyato mawaqa suna jin ta bakinsu dangane da matsayin waxannan waqoqi cewa rubutattu ne ko kuwa na baka ne. Wasu mawaqan na da ra'ayin cewa waqoqin baka suke yi irin su Aminu Ala ya ce waqoqinsa, waqoqin baka ne tunda ba ya bin qa'idojin rubutattun waqoqi kai tsaye. Wasu kuma suna nuna cewa waqoqinsu rubutattu ne irin su Sha-Bege. Mamuda Nagudu ya nuna cewa ya san qa'idojin rubutattun waqoqi don ya iya aruli, a iya cewa watakila shi ma nasa rubutattu xin ne.

Daxin daxawa, Farfesa Abdulqadir Xangambo ya nuna cewa kafin waqa ta zama rubutatta, sai tana da wasu siffofi kamar haka. Sai waqa na da aruli, shi aruli muhimmi ne a waqa rubutatta. Ana iya cewa shi ne ruhin waqa rubutatta. Rerawa ita ce ruhin waqar baka. Qafiya (amsa-amo), a nan an fi damuwa da babban amsa-amo don ana iya raxa wa waqa suna da shi. Sai daidaiton yawan layuka, idan ba su daidaitu ba, ya nuna cewa shi ne Farfesa Xandatti Abdulqadir ya kira Taqadarin baiti. Saboda haka, wasu mawaqan sun san qa'idojin rubutattar waqa, wasu kuma ba su sani ba. Ita kuwa waqar baka, idan aka yi ta babu rerawa ta zama zance kara zube in ji Xangambo.

Shi kuwa Farfesa Isa Mukhtar yana da ra'ayin cewa waxannan waqoqi jemagu ne, don suna tsakanin waqoqin baka da rubutattu. Hankaki ne sun bar ta su tafiyar sun kasa ta wasu. Kuma an saki gargajiya ta kixa, an yi sallama da kalangu, da ganga, da jauje, da kotso, da dundufa da

sauransu. Sannan waqoqin ba za su yanku a kan kari na baharin waqa ba. Balle a fitar da illoli da zihafai saboda karin muryar Indiyawa. Don haka, sabon qarni, sabuwar waqa.

i. Qarni na sha tara (Q-19) waqoqin jihadi
ii. Qarni na ashirin (Q-20) waqoqin hululu
iii. Qarni na ashirin da xaya (Q-21) waqoqin fiyano.

### 3.6.1 Matsayin Waqoqin ga Masu yin Su

Aminu Ala ya bayyana cewa waqoqin sun tara kamanceceniya na abubuwa guda biyu. Don suna na zubi da tsari na rubutacciyar waqa, na tsara su kan jigo da warwarar jigo dalla-dalla. Wato suna da wasu daga cikin siffofin rubutacciyar waqa. Ta haka kuma a kan yi wasu abubuwa na daga siffar waqar baka kamar karviya, amfani da kayan kixa da sauransu. Ya nuna cewa waqoqin baka sun fi karvuwa saboda amon kixa da karviya. Amma zubi da tsari na rubutacciyar waqa ya fi shigar da ilmi da fasaha. Shi ne aka samu haxuwar siffofin waqoqin wuri xaya. Ya nuna cewa waqoqin sun fi siffantuwa da waqar baka fiye da rubutacciya. Ya kawo misali da waqar *Baubawan Burmi* ya nuna tana da salo guda biyu amma an fi hukunta ta a cikin waqar baka, don an karya dokar rubutacciyar waqa. Ita rubutacciyar waqar, inda aka aje numfashi, a nan aka tsaya. Ya nuna cewa kixa da sauran siffofin waqar baka sun fi sa daxi da shauqi da nishaxantarwa. Bisa ga abin da ya gabata a iya cewa Aminu Ala ya hukunta waqoqin a matsayin waqoqin baka.

Shi kuwa Jibrin Muhammad Jalatu ya nuna cewa waxannan waqoqi na fiyano sun fi siffantuwa da rubutattun waqoqi, don yadda ake yin komai a qa'idance, kamar amfani da qafiya. Ya bayyana cewa saboda qafiya ana iya saka su a vangaren rubutattu xin.

Dangane da matsayin waqoqin fiyano Hausa, ina tattare da masu ra'ayin cewa waxannan waqoqi rubutattu ne:

i. Asalin waqoqin dai a rubuce suke, haxuwarsu da kayan kixa na zamani, a iya cewa bai isa ya canza masu mafari ba, kowa ya san zamani riga ne.

ii. Idan aka kalle su ta fuskar jigo, nan ma za a iya yanke hukunci, don rubutattun waqoqin Hausa ko na da, a jigonsu ba a cika samun yabo ba, in kuwa an samu na yabo, sai dai yabon Annabi, su ma waqoqin na yanzu haka suke. Amma akasarin waqoqin baka, suna yabo ne musamman ga iyayen gidansu.

iii. Ta fuskar salon tsari ma, waqoqin na zamani sun fi kama da rubutattu. Akwai yabon farawa (Basmalla) da na rufewa (Tamat). Akwai amsa-amo a ire-iren waqoqin. Ana kuma samun babba da qaramin amsa-amo, wani lokaci har uwar-goyon amsa-amo duk ana samu. Ga kuma amsa-amon baiti. Yawancin baitocin suna da tsarin rubutattar waqa, amma a kan samu taqadarin baiti. Wanda mawuyaci ne a same su a waqoqin baka.

iv. Akwai amfani da aron kalmomi daga harshen Turanci ko Larabci. Wanda yake fitacciyar sifa ta rubutattun waqoqi, amma waqoqin baka ba su cika aron kalmomi ba, sai dai amfani da tsofaffin kalmomi ko tsohuwar Hausa.

v. Sannan kuma, kamar yadda aka san waqa rubutatta, yawancin marubutan sukan kawo adireshinsu a qarshen waqa, a waqoqin yau xin ma, a kan samu masu wannan siffa xin. Da sauran abubuwa makamantan haka.

Bisa abin da ya gabata, ana iya cewa, har yanzu dai waqoqin Hausa na fiyano na zamani, ba a sama masu gurbi ba a farfajiyar waqa. Saboda kowane manazarci da yadda yake kallonsu kuma yakan qoqarin kafa hujja mai qwari daidai fahimta. Ko ma dai yaya, ya rage ga sauran manazarta

masu sha'awar waqa da a dage da nazarce-nazarce na waxannan waqoqi don sa ma masu tsayayyen gurbi a duniyar waqa.

### 3.6.2 Ra'in Bincike

Wannan bincike ya dogara ne a kan ra'in *Isar da saqo* ( Dialogical Theory) don nazarin farfaganda a waqoqin fiyano na Hausa. Shi dai ra'in *Isar da saqo*, ra'i ne wanda wani masanin ra'o'in adabi da tarke na zamani mai suna Mikhail Bakhtin xan qasar Russia ya qirqiro a cikin littafin *Cultural Criticism: A Primer Of Key Concepts* na Arthur Asa Berger (1995). A cikinsa ne Bakhtin ya yi da'awar cewa magana ko rubutu na tattare da wani saqo da ake son a isar ga jama'a. Haka kuma, rubutun nan ko maganar nan suna tattare da manufofin da aka yaxa. Abin da aka faxa ko aka rubuta, saqo ne na musamman ga jama'a da kuma irin sakamakon da za a samu.

*Ra'in Isar da saqo*, ra'i ne da ke nuna cewa idan mutum ya yi magana ko ya yi wani rubutu, a maganar nan ko rubutun nan da ya yi, dole akwai manufa a zuciyarsa. Manufar ta isa ga al'ummar da ake son a isar wa. Dole rubutu ko wani zance da aka yi yana da saqon da yake son isarwa. Akwai abin da ake son a sani ko a fahimta. Ba za a yi rubutu ko wata magana haka nan ba, sai da manufa a zuciya ta son canza xabi'a, halayya, tunani ko wasu aqidoji na mutanen ake son a isar wa da saqon. Magana ko rubutu na da manufar sauya wani al'amari ga jama'a. A kan iya samun sakamakon nan take, ko kuma daga baya. Duk abin da aka faxi, ko aka rubuta ana so a samu canji da tasiri a zukatan jama'a. Wato mai zance ko rubutun nan yana so ya cusa wani ra'ayi a musamman don ya samu tasiri a kan su. Dole ana so wani abu ya faru bayan an isar sa saqon nan. Don haka ne aka zavi wannan ra'i don a xora wannan bincike akai kasancewar

binciken ya shafi farfaganda, farfaganda kuwa ana yin ta ne domin a yaxa wata manufa ko bayani da nufin canza xabi'un mutane don kawo wani sauyi.

Haka kuma farfaganda ta shafi cusa wani ra'ayi na gaskiya ko akasin haka don a samu tasiri ga tunanin jama'a. Duk wani qoqari don yaxa wata manufa ta fuskoki daban-daban. Mawaqan da suka yi waxannan waqoqi, suna da wata manufa da suke da ita a zukatansu zuwa ga jama'a. Don haka, waqoqin nan da aka yi nazarinsu, suna yin farfaganda zuwa mutane, don a samu wani sauyi da canji a yadda ake gudanar da mulki. Saboda haka, farfaganda ita ce manufar mawaqan, don suna zayyana irin abin da ke faruwa a qasa na rashin jin daxi, tun daga yanayin gudanar da mulki, zamantakewa da tattalin arziqi don a yi bore da tawaye ga mulkin Nijeriya. Manufar mawaqan kenan zuwa ga al'umma. Daxin daxawa, ra'in zai dubi yanayin yadda ake tafiyar da mulki da addini da zamantakewa da tattalin arziqi kamar yadda suka bayyana a cikin waqoqin. Za a ga yadda mawaqan suka yi qoqarin amfani da su domin yaxa manufarsu da nufin canza xabi'un jama'a don kira ga bore da tawaye.

### 3.7 Yadda aka Gudanar da Aikin bisa Tsari

An aiwatar da wannan aiki cikin tsari ingantacce, mai qayatarwa. Don haka ne aka kasa aikin zuwa babi guda biyar. A wannan aiki, an yi tsokaci kan waqoqin fiyano na Hausa na farfaganda. Babi na xaya ya qunshi gabatarwa wadda ta naxe aikin gaba xaya, sai manufar bincike. Da dalilin bincike da muhimmancinsa. An yi hashashen bincike da iyakacinsa. Babi na biyu ya shafi waiwaye da bitar ayyukan da suka gabata da ke da alaqa da wannan aiki kama daga kundayen bincike tun daga na digiri na xaya har zuwa na digirgir, ga muqalu da bugaggun littattafai da aka duba don inganci na wannan aiki. An yi maganar samuwaqar waqoqim fiyano na Hausa da kawo ma'anar fiyano da wuraren da ake rera waqoqin fiyano na Hausa. Babi na uku ya qunshi dabaru

da hanyoyin gudanar da bincike, hanyoyin da aka bi, aka samo bayanai da suka shafi wannan aiki. A babi na huxu farfaganda a waqoqin fiyano na Hausa ta bayyyana. A nan kuma aka fito da manyan rassa huxu da waqoqin suka qunsa, wato waqoqin na maganar yanayin yadda ake mulki, addini sai tattalin arziki da zamantakewa. Sannan an yi nazarin waqoqin, inda aka xora su a kan mizanin farfaganda, aka gano cewa ai  suna qarqashin farar farfaganda ne, hakan ya faru ne, saboda yadda waqoqin ke qoqarin tunkarar lamarin kaitsaye, har ma sukan bayyana haka a wasu xiyan baitocinsu. Ga sanin kafar da saqon ke fitowa, ga kuma amfani da qabilanci, da vangarenci, har ma da addini. Kuma haka, ta ba da damar aka fahimci ashe waqoqin na xauke da wani gagarumin saqo da a kan rasa hanyar isarwa sai ta waqa. Don ita waqa, wata hanya ce ta isar da saqo cikin sauqi, ana amfani da ita don a wayar da kan al'umma. A babi na biyar aikin ya kammala don ya qunshi jawabin kammalawa, shawarwari sai manazarta da rataye.

### 3.8 Kammalawa

An kammala wannan babi bayan an kawo bayanai kan hanyoyin da aka bi wajen gudanar da wannan bincike. Kamar yadda aka bayyana an yi hira da mawaqan don jin ta bakinsu musamman kan dalilin rubuta waqoqin, tare da tarihin rayuwarsu a taqaice. Wasu kuma an yi hira da su don jin matsayin waqoqin nasu. An kuma kai ziyara a wasu garuruwan qasar Hausa da sitidiyo don tattaro bayanai masu inganci. An samo bayanai daga xakunan karatu na jami'i'o mabambanta wanda ya haxa da kundayen digiri, muqalu da bugaggun litttattafai. An hau yanar gizo don binciko abubuwa masu muhimmanci. Yayin aiwatar da wannan bincike, an bi wasu hanyoyi mabambanta don taro bayanai da suka ciyar da aikin gaba. Wasu bayanan an same me su kai tsaye, wasu sai da aka bi wasu hannyoyi daban.

# BABI NA HUXU

# FARFAGANDA A WAQOQIN FIYANO NA HAUSA

## 4.0 Gabatarwa

Masu shirya waqa ta baka ce ko rubutatta, mutane ne masu tsananin fasaha da hikima da zalaqa wajen bayyana saqonninsu da manufofinsu ga al'umma baki xaya. Manufofin waqoqin siyasa, musamman irin waxannan da ake yi da kayan kixa na zamani na farfaganda, cike suke da abin daya shafi addini, zamantakewar jama'a, yanayin tattalin arziqin qasa da yadda ake sarrafa shi, da yanayin yadda ake tafiyar da mulkin kansa. Sannan waqoqin na kira da a yi kishin kai, da kuma saurin tunatar da al'umma yadda ya kamata a yi mulkinsu, da yadda ya kamata a tafiyar da duk wani al'amari na siyasa. Waqoqin kuma, na fito da matsalolin da ke tattare da jama'a, da nuna irin shuwagabannin da ya dace a zava. Mawaqan kan yi nazarin abin da ke wakana a harkar mulki, sai su bayyana su a cikin waqoqin, suna masu jawo hankalin jama'a da tsuma su, don su gane inda aka kwana, da inda za a tashi. Savanin waqoqin siyasa na jam'iyya da a kan yi kacokam kan manufofin jam'iyya da muqarrabanta.

Waqoqin nan da ake yi na siyasa, da kayan kixa na zamani, waqoqi ne na farfaganda, domin suna qoqarin zaburar da mutane da ma tunzura su zuwa ga bore da tawaye ga shuwagabannin Nijeriya, matsawar ba za a yi riqo da gaskiya ba. Don haka, waqoqin na qoqarin kira da faxakar da jama'a da cusa masu wani ra'ayi na kaucewa shuwagabanni.

Wannan kira na neman canji da ake yi a cikin waqoqin nan, ya zama dole musamman idan aka lura da lokacin da ake aiwatar da waxannan waqoqi, lokaci ne da mutanen Nijeriya ke neman agaji. Sannan lokaci ne da kan mage ya waye, kowa ya san inda ke yi masa ciwo, don yawaitar ilmin boko da na addini.

Wani abin lura kuma, matasan nan da ke yin irin waxannan waqoqi na farfaganda, ba su ratso zamanin mulkin mallaka ba, balle a ce sun xanxana irin haka, shi ya sa yanzu suke nema da a yi tawaye ga shugabanni. Amma sai ga irin waqoqi da aka yi zamanin neman ‘yancin kai, kamar waqar *Arewa Jumhuriya Ko Mulukiya* da ke farfaganda zuwa ga al’ummar Arewa, musamman ga sarakuna cewa kada a yarda da tsarin Jumhuriya sun dawo.

Don haka, a wannan babi, aka yi nazarin ruhin wannan aiki wato Farfaganda. An kawo taqaitaccen tarihin mawaqan tare da bayanin salsalar waqoqin. An yi binciken dalilin da ya haifar da samuwar waqoqi masu jigon farfaganda. Sai dalilin da ya sa aka kira su waqoqin farfaganda. An kuma bayyana yadda farfaganda ta shafi waxannan waqoqi na zamani, wato aka yi qoqarin gano inda waqoqin suka fi karkata a cikin nau’o’in na farfaganda. Har wayau, a wannan babi aka yi nazarin manyan rassa guda huxu da waqoqin nan na fiyano suka qunsa. An bayyana yadda marubutan suka yi amfani da yanayin gudanar da mulki da addini da tattalin arziqi da zamantakewa a cikin waqoqin suka yi farfaganda. Wato a nan ne za a sha romon farfaganda.

### 4.1 Tarihin Aminu Ladan Abubakar (ALA)

An haifi Aminu Ladan Abubakar (Ala) a shekarar 1973, a jihar Kano, a unguwar Yakasai. Ya yi karatun primary school daga shekarar 1980-1986 a Tudun Murtala primary school. Sannan daga bisani ya tafi Dakata Kawaji Govt Senior secondary School daga 1986-1992. Daga bisani ya samu tsaiko wanda ya ba shi damar shiga cikin harkokin rubuce-rubuce na qagaggun labarai. Ya rubuta littattafai kimanin guda tara ko sha xaya. Littafinsa na farko shi ne *Jirgi xaya shi ke xauke da mu* 1-3, da *Ceto Ko Cuta* , da *Cin Zarafi,* da *Baqar Aniya,* da *Qawa Zuci*, da *Tarzoma*. Daga bisani ya koma ya yi national diploma a department of Arts and Industrial Design a SOT, School Of Technology. Bayan haka, yanzu yake qoqarin shiga Open University don ya yi digiri.

Ya yi aiki da Hikima Multi Media daga shekarar 2007-2008. Ya yi kimanin shekaru biyar yana a matsayin manager. Daga bisani ya buxe kamfaninsa yau shekara xaya kenan, wanda yake a Guda Abdullahi Way, lamba ta 23, Garban Gora House, Farm Centre, Kano, mai suna Taskar Ala Global Ltd.

Sannan kuma, ya tsunduma harkar waqa tun yana xan Islamiyya. Tun ana koya masu darasi da ilmantarwa, cikin abin da ya shafi addini, har suka samu kimshe na sha'awar waqa kuma daga sauraren marubuta waqoqi iri daban-daban, daga jagorancin mutane iri daban-daban, irin su Abdullahi Sani makarantar lungu, wani tsohon ma'aikacin gidan rediyon jihar Kano. Sannan ya yi shekara biyu yana gabatar da waqa ana yi masa tambayoyi a dandalin qungiyar marubuta ta qasa, reshen jihar Kano, Association Of Nigerian Authors, ita ake ce ma ANA, Kano. Ya yi shugabancin qungiyar marubuta ta jihar Kano, wadda aka fi sani da HAF. Hausa Authors Forum,

daga bisani ya yi murabus da kansa. Yanzu kuma yana nan a kamfaninsa mai suna Taskar Ala Global Ltd.

### 4.1.1 Dalilin Rubuta Waqar *Baubawan Burmi* da *Bubukuwa* da *Xaurin Gwarmai*

**i. Baubawan Burmi:** Ya bayyana cewa baubayi wasu mutane ne da suke a tsakanin Nasarawa da Bauchi, sunan nan kamar Gwari ko in ce Gbagy. Idan aka yi magana ba daidai ba, sai a ce to ka zama kamar Gwari, saboda Gwari yana so ya yi Hausa sai ya rinqa faxin ta ba daidai ba. Su kuma Baubayi sukan yi magana da takan sava da yadda masu harshen suke faxi. Duk yadda baubawa yake ko takalmi ne zai sa, zai iya sa hagu a dama, dama a hagu, don ya bambanta kansa da sauran mutane da ba baubayi ba, su ne ake kira baubayi. Kuma a Larabci, a kalmar Larabci, an ce 'wal ajlu', da mu baubayi waxanda ba Larabawa ba. Saboda haka, wanda ma ba Bahaushe ba kana iya kiransa Baubawa, amma wanda yake yin wani abu ba daidai ba, savanin daidai shi ne ake kiransa Baubawa.

Abin da ake nufi da 'burmi', shi ne kamar a kifa wata qwarya a cikin wata qwarya don hana abin da aka xebo na daga ruwa ya riqa tangal-tangal. Idan aka saka qwarya qarama, za ta kamfato ruwan ta kwanta a ciki, idan aka saka qwarya babba, ruwan zai yi tangaxi ya varar da ita. Saboda haka, sai ka yi burmi, daidai wanda zai shiga ya zauna. Saboda haka idan aka yi baubawan burmi, an yi burmin da ba daidai ba, wato burmin bai zauna ba, shi ne abin da ake nufi da 'Baubawan Burmi'.

Ya yi waqar *Baubawan Burmi* ne a kan tsarin shugabanci ko tsarin zaven shugaba, saboda haka ta kalli dimokraxiyyar Nijeriya. Yadda muka xauki dimokraxiyya da yadda muke gudanar da ita ya sava da yadda aka tsara dimokraxiyyar. Yadda muke zaven shugaba, mu xora shi a kan mulki, ya sava da irin kwalitin da shugaba yake gabatarwa a zave shi. Wanda ya xauki kuxi ya watsa a qasa, muka yi wawa, shi muke xauka mu xora a kan shugabanci. Wanda ya biya mu, ya sayi quri'armu, shi muke xauka mu xora, ba tare da bin diddiqin asalinsa, kwalitinsa da nagartarsa, da kuma irin alqawurran da ya xauka, wanda ya ja hankalinmu da su mu zave sa. To, ba mu bin duk waxannan qa'idoji, illa iyaka kawai muna zaven 'yan baranda ne waxanda za su jiqa shalisho da sauransu. Kamar yadda waqar ta qunsa, za a yi yaqin neman zave babu 'yayansu, babu 'yanuwansu, tun daga nan ka gane cewa ga irin dimension xin da siyasa ta xauka gurvatacce ne. To, wannan shi ne abin da *Baubawan Burmi* ta qunsa. Wanda jigonta ya fara tun daga amshinta, 'Baubawan burmi, kasassavarmu ce kan zaven jagora'.

**ii. Waqar *Bubukuwa***: An yi ta ne a kan azzaluman shuwagabanni, waxanda sukan yi sata ba a kula ba, amma kuma an fi kula da qaramin varawon da zai haura gida ko ya tare hanya, sata kuma sata ce. Wannan ya faxaka a cikin warwarar jigo xin. Wato dai, waqar na magana a kan tsarin shugabanci da rashin tsaro a qasa, tana kuma nuna sauri babu wurin zuwa. A qamusun Hausa na Jami'ar Bayero Kano, sun ba da ma'anar bubukuwa cewa wata ciyawa ce da ake fitowa da an yi ruwan farko. Ya sake bayyana cewa, wasu na ganin bubukuwa wani tsuntsu ne, wasu kuma sun ce qwaro ne mai nawar tafiya. Waqa ce da aka yi akan gurvatattun shuwagabanni, wanda suke tafka varna amma ba a yi masu hukunci.

**iii. Waqar *Xaurin Gwarmai*:** Gwarmai dai wani mutum ne a tarihi. Akwai kuma gari Gwarmai. Ya yi qulli, sai aka ce ya kwance, sai ya kasa kwancewa, irin sa ake yi wa salga. Shi ya sa ake shaguve, ake cewa "Kar ka yi mani xaurin gwarmai mana". Shi ya yi qulli ya kasa kwancewa. Shi ne xaurin da aka yi wa Nijeriya a cikin tsarin mulki, har an kasa warwarewa a cikin halin da ake ciki. Wato, irin halin da Nijeriya ta shiga kenan, an kasa shawo kan matsalar.

Dukkansu dai kusan manufofinsu xaya, illa iyaka an samu rabe-rabe na ayyuka, misali *Baubawan Burmi* ta kalli siyasa, ita kuma *Xaurin Gwarmai* ta kalli ma'adanai ne, da gundarin arziqin da Allah Ta'ala Ya yi wa Nijeriya, da baiwa amma, kuma muke cikin wahala saboda rashin lida. Ita kuma *Bubukuwa* tana bayani a kan rashin tsaro na qasa da rashin shuwagabanni, kuma mai dokar bacci, yana gyangyaxi.

## 4.2 Tarihin Jibrin Muhammad Jalatu

An haifi Jibrin Jalatu a shekarar 1985, a wani qauye mai suna Jalatu, a cikin Bakori, a Katsina kenan. A nan dai ya tashi kamar shekara tara. Ya yi karatunsa a Bauchi, a qaramar hukunar Ningi ya yi tsawon shekara tara a Ningi. Sai ya dawo Kaduna, yana zaune na tsawon shekaru takwas zuwa tara. Duka dai shekarunsa ba su wuce ashirin da bakwai ba. Yana da mata xaya, da xiya xaya. Yana zaune a Kaduna, a unguwar Rimi.

Ya fara tu'ammali da waqa tun yana xan qarami. Amma ba bugawa irin yadda ake a fiano ba, ko kuma a yi ta da ganguna ba. Amma bai fara tunanin buga ta ba, sai 2003, ya fara tunanin shiga sitidiyo domin ya yi waqa. Amma fa lokacin duk ba a kai ga bugawar ba. A lokacin da ya fara buga waqa a 2005-2006 a tsakanin nan.

### 4.2.1 Dalilin Rubuta Waqar Mafarkin Mulki I da II da Ku Yi Haquri

***i. Waqar Mafarkin Mulki I*** da ***Mafarkin Mulki II*** tun yana xan qarami ya fara tunanin yaya zai yi ya isar da saqo ga al'umma. Sai ya ga yadda yanayin rayuwa ke tafiya wasu na jin daxi, wasu kuwa cikin wahala suke. Ya ga yadda ake fama, sai ya xauka cewa duka duniyar abin haka yake. Daga baya sai ya fara ganin ashe akwai bambanci tsakanin 'yan nan gidan, da 'yan can gidan, ma'ana da ya fara buxe ido kenan. Sai ya fara tunanin tunda haka ne, ya za ya yi qoqari ya gaya wa mutane, amma ta yaya? Kawai Allah da na Shi iko, sai ya fara tunanin bari ya ce shi shugaba ne mai mulki, to amma kuma sai ya ga hankalin mutane ba zai iya xauka ba.

Sai da ya fara girma, ya fara hankali, sai ya ga ashe akwai bambanci. Daga nan ya ce bari ya yi waqa ya nuna akwai talaka a duniya, akwai wanda ke wahala. Amma kuma hakan, sai ya ga ya faxa, an riga shi faxi. Wancan ya ce akwai talaka, wancan ya ce akwai talaka. Qarshe sai ya ce, bari ya zama shi ne shugaban qasa, amma ba mai adalci ba, shi mai muzgunawa talaka, don a san saqo ya isar ta wannan manufa.

Da ya yi shi haka, sai ya ga kai ai hankali ma ba zai xauka ba, a ce kamar shi yaro shi ne shugaban qasa, kai hankalin mutane ba zai xauka ba. Yana nan da shi a kai, bai rubuta ba sai a 2006. Sai ya rubuta ta ya aje, bai buga ba sai a 2009. Lokacin da ya rubuta sai ya ce mafi alfanu, gara ya ce a mafarki ne, shi kuma mafarki an san ko a yaya kana iya yinsa. Don ko ka ce kai shugaban qasa ne ma, abu ne mai sauqi. Sai ya ce bari kawai ya ce shi shugaban qasa ne. Lokacin da ya yi waqar sai wasu su ce da wane yake, wasu su ce da wane yake. Shi dai ya yi domin ya isar da saqon cewa akwai waxanda suke wahala a duniya, ba wai duka ne ake jin daxi ba. Sannan kuma, waxanda ke cutarwa xin, duk iyakacin abin da za su yi, a duniya ne. Shi ya sa ma za a ji ‘yan amshi suna cewa a ‘duniya’.

**ii.Waqar** ***Ku Yi Haquri:*** Ita ma wannan tana tare da su ne tunda an ce “jinjinar talakawa ce, daga Jibrin, haqurin nan da muke yi, kada mu gaza, mu qara zai mana amfani can”, can lahira ma’ana. Abin da ya duba, sai ya ga gaba xaya, duk waxannan abubuwan har qasa taka ce, haqqi naka ne. Shuwagabannin kai ka zava, kai wai kuma fa kai suke mulki, amma ba su damu da cinka, ko shanka, ko kuma lafiyarka, ko kuma lafiyar iyalinka ba. Duk wata matsala ba su iya taimaka maka, balle a ce sun kare ma ita. Wanda kuma a yadda addini ya nuna mana shi ne a kula da su, a kare haqqin talaka. Sai yake nuna wa talaka, yana mai shi jinjina ta musamman da yake yin haquri. To, amma fa kar ya gaji da wannan haqurin, insha Allahu zai masa amfani a can lahira. Shi ya sa yake cewa “Jinjinar talakawa ce”.

### 4.3 Tarihin Haruna Aliyu Ningi

An haife Haruna Aliyu Ningi a ranar 22/11/1972 a garin Ningi, a wani qauye da ake kira Rumbu. Ya yi karatu na firamare da sakandare duk a qaramar hukumar Ningi. Ya je makarantar polytechnic da ke Qauran Namoda, a nan ya yi karatun diploma, ya karanta financial studies, ya gama a shekarar 1996. Daga nan dawo, sai ya shiga harkar siyasa a shekarar 1997 lokacin Abacha, wannan shi ne sanadin fara waqarsa ta siyasa. Iyayensa babu wanda ya tava yin waqa, iyayensa malamai ne, ba gado ya yi ba karambani ne . Yana da mata huxu da ‘yaya shidda.

#### 4.3.1 Dalilin Rubuta Waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* da *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi* da *Hawaye*

**i. Waqar *Ba Mu Yarda Ta zarce Ba:*** Abin da ya sa ya yi ta dalilai ne guda biyu, na farko dai tukuna shi ne ya wayar wa ‘yan Nijeriya kai. Su san mene ne ‘yancinsu a dimokraxiyya. Na biyu kuma shi ne, abubuwan da Obasanjo ya xauko a lokacin sun sava wa tsarin mulki na qasa, idan aka bar su, kuma suka xore, to ba mu san abin da zai kasance a qarshe ba. Domin ya zamana za a samu a wani ruxani wanda ba mu san qarshensa a qasa ba. Shi ya sa ma a cikin waqar ya ce “A kan mutum xaya ba za a sa qasarmu a yaqi ba.” Inda a ce an bar shi ya aiwatar da wannan abin, da mulkin dimokraxiyya kusan ya zo qarshe ke nan, tunda za a mayar da abin ba qa’ida. To, waxannan abubuwa suna xaya daga cikin dalilan da ya sa ya tsaya ya yi wannan waqa. Domin a wannan lokaci ana ganin ba wanda ya isa ya faxa xin, to amma komi a rayuwa sai da sadaukarwa, wannan shi ne dalilin da ya sa ya yi waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*. Ba waqa ce da aka sa shi ko aka biya shi ba, waqa ce da na yi a matsayin sadaukarwa.

Waqar ta yi tasiri na rushe shirin ta zarce sosai, domin lokacin da aka yi ta, an kai ta Majalisar Dokoki ta qasa ne. ‘Yan Majalisar da suka ji abubuwan, sai suka dinga xaukar waqar suna tafiya da ita mazavunsu suna raba wa jama’a, to sai jama’a suka farga da wuri-wuri, sai suka yi caa a kan lamarin cewa lallai su kam ba su yarda ba. Ya rubuta waqar a shekarar 2007.

***ii. Waqar Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi:*** Waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi* abin da ya sa ya rubuta waqar a lokacin da ka yi zaven 2007 a jihar Bauchi, an samu rikice-rikice, an ta kashe-kashen rayuka ba adadi. Sai bayan an zo an kafa gwamnati, sai duk waxannan mutanen da suka yi ta’addancin kashe-kashen, ya zamana duk yawanci an koma ana kama wasu, wasu na gidan yari, wasu sun gudu. Kusan dai kawai abin ya zo masu ba daidai ba, duk abin da aka yi, ba a ci gajiyar da su ba. Sai aka ga zaven 2011 ya doso, kuma ba mamaki a sake kwata irin waccan abin da aka kwata a baya. Shi ne ya ga ya kamata yu kira jama’a su fahimta cewa duk waxannan abubuwa da suke yi ba riba. Shi ne ya yi qasida *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi*, *Manyanmu Na Inuwa Mu ne A Rana*. Saboda dama, da matasa da mutanen karkara su ake amfani da su wajen tada ta’addanci da rikicin siyasa, idan an samu mulki, su ne ba a yi da su. Shi ne suka kira su a cikin wannan waqar a kan su fahimta cewa gaba tsakaninmu ba ta da amfani, ba don su kyautata mana ba, don biyan buqatunsu ne kawai. Ya qara da cewa, waqar ta yi magana a kan yadda talakawa da matasa ke xaukar siyasa kamar do-or-die, alhali manyanmu suna amfani da mu ne, ba wai suna kyautata mana ba. Daga lokacin da suka samu mulki, sai su yi ko oho da mu.

**iii. Waqar *Hawaye:*** Akwai hukuma da ake kira ‘Gyara Kayanka’, lokacin da Nijeriya ta cika shekara hamsin da samun ‘yanci, sai ta shirya wata gasa, a kan kowa da mawallafi, ya je ya

rubuto me ye ra'ayinsa game da samun 'yancin Nijeriya. Shi a nasa ra'ayin, da ya tsaya, ya yi nazari, sai ya ga a shekara hamsin da muka yi da 'yancin kai, kusan cewa abin kuka ne za mu yi a Nijeriya, ba wai murna ba. Domin qawayen Nijeriya da suka samu 'yanci tare, suka fara abubuwa tare, yanzu haka sun ci gaba, wasu na qera nukiliya. Mu kam har yanzu ba abin da muka tavuka. Wannan abun sai ya ga mu ba murna ya kamata mu yi ba, kuka ya kamata mu yi. Shi ya sa da ya buga waqar sai ya sanya mata suna *Hawaye* a cikin waqar akwai inda yake tambaya cewa, shin mamarmu kuka take yi ko murna take yi? saboda irin abubuwan takaicin da ke faruwa a qasar nan. Wannan shi ne dalilin yin waqar *Hawaye*. Wato kuka za a yi, ba batun murna muke ba. Ya ce Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu, tunda idan ka ce mace ta kai shekara hamsin, ba budurwa ba ce. A shekara hamsin Nijeriya rarrafe take yi, shi ne yake tambaya, shin me ya faru.

### 4.4 Tarihin AbdulAziz Abdullahi Ningi

AbdulAziz Abdullahi Ningi, wasu kuma suna masa laqabi da PTF, saboda ya yi wa PTF qasida wacce ake kira *PTF qawata, Kin Zama Garkuwa Yau Ga Al'ummar Qasata*. Ana sa wa a gidan rediyon Kaduna. Ya yi makarantar firamare da ake kiranta Garxo Nomadic Primary School irin makarantar 'yayan Fulani. Ya yi firamare zuwa 1987. Daga nan sai ya tafi GSS Ningi ya yi karatun shekara uku. Daga nan ya tsaya da karatu. Ya koma hidimar kasuwanci. Ya fara tu'ammali da qasida tun zero party a shekarar 1996, lokacin ba jam'iyya, zamanin Babangida gabanin na Abacha. Daga nan har ka zo, aka yi UNCP da DPN, a lokacin ya yi ra'ayin DPN, shi kuma Haruna ya yi ra'ayin UNCP.

### 4.4.1 Dalilin Rubuta Waqar *Rigar 'Yanci*

**i. Waqar *Rigar 'Yanci:*** Ita dai wannan waqa ya yi ta a shekarar 2007, ganin irin abin da yake tafiya a Nijeriya, na irin yanayin siyasa tunda ita siyasa an mata laqabi dai rigar 'yanci ce, amma kuma sai ya zamana, xaya daga cikin 'yancin, shi ne kai ra'ayin wanda kake so. Biyu daga cikinsa, ka kaxa quri'a ga wanda kake so. Uku daga cikinsa, a tabbatar maka da wanda ka kaxa wa quri'a. Sai ya zamana duka a qasarmu Nijeriya hakan ba ta samuwa. Ba a barin ka da zavin wanda kake so, kuma in ka kaxa quri'ar, ka kaxa a banza. Sai dai a je, a xauko wanda ake ra'ayi, wanda zai biya buqatar waxansu miyagun qasa, maimakon wanda za a zave sa bisa ra'ayi na mutane, don yi wa mutane aiki. Wanda ta wannan siga ce, abin da kuka zava da quri'a, ya zama shi aka tabbatar, shi ne kuke da dama da iko a kansa. Wanda zai iya kasancewa shi ne bawanku, wanda zai yi maku bauta. Ku kuma waxanda kuka kaxa quri'a, ku ne iyayen gidansa. To, amma yanzu waxanda ake naxawa, su ne iyayen gidan masu kaxa quri'a, masu kaxa quri'a su ne suka koma bayi.

## 4.5 Tarihin Muhammad Sani Aliyu

An haifi Muhammad Sani Aliyu a garin Katsina, a unguwar Qofar Qaura a shekarar 1974. Ya yi makarantar firamare a Qofar Qaura primary school. Ya yi JSS a ATC. Sannan ya yi Teachers College Dutsinma, UPE Dutsinma, a matakin grade II. Bayan ya gama grade II, sai ya wuce polytechnic da ke Katsina a shekarar 1992-1993 ya samu qaramar diploma. Ya sake komawa a shekarar 2006 inda na kammala HND a vangaren Business Administration. Ya tava ayyuka a wurare. Ya tava aikin koyarwa a makarantu masu zaman kansu, da kuma makarantun gwamnati.

Yanzu yana tare da gidan rediyon companion FM, inda yake gabatar da wani shiri wanda ake ce masa *Tun Yana Xanye*. Ya fara sha'awa ya yi waqa kusan tun yana firamare. Ya taso da xabi'a ta son waqa. Bayan ya gama sakandare sai ya ga cewa ya kamata ya bayar da gudunmuwa a cikin al'umma, ya kamata ya yi wani abu wanda zai shafi al'umma baki xaya.

### 4.5.1 Dalilin Rubuta waqar *Almajiri*

**i. Waqar *Almajiri:*** Ya ce ya daxe da rubuta ta, kusan kimanin shekara goma ko sha biyar da tunanin ya fara yi wa almajiri waqa. Saboda ya kula da irin yadda rayuwa ta almajiri, ba yana nufin kowane mai bara ba. A waqar ba ya nufin musakai da makafi da manyan mutane masu bara ba. A waqar ya mayar da hankali a kan yaro karami wanda ake turawa makarantar allo ya je, ya yi karatu. Abin da ya sa ya fi mayar da hankali, ya ga cewa ita rayuwar yaro tana buqatar wata kula ta musamman. Kuma tana buqatar wasu haqqoqi da za a kula da shi domin ya yi karatu. Sai ya ga ana tura yara su yi karatu, amma sai ya zamanto maimakon yaran nan su yi karatu, suna ta wahalhalu na rayuwa, a qarshe wasu ma ba karatun suke yi ba. Sannan kuma, a ma yanayin da suke xin su nemi karatun, gaskiya duk wata qa'ida ta neman karatu kusan an sake ta. A tunaninsa ba yana kushe ko kuma zargi, ko qoqarin hana karatu na allo ba ne. Yana so ya zamanto, yara sun sami ilmi na addini. To, amma kuma hanyoyin da ake bi yaran su samu ilmin, gaskiya akwai buqatar gyara a ciki. Ma'ana sai yake ganin yaro shi ne abin da za a tausayamawa a cikin al'amarin. Ya kamata shi yaron a kula da shi in dai ilmin ake son ya samu. Ya yi waqar *Almajiri* amma ba don wata qungiya ko wata gwamnati ta sanya shi ba. Tunaninsa ne kawai.

## 4.6 Taqaitaccen Tarihin Siyasa a Nijeriya

A shekarar 1900, sojojin Birtaniya (Ingila) qarqashin jagorancin gwamna Lugga (Frederick John Deathry Lugard) sun rushe yarjejeniyar Royal Niger Company da ke kula da wasu sassan da aka sani da Nijeriya a yanzu, suka kuma yaqi Arewa ta zama a qarqashinsu. Cibiyar mulkin Arewa, Sakkwato, ta faxa qarqashinsu a 1903, kuma ta qunshi garuruwa irin su Katsina, Kano, Adamawa, Daura, Zazzau, Haxeja, Jama'are, Misau, Kazaure, Ilorin, Bida da sauransu. A 1906, kusan dukkan Daular Usmaniyya wadda ta kafu a 1804 ta faxa hannun Turawan Mulkin Mallaka, haka kuma sauran sassa na Kudancin Nijeriya. A shekarar 1914 kuma sai Turawa suka haxe manyan sassan Nijeriya guda biyu Arewa (Protectorate Of Northern Nigeria) da kuma Kudu (Protectorate Of Southern Nigeria). Turawa sun riqa gudanar da mulki mai shamaki (Indirect Rule) har zuwa lokacin da qasar ta sami mulkin kai a 1960. Birniwa (2010)

Lokacin da Turawan Mulkin Mallaka suke cin karensu babu babbaka a qasar nan, ba su yarda an kafa jam'iyyun siyasa kai tsaye ba, domin za su iya zama kishiyoyi ga mulkinsu. Abin da 'yan qasa waxanda suka sami ilmin zamani suka fara yi shi ne kafa qungiyoyin al'adu waxanda a qarqashin inuwarsu ne suka riqa tattauna abubuwa da suka dame su, su da lardunansu, da ma qasar baki xaya, ciki kuwa har da yadda za a samu mulkin kai. Birniwa (2010).

Kamar yadda Gaya (1998) ya zayyana cewa Danbazau ya bayyana cewa "Kafin shekarar 1950 (Miladiyya), babu wata jam'iyya da za a iya kira jam'iyyar siyasa a jihar Arewa. Amma akwai jam'iyyar Mutanen Arewa (JAMA), wadda ta koma jam'iyyar Nijeriya Ta Arewa (JANA). Amma wannan jam'iyyar, ba ta da wani muhimmin amfani a siyasance. A wannan lokaci,

linzamin mulkin mallaka da na danniya, ya fara jinata bakin talakawan Nijeriya ta Arewa, saboda haka, wasu mutane daga cikin jam'iyyar Mutanen Arewa, suka fara yin suka kan cutar da sarakuna da iyayen gidansu Ingilishi.

A wannan lokaci, Abdulqadir Xanjaji ya yi magana kan jirgin qasa a wata jarida da ake kira *comet* da ake bugawa a Kano. Wannan magana ita ce ta yadda reliwe ke danne mutane. Shi kuma Mudi Sipikin ya rera wata waqa ta yadda ake cutar talakawa, musamman na Arewa wajen cinikin gyaxa. A wannan lokaci maimakom jam'iyyar Mutanen Arewa ta ba su goyon baya, sai ta ja kunnuwansu a kan cewa sun vata wa D.O da sarki zuciya. Wannan shi ne farkon layin da ya raba sarakuna da Turawa da 'yan kazaginsu daga cikin 'yan boko a vangare guda, kuma talakawa da ake cuta a xaya vangaren. Wannan shi ne farkon kafa jam'iyyar NEPU. Amma binciken manazarta harkokin siyasa ya fi nuna jam'iyyar NPC ce ta kafu a sanadiyar haka.

Kafin Nijeriya ta samu 'yancin kai, an xan fara harkokin siyasa gadan-gadan, inda aka samu jam'iyyun siyasa irin su NPC da NEPU, sauran su ne, NCNC da AG. Babbar manufar jam'iyyar NPC kamar yadda Birniwa (2010) ya ce 'ita ce kau da jahilci da lalaci da zalunci.' Ita kuwa jam'iyyar NEPU, tata manufar ita ce ' qwato wa talakawa haqqinsu daga hannun Turawa 'yan Mulkin Mallaka da sarakuna da sauran waxanda 'yan jam'iyyar suke ganin suna zaluntar su.

Bayan an samu 'yancin kai a 1960, an ci gaba da gudanar da harkokin siyasa, har lokacin da sojoji suka tafka juyin mulki na farko a Nijeriya, wanda ya yi sanadiyar rasa rayukan manya a qasa da kuma rushewar jam'iyyun siyasa. Tun daga wannan lokaci, ba a sake jin xuruyar jam'iyyun siyasa ba, sai a Jumhuriya ta biyu, da aka samu jam'iyyun siyasa kamar su NPN da

PRP da GNPP da UPN da NPP, amma waxanda suka fi shahara a Arewa su ne NPN da PRP. An sake samun juyin mulkin soja na biyu, wanda ya yi sanadiyar rushewar gwannatin farar hula da ci gaba da mulkin soja har zuwa wani xan lokaci.

Bayan sojoji sun xanxana mulkin Nijeriya na wani lokaci, sai kuma aka kaxa kugen siyasa da nufin mayar da mulki a hannun farar hula. An samu jam'iyyun siyasa mashahurai guda biyu da SDP da NRC, sun ci zamaninsu na xan lokaci. Sa aka sake kawo tsarin mulkin siyasa a qasa, inda aka kafa wasu jam'iyyu irin su GDM da UNCP da CNC da NCPA da sauransu. Haka dai aka ci gaba da harkokin siyasa har zuwa Jumhuriya ta huxu. A wannan Jumhiriya da ake ciki, an sake fito da wasu jam'iyyun siyasa waxanda suka yi fice kamar PDP da ANPP da AD. An samu canje-canje daga baya da qari jam'iyyu kamar CPC da ACN da sauran makamantansu.

### 4.7 Samuwar Waqoqin Farfaganda Na Fiyano

Waqoqin nan da ake yi da kayan kixa na zamani, ba su daxe da samuwa ba. Bincike ya nuna cewa an fara samun su sakamakon cuxanya da Turawa. Fiyano da tasoshi da jita abin kixa ne na Turawa. Kamar yadda Gusau (2008) ya bayyana.

Sulluvewar Gwamnati tarayya daga hannun 'yan Arewa, ya haifar sa samuwar waxannan waqoqi na farfaganda. Ma'ana muhimman muqamai sai 'yan kudu da yamma. Mulki ya sufcewa 'yan Arewa.

Raxaxin talauci da ke damun Arewa, shi ma taimaka wajen bunqasar samuwar waqoqin. Keve Arewa da aka yi, wato ba a damawa da ita.

Sha'awa ta waqoqi a wannan zamani, shi ma ya taimaka, wanda ya samo asali daga samuwar kayan kixa na zamani, da suke amfani da na'ura mai qwaqwalwa, har aka yi masu laqani da kixan komfuta.

Hanyar yaxa su ta bunqasa saboda yaxuwar faya-fayai na CD. Masu sauqin samu da kuma rahusa.

Samuwar wayoyin zamani na hannu masu xaukar sauti su ajiye shi. Har a sautin kira ana amfani da su.

Tofa (2011) ya ce "…Idan ba Arewa a Nijeriya, ba Nijeriya. Domin Arewa ce ginshiqin kasancewar Nijeriya qasa xaya. Duk wahalhalun da miskilolin da Arewa take ciki a halin yanzu, rashin ta samma gyara su da gaske ba qaramar hasara yake jawowa Nijeriya ba". Ya bayyana muhimmancin Arewa kasancewar mafakar duk 'yan Nijeriya. Ya bayyana ma'adanai da albarkatun qasa da Arewa take da su. Ya tattauna matsalolin Arewa. Ya yi maganar shuwagabanni da sarakuna da sauran dattawan Nijeriya masu kishin kai, son juna da hangen nesa. Waxanda suka fito daga qabilu daban-daban, kuma suka rabu a kan addini. A haka suka yi zaman lafiya da lumana, ba tare da tashin hankali ba. Ga taimakon juna. 'Ya'yansu da suka biyo bayansu, ba su koyi da su ba. A Jumhuriya ta biyu aka samu masu kishin kai, har suka samu nasara daidai gwargwado. Abubuwa ba su tafi yadda ya kamata sosai a Arewa ba.

Shuwagabannin yanzu ta kansu kawai suke yi. Ya yi maganar rashin ingancin shuwagabannin Arewa. Lokacin da wasu ke qoqarin a gyara, wasu kuma na qoqarin su vata. An samu shigowar jam'iyyun siyasa gadan-gadan, kuma sun taimaka wajen raba kan manya. Abubuwa sun faru a Arewa marasa daxi. Lokacin da haka ke faruwa, sauran yankunan Nijeriya suna can suna shirya makircin ciyar da Arewa baya. Don Arewa ta wuce su ta vangaren mulki. Ya qara nuna muhimmancin manyan Arewa na da, masu kishin kai. Tunda an daxe ana cin gajiyarsu. Ya kawo tarihin yadda aka gudanar da mulki a Nijeriya. Tun daga mulkin soja har na farar hula, tare da bayyana duk juyin juya halin da aka yi a Nijeriya. Da irin gumurzun da aka yi tsakanin 'yan Arewa. Ya ta'allaqa tavarvarewar Arewa ga 'yan Arewa xin ya ce " A gaskiya duk wanda ya nutsu, ya auna al'amura ba tare da tsoro ba, zai tarar da cewar mutanen Arewa su ne babbar mushkilar kansu ba wasu ba. Lallai mu daina xora wa wasu daban nauyi ko laifin jidalanmu. Mu ne muka rena kanmu har sai da alkadarinmu ya karye, ya fara ruvewa…" Ya kawo shawarwari kan abin da yake ganin zai ciyar da Arewa gaba. Ya yi maganar haxin kai na gangamin taro na kowa da kowa. A bayyana gaskiya al'amurra, don a samu sulhu tsakani da zaman lafiya da sauransu.

### 4.8 Me a Sa aka Kira Su Waqoqin Farfaganda

An kira su waqoqin farfaganda saboda qoqarin da waqoqin ke yi na yaxa wani ra'ayi ko xabi'a ko aqida a zukatan al'umma. Sannan waqoqin na qoqarin canza tunanin mutane da ma faxakar da su don a samu sauyi da canji a tsarin siyasar Nijeriya. Haka kuma, waqoqin na yaxa wasu bayanai da zummar jan hankalin jama'a. Waqoqin na juya tunanin mutane, tare da yunqurin samun tasiri a kansu. Haka kuma, waqoqin na fayyace wa jama'a 'yancinsu, don mawaqan na baza ra'ayinsu da tunaninsu dalla-dalla don jawo hankalin mutane zuwa ga manufa.

An kira su waqoqin farfaganda saboda sigarsu ta kira ga bore da tawaye zuwa ga gwamnatin Nijeriya, don suna bayyana muhimmancin mulkin dimokraxiyya da yadda ya kamata a tafiyar da shi. Mawaqan na jajircewa wajen xaukaka manufofinsu, ma'ana a shirye suke, sun zage damtse, sai sun ga an samu sauyi a siyasar Nijeriya. Waqoqin na kushe da suka da nuna rashin dacewa ga kowane vangare na rayuwar jama'a.

Haka kuma, waqoqin na kangarar da jama'a, suna zaburar da su don wani lokaci suna amfani da vangaranci, wato suna nuna abin kamar Arewa kawai ya shafa. Ga kuma bayyana haqiqanin gaskiyar al'amari, musamman kan abubuwan da suka shafi tattalin arziqi, zamantakewa, da ma siyasar kanta. Sukan fuskanci al'amarin kai tsaye, babu gudu, babu ja da baya. Ma'ana suna nuna jajircewarsu a kan manufofinsu.

**4.9 Farfaganda A Waqoqin Fiyano Na Hausa**

Masana da dama sun bayyana ta bakinsu kan ma'anar farfaganda. Daga cikinsu akwai Doob (1948) da Lasswell (1977) da Ellul (1965/ 1973) da Barlett da Goebbel. Inda suka haxu a kan cewa farfaganda wani qoqari ne na canza tunani da manufofin mutane zuwa da wani abu da ake son su gane. A cikin littafin *The New Book Of Knowledge* an nuna kalmar Farfaganda ta samo asali daga kalmar aikatau ta harshen Latin *propagare*, *to propagate* a Ingilishi ma'ana a yaxa. Tana kuma nufin a watsa ko a isar daga wani zuwa wani. A cikin *Shorter Oxford English On Historical Principles* an nuna kalmar ta samo asali daga harshen Latin *congregation de propaganda fide,* wata qungiyar haxin kai domin yaxa addinin Kirista. Wani kwamitin manya-manya 'yan cocin Katolika wadda shugaba Gregory na XV ya qirqiro. A lokacin da Hausawa

suka aro ta, suka fara mu'amala da wannan kalma ta 'Farfaganda', kalma ce ta Allah da Annabi, wato faxakarwa zuwa ga wani abu marar kyau ko nuna amfanin abu. Daga baya kalmar ta samu yawan ma'ana. Yawan ma'ana na faruwa a harsuna na duniya, wanda shi ma harshen Hausa yakan ci karo da irin waxannan sauye-sauye, inda ake samun kalma xaya tak da yawan ma'anoni a jikinta dangane da muhallin da aka yi amfani da ita. Wurma (2008). Sannan akwai dalilai da ke sa a sami kalma mai yawan ma'ana, kamar juyin zamani, yalwar harshe da sauransu. Don haka, ana kyautata zaton irin haka ne ya samu wannan kalmar da aka aro zuwa Hausa. Farfaganda dai a wajen Bahaushe na yau da kullum tana nufin " Yaxa karya ko yaudara ko wayo ko ma cuta."

Farfaganda kamar yadda aka bayyana a baya, tana nufin duk wani qoqari don yaxa wata manufa a fuskoki daban-daban ko wasu labarai ko dabaru da ake yaxawa cikin hikima. Farfaganda na nufin kevavvun bayanai domin havvaqa wata aqida, ra'ayi ko xabi'a da duk wani qoqari na jan hankali. Tana kuma nufin yaxa wata manufa ko bayani ko qarya ko wani ra'ayi da nufin canza tunanin mutane ko faxakar da al'umma don kawo wani sauyi. Da duk wani yunquri na yaxa wata manufa. Tana nufin watsa labarai na gaskiya ko qarya don a samu tasiri ga tunanin mutane.

Ni kuwa a ganina kuwa, farfaganda wani shiri ne na musamman da a kan yi domin a jawo hankalin jama'a, a sauya tunaninsu, su amince da wani ra'ayi ko tunani da ka iya zama ko gaskiya ko qarya ta yin amfani da wasu alamomi don cimma wani buri na musamman. Irin wannan tsari ne wasu marubuta waqoqin Hausa ke bi, suna ilmantar da mutane kan wani shiri da su marubutan ke ganin bai yi masu daxi ba, watakila abu ne mai amfani ko marar shi ga

al'umma. Akan yaxa farfaganda a gidajen rediyo da talabijin, a jaridu da mujallu, da fina-finai da waqoqi da sauran makamantansu.

Farfaganda wata hanya ce da ake amfani domin a cusa ra'ayi don a jawo hankalin jama'a ga wani al'amari ya alla sabo ne ko tsoho don abin ya samu kavuwa sosai da sosai. Ana yin farfaganda don a nuna qyama ko adawa ga wani abu, don a muzanta ko tallata abin.

Wasu daga cikin waqoqin nan zamani da ake aiwatarwa da kayan kixa na zamani, waqoqi ne na farfaganda da ke qoqarin sauya ra'ayin jama'a da canza wani matsayi da mutum yake da shi zuwa ga wanda ake qoqarin ya fahimta. Haka kuma, waqoqin na qoqarin yaxa manufofinsu domin a samu tasiri a tunanin jama'a ga kuma qoqarin jawo hankali da lallashi don cimma buqata. A don haka, aka yi nazarin yadda marubutan suka yi amfani da yanayin yadda ake gudanar da mulki da addini da tattalin arziqi da zamantakewa a cikin waqoqin, suka yi farfaganda da nufin canja tunanin mutane.

**i.** Waqar ***Baubawan Burmi*** ta Aminu Ala, tana daga cikin waqoqin siyasa na farfaganda, don waqa ce da aka yi da nufin farfaganda zuwa ga al'umma kan yanayin yadda ake aiwatar da mulki, wato ana mulki a hagungunce, ba bisa tsarin da ya dace ba. Waqar ta yi qoqarin faxakar da jama'a illolin shuwagabannin da suka zava, tare da fito da aibobi da halayyar mahukunta a yayin gudanar da mulki. Wato dai, a nuna irin yadda mahukuntan ke jan zaren mulkinsu yadda ya yi masu daxi, ba tare da yin yadda ya dace ba.

**ii.** A waqar ***Bubukuwa*** ta Aminu Ala, bubukuwa kamar yadda ake faxa wata tsuntsuwa ce mai nawar tafiya, wasu kuwa kan ce wata ciyawa ce mai fitowa idan an yi ruwan sama. Ya yi amfani da yanayin tsuntsuwar, ko ta ciyawa ya suranta mahukunta da yadda suke aiwatar da shugabancin nasu. Kamar yadda ya ce:

(1) "Gudun da ba kuvuta ashe, ya zama saukon bubukuwa."

Ita ma waqa ce ta farfaganda da ke bayyana wa al'umma abubuwan da ke faruwa a cikin qasa. Waqar ta fito da hoton siyasar Nijeriya, da nuna yadda shuwagabanni ba su aiki yadda ya dace. Tafiya kawai ake yi babu wurin zuwa, abin da mahukunta ke so shi ake yi, shi ne doka, wato adalci shi ne abin da suke so. Mawaqin ya nuna rayuwa na tafiya bisa tafarkin da bai yi daidai ba. Sai kuma ya nuna cewa shuwagabanni a fanxare suke, a karkace. Ya sake nuna cewa idan ba a canza yadda tsarin yake ba, abubuwa ba za su tafi daidai ba. Ya tavo dukkan rukunonin al'umma, tun daga shuwagabanni, malamai, attajirai da sauransu, ya nuna manufarsa, da nufin cewa idan sun gyara, sauran al'umma za ta gyaru. Ya yi qoqarin baza ra'ayinsa ga al'umma maza da mata, yara da manya da sauran waxanda abin ya shafa kan sha'anin mulkin dimokraxiyyar da ake yi a Nijeriya. Wanda yake ganin mulkin kama-karya ne.

**iii.** Waqar ***Xaurin Gwarmai*** ta Aminu Ala, kamar sauran da suka gabata, ita ma waqa ce ta farfaganda da aka yi da nufin sauya tunanin jama'a kan su zama masu kishin kansu, su kuma zama masu tunani idan sun tashi zaven shugaba. Wanda rashin shuwagabanni adalai ya saka 'yan Nijeriya halin da ake ciki, shi ne ya siffanta halin da ake ciki da xaurin gwarmai. Idan an yi wa mutum xaurin gwarmai a tunanin Bahaushe, an saka shi cikin fitina da bala'i, ana neman mahallakarsa kenan. A wannan waqa, Ala ya kalli taswirar Nijeriya, ya yi maganar albarkatun

qasa da ake da su, kamar ma'adanai irin su tama da qarafa, man fetur. Ya yi maganar qasar noma mai kyau da ake da akwai, wato ya fito da tattalin arziqin Nijeriya gaba xaya, ya yi maganarsu da nufin faxakar da mutane don su san inda aka dosa. Ya kuma nuna cewa jama'a sun qosa da halin wayyo, suna neman sauyi da gaggawa. Ya yi farfaganda qwarai, yana mai baza ra'ayinsa da nufin jan hankalin al'umma baki xaya.

**iv.** Waqar ***Mafarkin Mulki I*** ta Jibrin Jalatu, wannan waqa tana xaya daga cikin waqoqin farfaganda ta siyasa da aka yi a zamanin nan. Mawaqin ya suranta yanayin shuwagabanni da yadda suke tafiyar da mulkin jama'a. Ya bayyana abubuwan da ke faruwa na rashin adalci da zalunci. Ya suranta mulkin Nijeriya tun daga lokacin samun mulkin, har zuwa lokacin da zai qare. Ya kuma zayyana abin da ke gudana tsakanin mahukuntan da mabiyansu, da kuma abin da ke wakana tsakanin mahukuntan da sauran muqarrabansu. Ya jaddada yadda mahukunta ke cin karensu babu babbaka, da sauran abin da ya shafi siyasar qasa na zahiri, duk ya tavo su.

**v.** Waqar ***Mafarkin Mulki II*** ta Jibrin Jalatu, kamar waqar da ta gabata, a wannan ma, mawaqin ya yi nazarin siyasar Nijeriya gaba xaya, ya bayyana shi a cikin waqar. Kamar yadda ya nuna, wannan waqa ci gaba ce ta *Mafarkin Mulki I.* kenan ya suranta siyasar Nijeriya na yadda ake aiwatar da zanguna na mulki, wato zango na xaya da na biyu. Ya ayyana matsalolin da 'yan Nijeriya ke fuskanta, tare da bayyana manyan buqatun da suke mafarkin samu, don kowane shugaba ya hau, da irin yadda yake tafiyar da al'umma. Ya zayyana halin ko-in-kula da mahukunta ke nunawa kan dukkan sha'anin mulki. Ya yi farfaganda sosai, yana mai jaddada manufarsa ta bayyana abin da ke wakana tun daga samun mulki har zuwa qarshe.

**vi.** Waqar ***Ku Yi Haquri*** ta Jibrin Jalatu ko da jin sunan waqar, akwai wasu alamu na sauya tunani da jawo hankali. Don haka, wannan waqa ce ta farfaganda da mawaqin ya yi don ya tallata manufarsa zuwa ga mutanen Nijeriya kan kura-kuran da shuwagabanni ke tafkawa. Ya yi hakan ne, ta hanyar ba da hakuri, da nuna lallai ana yin abubuwan da ba su kamata ba. Don haka, a yi haquri, a mayar da komai ga Allah. Mawaqin ya baza ra'ayinsa sosai. Maimakon ya buxe waqarsa da basmalla kamar yadda aka saba, sai ya buxe da tararrabi da rashin jin daxi, wanda ya bayyana lamarin zuwa wani matsayi na ban tausayi, da ban tsoro:

(2) A dinga tunani,
Akwai jin tausai,
Akwai jin tausai,
Akwai jin tsoro.

**vii.** Waqar ***Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*** *ta* Haruna Aliyu Ningi, Xan'Asabe da Wushishi (2008) sun bayyana cewa, waqa ce da Haruna Aliyu Ningi ya rera. Shi dai asalinsa mutumin Bauchi ne, kuma a farkon wannan Jumhuriyar xan PDP ne, don har ya rerawa jam'iyyar waqa. Bayan shekaru huxu na farko, sai PDP ta xare, wasu suka fice, wasu aka ce an kore su. Da tafiya ta yi tafiya, sai jam'iyyar ta zama ta wasu qalilan waxanda ba su, suka kafa ta ba. A shekarar 2003, da aka sake zave, zango na biyu, sai PDP ta sake kafa gwamnati. A dokar qasa, ba a ba kowa damar ya nemi takara ba, bayan shekaru takwas, wato zubi na biyu. Dab da qarshen mulkin PDP, sai suka nemi su juya tsarin saboda Obasanjo ya ci gaba. A matsayinsa na xan jam'iyya wanda ba ya goyon bayan Obasanjo ya ci gaba, sai Haruna Ningi ya tsara waqarsa mai sunan *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*. Ya rera waqar a lokacin da ake gwagwarmayar yin canje-canje a tsarin mulkin qasa.

Shi kuwa Hussaini (2009) cewa ya yi "Kamar yadda mawallafin ya ce 'Na yi wannan waqar ne domin in ba da tawa gudunmuwar ta rusa mugun nufi na shuwagabanni masu son dagula tsarin mulkin qasar nan."

Kamar yadda sunan waqar ya bayyana *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*, waqa ce ta farfaganda, mai qoqarin tunzura ‘yan Nijeriya da su bijirewa tsarin nan na ta zarce, wanda aka yi qoqarin tabbatarwa a Nijeriya. Amin (2000) ya qarfafa cewa “Masana lugga, Galadanci (1976) da Bagari (1981) sun bayyana cewa duk inda qunshin zance ya zo tsakanin ba……..da……ba, to jimla ce korau, wacce ke kore abu gaba xaya.” Idan haka ne kuwa, wannan waqa an yi ta ne don a nuna bore da bijirewa tsarin ta zarce. Haka, waqa ce ta farfaganda, domin ta yi qoqarin sauya tunanin al’umma, hakan ya faru ta irin karvuwar da waqar ta samu a wurin jama’a. Tasirinta a wurin jama’a ya jaza rushe shirin ta zarce, har ba a samu damar aiwatar da tsarin ba. Haka kuma, waqar ta yi qoqarin wayar da kai sosai, kusan ma a ce ita fara fargar da ‘yan Nijeriya.

**viii.** Waqar ***Kada Mu Xauki Siyasa Sa Zafi*** ta Haruna Aliyu Ningi, kamar sauran waqoqin na farfaganda, ita ma wannan waqar an yi ta domin kiran jama’a musamman matasa, su farga, su lura da irin abubuwan da suke gudana na harkokin siyasa. Ya yi kira ga jama’a cewa kada su xauki siyasar nan da zafi, don ya bayyana laifin jama’a da irin aibobin da suke tafkawa a wurin gudanar da siyasa. Ya nuna yadda shuwagabanni ke amfani da mutane don su ci zave, bayan samun mulkin sai su watsar da jama’a. Shi ne ya yi kira ga jama’a da su sauqaqa wa ransu, su sa shi a inuwa, don mahukuntan nan dai ba ta mu suke yi ba. Shi ne mawaqin yake cewa jama’a “Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.”

**ix.** Waqar ***Hawaye*** ta Haruna Aliyu Ningi, ko da jin sunan waqar, akwai alamu na jan hankali da qoqarin sauya tunani. Waqar *Hawaye* an yi ta da nufin ankarar da mutan Nijeriya, su san halin da Nijeriya take ciki. Kamar yadda Ningi ya ce: “Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu, amma tana rarrafe shin me ya faru.” Duk da cewa an yi waqar a lokacin da Nijeriya ta cika shekara hamsin da samun ‘yancin kai. Mawaqin na ganin ga Nijeriya da shekaru, ya kamata a ga wani abin kirki, abin a zo a gani a cikinta, amma ta zama kamar wadda aka haifa yanzu, wato wadda ta samu

‘yanci babu daxewa. An yi waqar domin a tunasar da ‘yan Nijeriya halin da qasarsu take ciki, me ya kawo hakan, wato rashin shuwagabanni da za su tafiyar da mulkin yadda ya dace.

**x.** Waqar ***Rigar ‘Yanci*** ta AbdulAziz Abdullahi Ningi, babu shakka, waqar an yi ta ne da nufin yaxa wata manufa a zukatan al’umma, domin mawaqin ya yi qoqarin fito da muhimmancin siyasa, da yadda ya kamata mulkin dimokraxiyyar ya kasance, har shi ya sa a cikin waqar yake cewa “Siyasa rigar ‘yanci, an ba ta sunan qwarai”, amma yadda ake aiwatar da ita a Nijeriya bai yi daidai ba. Ya cigaba da nuna yadda ake gudanar da mulki a hagunce, da yadda ake cuta wa talaka, babu wata kima da daraja. Ya fito da matsalolin da Nijeriya ke fuskanta, kamar matsalar rashin ‘yancin kai, wadda ta shafi danne haqqi, shi ne mawaqin yake kira ga dukkan al’umma da a tashi tsaye a nemi ‘yanci da canji, don lokaci ya yi. Sannan ya yi qoqarin wayar da kan jama’a kan manufofin siyasa na haqiqa, wato yadda ya dace a gudanar da ita cikin lalama da taimako, da bin haqqin jama’a, da sauran al’amuran siyasa baki xaya. Ya yi amfani da kakkausan harshe, yana mai kira da a yi tawaye, tare da nuna muhimmancin siyasa ba mulkin mallaka ba.

**xi.** Waqar ***Almajiri*** ta Muhammad Sani Aliyu, ita ma an yi ta da nufin farfaganda ta siyasa mai jivi da addini. An yi waqar ne domin a jawo hankalin jama’a su lura da halin da almajirai suke ciki. Waqar ta yi qoqarin bayyana matsayin almajiri da irin yadda rayuwarsa ke gudana a matsayinsa na mai neman ilmin addini. Ya nuna muhimmancin almajiri da hanyoyin da ya kamata a bi don inganta rayuwarsa. Ya yi maganar matsalar iyaye da suke kawo qananan yara karatu. Da sauran abubuwan da suka shafi rayuwarsa.

### 4.10 Waqoqin a Inuwar Farar Farfaganda

Bisa dukkan alamu, idan aka kalli yanaye-yanayen waqoqin da sigoginsu, a iya cewa waqoqi ne da ke da alaqa ko ke a qarqashin inuwar farar farfaganda. An ce hakan kuwa, domin kai tsaye an

san daga kafar da farfagandar take fitowa. Ga kuma amfani da sassauqar hanya don isar da saqon wato waqa. Haka kuma idan aka lura, za a ga cewa mawaqan kan fuskanci lamarin kai tsaye, su faxi abin da suke so su faxa ba tare da wani shayi ko tsoro ba, kamar yadda Aminu Ala ya ce a waqar *Baubawan Burmi* :

(3) "Allah Kai kab ban iko,
In qi abun gudu da fatar bakina."

(4) "Allah Kai kab ban hikima,
In yi ragargaza da harshen bakina.

(5) "In faxakar gun al'umma,
Don su yi qyamata ga mulki na gadara."

Haka ma a waqar *Xaurin Gwarmai* da 'yan amshi ke bayyana cewa:

(6) "Nai mubaya gun Ala, mai rushe shirin wawa,
Mai kira a kan a bi hanya, da ba ta gantsarwa,
Mai ragargaza da zalaqa, da baitocin baiwa,
Mai bindiga, mai tanka da sautin harbawa,
Ilahu kat tsare mu da sharri na duka mai cutarwa,
Mutum da aljani sulikina, tsare mu da cutarwa."

Bayan haka, mawaqan kan yi qoqarin jawo hankalin jama'a ta yin amfani da vangaranci, wani lokacin ma da addini domin cimma buqata ta farfaganda. Kusan a iya cewa waqoqin kacokam don 'yan Arewa aka yi su, duk da kasancewa mawaqan ma 'yan Arewar ne, akwai gugguvin manufar nuna vangaranci a waqoqin da nuna kishin kai. Domin kusan duk abin da mawaqan ke faxa, Arewa suka fi shafa, a Arewa aka fi yinsu ko ma a ce 'yan Arewa ake yi ma wa. Alal misali a waqar *Bubukuwa* ta Aminu Ala, a baiti na biyu, inda yake qoqarin ya nuna yanayin zamantakewa, musamman Arewa cewa ba a gudanar da shi yadda ya kamata, har ma yake ganin wasu abubuwa da suke faruwa, musamman a harkar tsaro, sun wanzu ne sakamakon rashin mahukunta na gari. Ya ce:

(7) “Varayinmu a kan qasa, atifishiyal muka qirqiro,
‘Yan dabarmu a ko’ina, atifishiyal muka qirqiro,
Masu 419 Arewa, na qirqira aka qirqiro,
Wahalar da muke ciki, ita tas sa suka bijjiro,
Na rashin shuwagabanni adalai, da rashin tsaro,
Rayukanmu kamar kiyashi, fagen kulawa ba tsaro,
Rabbi Kai Ne Rahimi, tsare qasar Nijeriya.”

Shi kuwa AbdulAziz Abdullahi Ningi a waqarsa ta *Rigar ‘Yanci*, ya yi kira da neman sauyi musamman a Arewa , don komai na Arewa a baya yake, an xaram mana sosai, shi ne yake kira musamman ga matasa da a dage a nemi ‘yancin arewa. Baiti na 12:

(8) “In ba butulci ba kai, ko nuna wauta ba,
Ya zan ci naman kare, kuma ga na rago ba,
Ya mai ido zai shiga garken makafi ba,
Sauyi muke so matasa, ban da tsoro ba,
Na Arewa an kakkave mu cikin ruwan sanyi.”

A waqar *Baubawan Burmi* Ala ya nuna rashin jin daxinsa kan yadda aka mayar da ‘yan Arewa kamar bayi, babu wani abin kirki a tare da su. An watsar da kimar Arewa, ba mulki, ba ilmi, a baiti na 10:

(9) “Dole in koka da tsiwa,
Dubi qasar nan arewa,
Ba ilmi talakawa,
Ba mu da ikon tavawa,
Mun zama jujin zubawa,
Tarkacen tarkatawa”.

### 4.11 Yanayin Gudanar da Mulki

Siyasa wata kalma ce da ake amfani da ita domin a nuna tsarin tafiyar da jama’a cikin adalci da kuma ba su damar zava ko ba da shawarwari kan hanyar da ta dace a mulke su, ba tare da nuna masu bambanci ba. Bai wa kowa haqqinsa da yi masa adalci, ko kuma hanyar shugabantar

jama'a ba da qarfi na zalunci ba. Tsarin siyasa, wani tsari ne da ya daxe ana amfani da shi a cikin Musulunci. Kusan ma yana da matuqar wahala a raba Musulunci da siyasa, domin yadda suke tafiya xan juma ne da xan jummai. A nan ne malamai suka ce ya halatta ga wanda ya san zai iya shugabantar jama'a, ya kuma tsare masu haqqinsu ya nemi shugabanci. Wannan ya nuna mutum zai iya tsayawa takara , a kuma zave shi. Ya zo a cikin littafin tarihi, muhimmancin siyasa da tasirinta ga al'umma, har ma sai da ta kai, idan babu siyasa, to al'umma ba za ta iya rayuwa a cikin kwanciyar hankali ba.

Bugu ga qari, su waxannan mawaqa, sukan dubi yanayin yadda ake gudanar da mulki, duba irin ta fahimta, su yi nazarin abin da ke faruwa na harkar mulki, sai nuna rashin jin daxinsu. Ta haka, suke qoqarin bayyana wa jama'a irin abin da ke faruwa tun daga samun mulki, har zuwa qarshensa. Sukan dubi hoton siyasar Nijeriya na zahiri, wato abin da ke wakana da gaske, sai su bayyana shi a cikin waqoqinsu, suna masu kira, da cusa wa jama'a ra'ayi kan manufofinsu. Don haka ne waqoqin suka faxo a qarqashin inuwar farar farfaganda, don suna magana kan ainihin abin da ke faruwa a Nijeriya. Haka kuma za a ga yadda ra'in Isar Da Saqo ya kalli irin farfagandar da aka yi da yadda aka isar da ita ga jama'a.

A waqar *Baubawan Burmi* ta Aminu Ala, ya yi maganar siyasar Nijeriya dangane da yadda ake gudanar da ita, shi ne ya nuna cewa ai gara ma lokacin mulkin mallaka, da irin nau'in mulkin da ke wakana a yanzu. Tunda a lokacin, jama'a ba su jigata ba, kamar yanzu. Don yanzu talauci ya dami jama'a, abin dai ba a cewa komai. Da ma Hausawa sun ce 'Kowar tuna bara, bai ji daxin bana ba.' A baiti na 11-13:

(10) “Dangi a duba mini hanya,
Da can da muna a mulkin mallaka.”

(11) “Wahala dai aka ba bawa,
Amma duk tsiya abinci a ba ka.”

(12) “Yanzu ko gadonmu talauci,
Ai kuxarsa ta fi dukanka da gora.”

A waqar *Bubukuwa* kuwa, sai ya nuna cewa duk yanayin da Nijeriya da mutanenta ke ciki, mahukunta suka haddasa hakan. Qasa ta rikice, komai a yamutse, babu cikakken tsaro, sata a ko’ina yin ta ake yi, babu wani tsari na a zo a gani a Nijeriya. Su shuwagabannin ba su da tausayi, aljihunsu kawai suka sani, sai wanda suke so. Talauci ya yi yawa, babu aikin yi, irin haka ke haddasa gurvacewar al’ada. Ya nuna hakan a baiti na 2:

(13) “Barayinmu a kan qasa, atifishiyal muka qirqiro,
‘Yan dabarmu a ko’ina, atifishiyal muka qirqiro,
Masu 419 arewa, na qirqira aka qirqiro,
Wahalar da muke ciki, ita tas sa suka bijjiro,
Na rashin shuwagabanni adalai, da rashin tsaro,
Rayukanmu kamar kiyashi, fagen kulawa ba tsaro,
Rabbi Kai Ne, Rahimi, tsare qasar Nijeriya.”

Haka kuma, Aminu Ala, a waqar *Xaurin Gwarmai*, ya kai kokensa zuwa ga Allah SWT kan abin da ke gudana a qasa, da nufin Allah ya amsa, Ya kuma kawo canji mai amfani, a baiti na 2:

(14) “Ubangiji har kullum Kai nake kai wa kukana,
Mai yaye haddi, gambi na taho da buqatuna,
Abin da ake a qasar nan ya xugunzuma tunanina,
Zan faxi da baxala, an ce da ni na iya bakina.”

Shi kuwa Jibrin Jalatu a waqarsa mai suna *Mafarkin Mulki I*, ya yi magana zuwa ga muqarraban qasa da sauran sarakuna da makamantansu, yana nuna yadda ake ba su cin hanci, idan ana so su

bi wani tsari na musamman wanda gwamnati ke so, su amsa, su yi shiru. Sai ya nuna wani lokaci a kan tilasta su, da su yi hakan. Ya nuna haka a baiti na 3:

(15) "Manya iyayen qasa, su ma na vata lamarinsu,
Su za su zo gabana, a da fa ni za ni je gabansu,
Ina faxi, ina tashi, har ina Allah taimake su,
Sai na sakwarkwata su, na karya qwarin da ke gurinsu,
Idan na zo da tsari suka qi bi, zan gina asusu,
Baho-bahon kuxi zan tattara in kai gabansu,
Wallahi za su bi ni, daga qarshe su shiga uquba."

Sai ya cigaba da nuna yadda ake zaluntar mutane masu gaskiya, da yadda ake kafa hukuma mai kula da kawar da cin hanci da gyaran halin jama'a amma sai a lave a qarqashin wannan inuwar a rinqa cutar duk wanda ya kaucewa wani tsari na gwamnati. Ya dai nuna yadda cin hanci ke gudana a Nijeriya. Ya nuna haka a baiti na 4:

(16) "A yanzu zamanin nan, in ba ka son gaskiya haqiqa,
Kome kake buqata, ka zo da toshiyar baki in ba ka,
Kafin a bincike ni, babu kowa a xaure fuska,
Idan ka nuna taurin kai, zan xau kuxi in ba ka,
Idan ka fanxare mun, zan sanya a addabe ka,
Ni in na kafa hukuma, wadda zan sa ta bincike ka,
Saboda gaskiyarka, za ta sa ka sha azaba."

Aminu Ala a waqar *Baubawan Burmi*, ya qara bayyana halin da mutanen Nijeriya ke ciki, ya nuna cewa talauci ya yi yawa, babu wadatar kirki, jama'a a quntace suke, a kuma wahalce. An dai zama mabarata a wajen shuwagabanni. Baiti na 14-16:

(17) "Talauci shi muka gado,
Jahilci ko ya zamanto rigarmu."

(18) "Ba mu da ikon yin mulki,
Balle mu ciro masharin kukanmu."

(19) "Mun xore da tumasanci,

Mabarata muke a hannun jagora.”

Sannan sai ya ci gaba da fayyace mahukunta, da yadda suke gudanar da mulkin kama-karya, musamman idan aka kaxa kugen siyasa, lokacin da suke yaqin neman zave. Sukan yi varin kuxi sosan gaske, su sa a yi atamfofi da riguna da sauran abubuwa na kamfe, a rarraba wa jama’a, daga waxannan abubuwa da aka raba, ba za a sake wadata mutane da komai ba. A baiti na 20-22:

(20) “Sannan ba sa alkunya,
Daga an doka tamburan nan na siyasa.”

(21) “Kunya ba tsoron Allah,
Su yi oda ta atamfar nan sosa.”

(22) “Sun mammanna gumakansu,
Su rarraba mu xauke su mu xaura.”

Bai gushe ba, sai da ya siffanta nau’in mulkin Nijeriya, da wata siffa ta rashin adalci, zalunci da quntatawa na danne haqqin talaka, tare da nuna cewa mahukuntan dai kansu kawai suka sani. Kamar yadda ya bayyana a baiti na 30-32:

(23) “Allah wanga kashin mulki,
Ya yi kama guda kashin dankali.”

(24) “Na sama ya danne na qasa,
Idan ya so numfashi babu dalili.”

(25) “Jin daxinsu kawunansu,
Alfarmarsu iyalensu suna kibra.”

AbdulAziz Abdullahi Ningi a waqar *Rigar ‘Yanci*, ya suranta yadda ake tafiyar da mulkin Nijeriya. Ya fito da hoton siyasar Nijeriya na yadda ake naxa shuwagabanni maimakon a yi zave, don ba a barin a yi zaven, ballantana a zave wanda ya cancanta. Ya nuna Hukuma kawai ke zavar

wanda take so, kuma dole a yi shi. Sai kuma ya yi kira ga mahukunta da nufin nasiha cewar ba a nan gidan duniya za a dauwama ba, akwai babban masauki da ke jiran kowa. Idan lokaci ya yi, ko sakan ba za a qara wa mutum ba. Duk da haka dai, ya nuna qyamarsa ga mulkin da ke wakana a Nijeriya, ana neman canji. A baiti na 3:

(26) "Wannan Dimurkixiyyar, hanyar akwai kurxiya,
Da'awarsu kullum naxi, an tara 'yan danniya,
Kuma babu mai dauwama, ko qara kwana xaya,
Nasabarta ba dole ne, gun mai rashin gaskiya,
Za mu wanke Jumhuriyar, bana mai gaji ya yi."

Haka kuma, ya ci gaba da nuna cewa kowa na da ra'ayi da damar da zai so wanda yake so, ko ya zava. Don haka, mahukuntan sun bauxe ba su bin tafarkin Allah, ba za a sake zavar wanda ba zai taimaki al'umma ba. Bana dai kan mage ya waye, jama'a sun farga da abin da ke faruwa. Wanda zai taimaki qasa da al'ummarta shi ake fatan a samu. A baiti na 4:

(27) "Ra'ayinka qaunar mutum, damarka ce xan-uwa,
Shin wane me zai mana, ko zai idan yawa,
Ku zubar batun jam'iyya, ba ma qawancen qawa,
Kun daina bautar gumaka, ba mu bin wawa,
Sai wanda zai taimaka wa qasarmu in ya yi."

A cikin waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba,* Haruna Ningi ya yi sallama baki xaya zuwa ga xaukacin 'yan Nijeriya, tare da jawo hankalinsu zuwa ga manufarsa ta farfaganda ta nufin qoqarin sauya masu tunani, ya nuna yana xauke da wani muhimmin saqo a gare su. A baiti na 2:

(28) "To, salama, salama kaf, jama'a ta qasarmu ku saurara,
Na zo da bayani ne, da na tattara a cikin gora,
In ya yi ku amsa min, in bai yi ba, kar ku zubar shara,
Ku kira ni mu tattauna, wataqil ba ku gane bayanin ba."

Maganar wasu manyan qasa, da ba su da kishin qasa, da suke goyon bayan ta zarce ya yi. Ya nuna yadda suka yaudari Abacha, suka so ya yi ta zarce, sai hakan ba ta samu ba, shi ne suke so Obasanjo ya yi karo na uku. Baiti na 3:

(29) "Da akwai wasu gungun 'yan qasarmu a bar qauna,
Ba su yarda da Allah ba, sun mai da qasarmu kamar waina,
Yau na xaga yatsana, ku zo a idonku in nunnuna,
Sun vadda Abacha a da, a yanzun ma ba su qyale ba."

Ningi ya yi qoqarin nuna wa 'yan Nijeriya, manyan qasa, masu goyon bayan ta zarce, da nuna yadda suke qoqarin rikita qasa, su vata duk wani tsari mai muhimmanci. Babu kishin qasa a tare da su, ya nuna da babu irin su, da qasa ta zauna lafiya. Baiti na 4:

(30) "Farkonsu akwai Mantau, ban mance tsiyar da ya shuka ba,
Na biyunsu akwai Ojo, dama ba mu san shi da kishi ba,
Sai Tom kuma and Jerry, ba wai na Fred da Quimby ba,
Da babu tawogar nan, da ba mu samu ta zarce ba."

Ya ci gaba da warware wa jama'a mugun nufin masu son ta zarce, da makircin da suke qullawa a cikin qasar nan mai albarka. Ya ce haka a baiti na 5-9:

(31) "Zan fara batun Mantau, ya mance jiharsu cikin yaqe,
Rikici suka huhhura, dubban jama'a aka yayyanke,
Bai kai masu diyya ba, bai damu ba, su aka faffarke,
In da a ta zarce ne, da kun ga shirin rikici babba."

(32) "Maganar na biyun Ojo, dama bai zo shi da hujja ba,
In ban da rasar kunya ta Ojo da raina karama ba,
Ya za a yi alhanzir, ba za mu kira shi haramun ba,
To, ku je ku ci ba ma ci, ba za a ciyar mu masifa ba."

(33) "Shi Tom da ake cewa, shi ne magininta da shirya ta,
Shi Jerry gwanin baki, shi ne aka ba shi ya yayata,

Allah da Ya karya ta da, ta yanzun zai daxa karya ta,
Sarkin da muke roqo, ba za ya bari mu ji kunya ba."

(34) "Shi xan-baqi, xan Kogi, shi ne suka ba jam'iyyata,
Mu ne muka goya ta, shi ko aka ba shi ya karya ta,
In ban da vatan kai ma, wa zai tafi Kongo bixar mata,
Zamansa a fatin ma, ya ce baxi ba ta da cin zave."

(35) "Da akwai wani gwamna ma, muryarsa ya wanda ya sha maye,
Xan-daudu da jar hula, yara ku kaxa masa nanaye,
Wai shi na ta zarce ne, mun gane abin da yake voye,
Shi Ribaxu yake tsoro, ba wai haxuwa a kiyoma ba."

A waqar *Mafarkin Mulki II* ta Jibrin Jalatu, ya ragargaji siyasar Nijeriya, ya kawo buqatun da 'yan Nijeriya suke fatan su ga sun samu, kamar adalci, a kyautata tsaro da sauran abin da ya shafi rayuwar jama'a, sai matsaloli wanda rashin adalci da rashin gaskiya ke haddasawa. A baiti na 2:

(36) "Suka ce gaskiya, na ce ba zan ba,
Suka ce taimako, na ce ku tafi gaba,
Suka ce yunwa, na ce ba ku mutu ba,
Suka ce tsaro, na ce ba ku gaji ba,
Kama-karya na sanya a gaba,
Kama-karya na sanya a gaba,
Ba ku wanda za ya ture ni a kan mulki."

Sannan, sai ya bayyana yadda shuwagabannin ke aiwatar da mulkin Nijeriya yadda suke so, ya nuna yadda suke ba da damar a yi yadda aka ga dama, a yi zalunci, a kuma cuci jama'a ba tare da shayi ba, saboda suna ganin mulkin na a hannunsu. Ya bayyana haka a baiti na 3:

(37) "Mahukuntan qasarmu duka ku saki jiki,
Iyayen qasa kawai ku saki jiki,
Mahukunta ma duk ku saki jiki,
Ai zalunci ina kan mulki,
Ba wani wanda za ya yi maku raki,
Kome za ai ni ne ke kan mulki."

Haruna Aliyu Ningi a cikin waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi* ya bayyana wa ‘yan Nijeriya matsayinsu a idon mahukunta, wato abin da shuwaganni ke yi wa talakawa masu zavensu. A baiti na 4:

(38) “Kai ne ake yi wa zagi ka dawo,
Kai ne ake maka duka ka dawo,
Kai za a nemi abinka, ka dawo,
Da ka ba su, sui maka kamun sakaina.”

Sannan ya qara jaddada wa jama’a yadda mahukuntan suka xauke su. Yadda suke amfani da talaka wajen siyasa su cimma buqatunsu. Da an samu biyan buqata, ba za a sake sauraren su ba. Wato, yadda suke ruxar jama’a da yaudara da qarya. A baiti na 5:

(39) “Kai za a sa wa aqida a kwanya,
Wacce akai mata fenti da qarya,
Ka kasa gane gabanta da baya,
Sun bar ka kullum da ihu a rana.”

A cikin waqar *Hawaye* kuwa, ya buxe waqar da basmalla, tare da neman taimako ga Allah, don shi ne Mai Nijeriya, da duk abin da ke cikinta. Shi ne yake addu’a Allah Ya gyara sha’anin siyasar Nijeriya gaba xaya. A baiti na 1:

(40) “Bismillah Allahu Mai Nijeriyata,
Kai Ka samar ta har ma al’ummarta,
Kuma Kai kaxai Ka gagari mai raba ta,
Addu’a muke yi Ka sake haxe ta sosai, iye.”

Sannan ya yi salati ga Manzon tsira SAW, da Alayensa da Sahabbansa. Sai kuma ya bayyana takaicinsa na yin waqar cewa halin na tayar da hankalinsa sosai. A baiti na 2:

(41) “To, nai salati ga Musxafa, Xaha Manzo,

Ahali, Sahabbansa su ma, masu qwazo,
Wannan qasidar da za na yi, zan ta yanzu,
Kuka take sa ni, ba murna nake ba, iye."

Sai kuma ya kawo tarihin siyasar Nijeriya, wato lokacin samun 'yancin kai. Duk da dai bai zurfafa ba, ya nuna yadda aka samu 'yancin kai, kuma an samu an tafiyar da siyasar daidai gwargwado. A baiti na 5:

(42) "An ba mu 'yanci na mulkin kai mutane,
Manyanmu sun taru, kowa ya yi zaune,
Sun tsara komai da komai, sun yi zane,
Sun fara aiki na ci gaba manya-manya, iye."

A waqar *Mafarkin Mulki I*, Jibrin Jalatu ya qara fito da kuma bayyana halin mahukuntan Nijeriya, ya nuna cewa ba su dai yin daidai, ba a tafiyar da mulkin yadda ya dace. Ya fito da hali na zalunci da kwaxayi na shuwagabanni. Ya bayyana yadda suke sha'ani da matan banza, da yadda ake ci wa qasa bashin da ya fi qarfinta kuma ba a damu da haqqin jama'a ba. A baiti na 5:

(43) "Tsaro a zamanina a kashe kowa a kan abinshi,
Ni na ci, na yi xaxin, na kwanta ina ta nishi,
Saboda taqamata, ba mai cewa da ni ka tashi,
Ka ji wahalallu, wai in wa qasarmu kishi,
Wata karuwa ta ce ban kurxi in gyara gashi,
Ko xan ten miliyan of dolas, ku kuna uquba."

Daga nan, sai ya karkata zuwa ga shuwagabannin addinai, na Musulmai da na Kiristan duka, ya nuna yadda suka shiga siyasa dumu-dumu, da kuma nuna yadda ake amfani da su ana cutar talaka, wato yadda suke fakewa a inuwar addini, su yi yadda bai kamata ba. Ya bayyana yadda ake ba su cin hanci don toshiyar baki. A baiti na 6:

(44) "Casa'in cikin xari na shugaban addinai na riqe su,
Ya kamata shuwagabannin addinai a je gida a gan su,
Yanzu wasu shuwagabannin addinai kwaxayi gare su,

Idan ka kama mulki na zamani, yanzu za ka gan su,
Talaka na ta ihu, wai me za na taimake su,
Ina da iyayen qasa, da mahukunta da ke wurinsu,
Babu yadda za ku yi, qarshe ku shiga azaba."

Shi kuwa Aminu Ala a waqar *Bubukuwa*, ya nuna cewa da irin abin da ke wakana, ana ta yi babu wata madosa, babu madogara ko alqibla, sai ya lissafo wasu ayyuka, ya nuna cewa gara a ce ya aikata su, ko ma mutuwa ta xauke shi, idan akwai rahama. Kamar yadda ya ce a baiti na 3:

(45) "Gudu da ba kuvuta ashe, ashe,
Gudu da ba tsira, ashe ashe,
Gudu da kwai halaka, ashe, ashe,
Gudu da ba nasara, ashe, ashe,
Gara nai kwanciya da shi, da shi,
Gara nai birgima da shi, da shi,
Gara nai barci da shi, da shi,
Gara ma mutuwa da shi, da shi,
In dai da dace, da qaruwa, bubukuwa."x 2

Ya ci gaba da farfagandarsa, yana bayyana dalilan da suka sa ya rubuta wannan waqa, wato ya duba ya ga shuwagabanni ba su tafiyar da mulkin yadda ya kamata, sun kauce hanya, sun bi son zuciya, ya zayyana irin waxannan shugabanni, kamar Kansila, Gwamnoni, Kwamishinoni, Ciyamomi da sauransu. Da haka ne ma, ya nuna cewa ai varayi iri-iri ne, sata ma ana yin ta, ta kowace hanya, kamar yadda ya nuna a baiti na 4:

(46) "Abin da ya sa ni tunzuri, na xora tsuwa cikin dare,
Na kasa bacci cikin dare, ina wasi-wasi na fanxare,
Batun hukunci nai nazari, da shi ya ka qagi falken dare,
Masu mulki daga Kansila, 'Yan-majalisa sun fanxare,
Kwamishinoni, Ciyamomi, ga Gwamnoni sun fanxare,
In suka saci haqqin jama'a, babu hukunci gare-gare,
Lallai varayi suna suka tara, an yi gudu da ba wurin zuwa."

Jibrin Jalatu, a waqarsa mai suna *Mafarkin Mulki II* ya bayyana irin yadda mahukunta ke qoqarin lalata mulkin qasa gaba xaya, dukiyar ba a tafi da ita yadda ya dace, sai dai su kwashe, su wadata kansu, da wanda suke so. Wato, fito da yadda suke qoqarin vata komai, da ma kashe qasar baki xaya. Ya zayyana quncin da 'yan Nijeriya ke fuskanta, don rashin adalai. A baiti na 5:

(47) "Nai masu tarnaqin baqar wahalata,
Duka qasa na barbazo matsalata,
Qadarar 'yan qasarmu na sace ta,
Makarantun qasarmu na lalata,
Burina kawai qasa na kashe ta,
Burina kawai qasa na kashe ta,
Sai mai cuta da zamba, zan ba mulki."

Sai ya ci gaba da magana kan buqatun 'yan Nijeriya na neman shugabanni na gari, adalai, masu gaskiya da riqon amana, waxanda za su yi kishin qasa, su kuma kamanta adalci, amma hakan ba ta samu ba. Sai waxanda ba su cancanta ba, su ne ke mulkin jama'a. A baiti na 6:

(48) "Suka ce tausayi, na ce ba mu gamu ba,
Suka ce jinqai, na ce ba mu haxu ba,
Kuma kishin qasa, ba za ai ba,
Mulkin gaskiya, na ce ba zan ba,
Kuma mai gaskiya, ba zai hau ba,
Kuma mai gaskiya, ba zai hau ba,
Sai marar gaskiya nake miqa wa mulki."

Haka kuma, a cikin waqarsa ta *Ku Yi Haquri*, ya kammala waqar yana mai gargaxi da faxakar da azzaluman mahukunta, da su sani cewa, duk mai zalunci ba shi da makoma mai kyau, ba zai shiga aljanna ba. Ya zayyana wasu laifuffuka, ya ce duk mai aikata su, ba zai samu rabo mai kyau ba, don haka gara a samu mafita tunda wuri. A abiti na 6:

(49) "A tuntuni tarkon matambaya de ikhwana,

Mai zalunci ba shi da fili aljanna,
Mai sata ba shi da fili aljanna,
Mai murxe zave, ba shi da fili aljanna,
Wasu ba su ibada, tun kan zave suka daina,
Ai nazari dai, don a lahira babu dabara."

AbdulAziz Ningi, a waqar *Rigar 'Yanci* ya ci gaba da fasalta siyasar Nijeriya, yana nuna yanayin mulkin dimokraxiyyar a karkace yake tafiya. Sai ya sake nuna cewa siyasar kamar dan wasu mutane na daban aka yi ta, don abin ya zama kamar gado, idan wannan ya sauka, sai ya ba wancan, kuma duk a qarqashin inuwa xaya. Wanda duk ba ya tare da su, ba za a dube shi da idon dimokraxiyya ba. A baiti na 5:

(50) "Sha'anin dimokraxiyyar, an mai da shi cuxi,
Fasalin a Nijeriya, ya zam kamar shinge,
Wadda bai cikin kewayen, sai dai a mar qage,
Motar dimokraxiyyar, tayarta na goge,
Tibinta zai bindiga, wasu wa'adi ya yi."

Sai ya ci gaba da faxakar da 'yan Nijeriya damarsu da 'yancinsu na zama 'yan qasa, da ma damar zaven wanda mutum ke so, wato ya bayyana manufar mulkin dimokraxiyya, wanda ke ba da 'yanci mai yawa, wanda ya bambanta shi da mulkin soja. Saboda haka, babu tilas kowa ya bi ra'ayinsa. A baiti na 6:

(51) "Manufar dimokraxiyyar, damar faxar kowa,
'Yancinka ne xan-adam, kai ra'ayin kowa,
In ba ka so babu tilas ko gaban kowa,
Ra'ayinka tamkar ka qone, har da ba kowa,
Duk faxarsu ba yi ba ne, ra'ayinmu sai mun yi."

Haka kuma Haruna Ningi a waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*, ya yi qoqarin bayyana saqonsa a fili, na nuna rashin amincewa kan tsarin mulkin ta zarce, sannan ya yi kira ga manyan qasa, masu faxa a ji, masu kuma goyon bayan ta zarce kamar su Gwamnoni, da Sanatoci, da Ministoci, da su miqa saqon jama'a zuwa ga shugaba Obasanjo cewa ba a yarda ta zarce ba. A baiti na 10:

(52) "Ga sautuna jama'a da Gwamnoninmu ku kai saqo,
To, ku zo Sanatocinmu, da refs-refs xinmu ku kai saqo,
Ku faxa wa Ministoci, su cije havarsu, su kai saqo,
Su faxa wa Obasanjo, mu kam ba mu yarda ta zarce ba."

Ya ci gaba da warware wa mutanen Nijeriya manufar ta zarce, yana mai kafa hujjoji qwarara da yake ganin tsarin bai dace ba. Ya nuna ko a tsarin mulki na qasa, ba a amince da tsarin ta zarce ba, don haka, abin ba mai yiwuwa ba ne. A baiti na 11:

(53) "To, batun daxa zarcewa, a son rai ma makaruhi ce,
Sannan a cikin tsarin mulki na qasarmu haramun ce,
To, bare daxa tursashi a kan jama'armu masifa ce,
To, ku gane bayanin nan, in kun qi ba za ku ci riba ba."

Ya nuna yadda aka yi qoqarin tursasa wa jama'a ta zarce, wanda kuma ya nuna bai yarda da tsarin ba, sai a kama shi, a xaure. Sai Ningi ya ce, shi dai ko me zai faru, sai dai ya faru, ba zai yarda ta zarce ba. A baiti na 12:

(54) "Wai wanda ya ce a'a, a kan ce Ribaxu ya kama shi,
In ba ya cikin gammen, ka sa makasanka su harbe shi,
Qarshe ko idan ya zo, mutum ba ya iya canza shi,
Ko za ka ci namana, zan ce ba mu yarda ta zarce ba."

A waqar *Mafarkin Mulki I,* Jalatu ya ci gaba da nuna yadda ake murxiyar zave, wanda jama'a suka zava daban, wanda kuma za a ba mulkin daban. Idan kuma aka kai qara a kotu, ba ta canza

zani, don su ma alqalan azzalumai ne. Ya kuma nuna cewa wanda ya bi gaskiya zai wahala, sai marar gaskiya ake so. A baiti na 7:

(55) "Ina mahukunta su ma sun biye halina,
A gama murxiyar zaven da akai, ina gida abu na,
A gama kai qara a kotuna, ni za a ban abu na,
Ka daina gaskiya a zahiri, sai ka zo mu zauna,
In ka qi ko, kullum kai kake a rana,
Domin a zahiri babu gaskiya kaf, a lamarina,
Gara ka zo mu zauna, in kuma ka qi, ka sha azaba."

Sai kuma ya zayyana yadda shuwagabannin ke damawa, ta yadda duk wani muqami ko wani mataki na mulki suke ke zavar wanda suke so, su ba shi ko da kuwa bai cancanta ba. Sukan yi hakan kuwa domin jin daxinsu da kuma samun damar handama da babakere. Duk wanda suka ba wa wani muqami, ba zai qi bin ra'ayinsu ba, idan ma ya sava, sai a karve daga hannunsa a ba wa wani. Don haka, duk wani mai faxa a ji da ke riqe da wani babban muqami, za a tarar akwai ra'ayina gwamnati a ciki. Ya nuna yadda ake kashe-mu-raba tsakanin shuwagabanni da mataimakansu. A baiti na 8:

(56) "Na zamo kamar xakin kura sai dai na jikina,
Ministan tsaro, ni zan naxa da kaina,
Ministan ilmi da lafiya, zan sa na wurina,
Ministan kuxi, ni ne zan naxa abu na,
Ministan sufurin jiragen sama, yana wurina,
Ministan ruwa shi ma, ni zan naxa da kaina,
Idan na sanya doka, kowanensu kar ya sava."

Ya ci gaba da zayyana yadda mahukunta ke cin karensu ba babbaka, yadda ake raba daidai tsakaninsu da mataimakansu, da nuna qarfin mulki da yin yadda rai ke so daga wasu daga cikin su. A baiti na 9:

(57) “Ministan ma’adanan qasa qwarai yana wurina,
Ciyaman fetur shi ma, zan sa na wurina,
Idan na tara duk gaba xayansu, zan ba su huxubana,
Arziqin qasar nan gaba xaya, mu voye kar mu nuna,
Zan ba ku fasentej mai yawa, in kun bi ra’ayina,
Wanda ya qi bi, zan sanya hukuma da ra’ayina,
Zan takura shi, gaskiya ta zame musiba.”

A waqar *Mafarkin Mulki II* ya ci gaba da jaddada yadda mahukunta suke qoqarin mamaye kowa da komi ta hanyar amfani da kuxi, don su mulki kowa yadda suke so, musamman waxanda suke riqe da wasu muqamai masu muhimmnci. A baiti na 7:

(58) “Sanatocin qasarmu na kama su,
In da ba kwaxayi, ni ke bin su,
Suka aje matsayinsu, na hau kansu,
‘Yayan banki na sa, na kashe su,
Na yi gidaduwa kamar burinsu,
Na yi gidaduwa kamar burinsu,
Ba mai ce da ni ka sauko daga kan mulki.”

Sai kuma ya bayyana siffofin macutan shuwagabanni, ya siffanta su, yadda da an gane su, za a shaida su, da yadda suke fankama da nuna isa da cikar isa ta zalunci. A baiti na 8:

(59) “Nai cuta qasarmu kwando-kwando,
Mamunguntan qasarmu dodo-dodo,
Kullum na fito a ce ga dodo,
Ni kuma na fi so, a ce min dodo,
Ni qiba, na yi tumbin kwaxo,
Na yi qibata kamar xan-kwaxo,
Waye wanda za ya raina ni a kan mulki.”

Haruna Ningi a cikin waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi* ya gargaxi jama’a cewa su daina sadaukar da rayinsu kan banza, ga wanda bai san darajarsu ba. Sai ka ji jama’a na cewa ai “baqar wane nake yi”. Shi kuwa zuciyarsa fari fat, kai kuwa ya bar ka da qunci da gaba tsakanin juna. Ya yi gargaxi sosai, a daina yin haka. A baiti 8:

(60) “Duk tsananin ra’ayi da adawa,
Kad da ka yarda su kai ka kushewa,
Duk wanda yai haka ya cika wawa,
Mai ce a kar ni saboda gwanina.”

Sai kuma ya faxakar da al’umma su duba yadda shuwagabannin suke mu’amala junansu. Ba za a ji wani tashin hankali a tsakaninsu ba, sai dai su magoya bayan ke yi. Sun mayar da mutane sakarkari. A baiti na 9:

(61) “Manyanmu kaf na siyasa ku duba,
Ba za ku ji su da zagin uba ba,
Ko su yi doki-in-doka a su ba,
Sai mu irin lamarin nan da quna.”

A cikin waqar *Hawaye* Ningi ya yi maganar samun mulkin kai a Nijeriya, cewa daga hannun Turawan mulkin mallaka. Sai ya nuna ai gara waxancan ‘yan mallakar da na yanzu, don na yanzu ‘yan ta’addanci ne, varna akwai suke tafkawa ba gyara ba. Babu kishin kai a tare da su. Ya ce yadda suke yi bai dace ba. A baiti na 8:

(62) “Mun samu mulki a gun ‘yan mallakar da,
‘Yan mallakar yanzu sun fi na da ta’adda,
Sun zare kishinsu, sun ce ba shadda,
An sa tunani kuwa Nijeriyata, iye.”

Ya ci gaba da nuna yanayin yadda ake tafiyar da mulkin Nijeriya, yanayin yadda ake tafi da rayuwar al’umma babu madosa. Tafiya ake yi, amma babu wurin zuwa, ana sauri babu hanyar fita. A baiti na 9:

(63) “Tafiya muke yi a kurmi mai itace,
Kuma ga dare, ga ruwa maqil a kwance,
Kuma ga macizan ruwa da na kan itace,

Ga babu mai toci ko sandar riqewa."

Haka, ya qara suranta siyasar Nijeriya, yana nuna a cuxe, a yamutse ake yin ta. An bar jama'a, maza da mata, yara da manya, kowa da kowa cikin qunci da rashin wadata. A baiti na 10:

(64) "Tafiyar da yara da manya ga su barjak,
Tafiya da yunwa da sanyi sun yi cancak,
Guzurin tuwon ma kari xaya ne kawai rak,
Ban san ta ya za mu je mu garin zuwan ba, iye."

AbdulAziz Ningi a waqar *Rigar 'Yanci,* ya jaddadawa mahukunta cewa yanzu fa babu yin yadda rai ke so. Don jama'a za su kasa, su tsare, su kuma raka quri'unsu. Mutane sun zage damtse, don ganin an ba wa wanda ya cancanta, don mahukuntan sun vata tsarin dimokraxiyyar gaba xaya. Ya ce haka a baiti na 7:

(65) " Ku masu qaunar naxi, bana babu mun farga,
A zuba, a zava, a kar, bana za mu ja daga,
Mu suturta jumhuriyar, damarmu ce danga,
Sun kar dimukraxiyyar, a qasarmu mucinga,
Tun tarihin duniya, ba a yin buhun qoyi."

Sai ya qara faxakar da shuwagabanni cewa damar mutum na nan , ta zavar abin da yake so. Su bar ganin sitiyarin mulkin na a hannunsu, su ce yadda suke so, za a yi, shugaba ba shi ke ba da rai ba, bare lafiya. Don haka, ba za a qara yin yadda suke so ba. A baiti na 8:

(66) "Duk wadda yai zai bari, har wadda bai zo ba,
Kuma shugaba bai yi ma, rai, dukiya, xa ba,
Ba wadda zai sa ka yin, ra'ayin da bai ma ba,
Kuma babu mai sa ka son mutumin da bai ma ba,
Wai don yana tutiyar, ya fi ka, sai ka yi."

A cikin waqarsa *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*, Haruna Ningi roqo ya yi zuwa ga al'ummar Nijeriya, a dage, a ga an rushe mummunan tsarin ta zarce, don ba za ya amfani al'umma da komai ba. Babu alhairi a tattare da shirin. A baiti na 13:

(67) "Na ce ya jama'a na qasa, Haruna na Ningi ina roqo,
To, idan jama'ar xazu wasu suka kasa isar saqo,
To, mu harhaxa kayanmu, mu salami mai tafiya tunqo,
Zamansu a mulkin nan, ba za ya zame mana hairan ba."

Sannan ya nuna cewa kada jama'a su fito a lokacin zave kwata-kwata, in dai aka ce zaven na ta zarce ne. Sai ya ce da al'ummar Nijeriya, a kawar da batun tsoro, don a cimma buri. A baiti na 15:

(68) "To, ku kauda batun zave, in dai ba a kyautata tsarin ba,
Sai mun yi su caccanza, sannan ba su ba mu dalili ba,
In dai muka sa tsoro, ba za mu rufe su da duka ba,
To, masu ta zarcen nan, ba za mu hana su zarce ba."

A waqar *Rigar 'Yanci,* AbdulAziz Ningi bai fasa ayyana wa mutanen Nijeriya 'yancinsu da damarsu ta zavo wanda ya cancanta ya jagorance su. Har ma ya yi kira ga jama'a a yi qoqari a wannan karon kada a yi zaven tumun dare, ya nuna duk juyin juya halin da za a yi, a jajirce, a tsaya kan manufa. Baiti na 9:

(69) "Ra'ayinka ne kar ka so, wani wadda bai ma ba,
"Yancinka ne xan-adam, ka qi wadda bai ma ba,
Damar ka zavo mutum, wadda bai da cuta ba,
Bana kar mu zavo mutane masu qeta ba,
Ko za a harbe mu ne, ra'ayinmu sai mun yi."

Ya ci gaba da tunasar da al'umma matsayin mahukunta, da nuna masu babu wata riba da za a samu idan an bi su, don ba tafarkin Allah suke bi ba. Shi ne yake faxakar da jama'a cewa a bijire wa tsarin shugabannin, tunda kansu kawai suka sani. A baiti na 10:

(70) “Mun kama bauta mu nai, kuma babu tsira ba,
Ba Annabawa ba ne, kuma ba Sahabbai ba,
Balle mu ce, za su kai mu zuwa ga tsira ba,
Ba wadda zai ma karatu, ba da koyo ba,
Don mi mike bin su, mui ta zama na hawi.”

Bai daina wayar da kan jama’a ba, yana mai faxakar da su al’amuran siyasa, musamman yadda ake tafi da mulkin a birkice. Ana jan al’umma a qasa, an mayar da su kamar bayi. Har gara ma lokacin bauta, da halin da ake ciki yanzu. Sannan ya nuna cewa an jarraba shuwagabannin a ga ko a dace, amma ba ta canza zani ba. Abin da suke yi ba kuskure ba ne, qeta ce da zalunci, kamar yadda mawaqin ya bayyana. A baiti na 11:

(71) “Mun bi su da, mun gwada, ba su bar mugunta ba,
Wasu sun bi, sun sake bi, ba su bar mugunta ba,
Duk wadda yai kuskure, in ba dagangan ba,
Bai sake yin kuskuren, in ba da qeta ba,
Ya za mu zave su, sun kuma mai da mu bayi.”

Haka a waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*, Haruna Ningi ya yi ta faxakar da al’umma munin ta zarce, ya nuna duk wanda ya goyi bayan hakan, idan musulmi ne, to bai san manufar addininsa ba, haka ma idan Kirita ne, bai san maufar Kiristancin nasa ba. Ya yi haka ne, don ya qara nuna qyamarsa kan tsarin ta zarce. A baiti na 16:

(72) “Duk wanda ya ce ta wuce, ku ce bai yarda da Allah ba,
To, idan a Musulmi ne, bai gane dalilin sallah ba,
To, idan a Kirista ne, bai san ma’anar gina coci ba,
Ai ni a mutuncina, gare su da bai wuce zagi ba.”

Ya yi maganar wasu gwamnoni da sanatoci waxanda suka qi bayyana ra’ayinsu a fili, wato ba su bayyana matsayinsu kan ta zarce ba. Sun tsaya tsaka-tsakiya abin su. A baiti na 17:

(73) “Da akwai Membas, Sanatas da Gwamnonin da sukai wayo,
A jiharsu ana wayyo, Abuja tana masu oyoyo,
Ba su kushe ta zarce ba, ba su ce mana eh ba ta ‘yan koyo,
Duk mai haka ko waye, bai girma a kwansituwansi ba.”

Sannan ya kira masu son ta zarce, waxanda ba su tsoron Allah, ya kuma qara kira da a bijire masu matuqar ba za su canza ba. A baiti na 18:

(74) "Duk wanda ta bar Allah, mu bar shi da wanda yake tsoro,
Amma mu sani duk ran da za ya kira mu wurin taro,
A cikin izinin Allah, mu taru da kanmu mu mar horo,
Mu gwada masa fau-fau cewa ba mu yarda ta zarce ba."

Ya ci gaba da maganar rashin kula da haqqin talakawa, don qasa babu tsaro, sata ta yi yawa, ko a hanya ba a bar mutane ba, ga masu tsaro amma a banza. Wato yana wayar da kai, a gane munin ta zarce. A baiti na 19:

(75) "To, idan ta tsaro ne dai, mun san ba ya tsare rayinmu,
Hanya ba mu tsere ba, a bi mu gidanmu a yanka mu,
Ga masu tsaro jingim, duk ya qi ya bar su, su kare mu,
Ga soja da 'yan sanda, har yau ba a bar tsare hanya ba."

A cikin waqar *Baubawan Burmi* Ala ya yi ta qoqarin faxakar da jama'a da kuma wayar masu da kai, don su nuna rashin amincewarsu ga tsarin mulkin da ke wakana, shi ne ma ya nuna cewa Allah Ne Ya ba shi ikon sanar da jama'a don su yi qyama ga mulkin. A baiti na 33-35:

(76) "Allah Kai Kab ban iko,
In qi abin gudu da fatar bakina."

(77) "Allah Kai Kab ban hikima,
In yi ragargaza da harshen bakina."

(78) "In faxakar gun al'umma,
Don su yi qyamata ga mulki na gadara."

Haka a waqar *Xaurin Gwarmai*, a karvin waqar, 'yan amshi, sun taya mawaqin, suna nuna goyon bayansa, don a ganinsu, mawaqin yana isar da saqon gaskiya. Don haka, suna roqon Allah Ya tsare Nijeriya da mutanen cikinta, suka ce:

(79) “Nai mubaya gun Ala, mai rushe shirin wawa,
Mai kira a kan a bi hanya da ba ta da gantsarwa,
Mai ragargaza da zalaqa da baitocin baiwa,
Mai bindiga, mai tanka da sautin harbawa,
Ilahu Kat tsare mu da sharri na duk mai cutarwa,
Mutum da aljani sulkina, tsare mu da cutarwa.”

A waqar *Mafarkin Mulki I,* mawaqin ya zayyana yanayin da mahukunta ke kasancewa, idan lokacin zave ya qarato, sai su shiga damuwa da takaicin miqa mulkin ga wani, don sun san abin da suka shuka, shi za su girba. Daga nan, za su fara tunanin wanda za su miqa wa mulki, tunda abin ya zama gado, sai su nemi na kusa da su, mai xabi’a irin tasu, wanda zai bi ra’ayinsu. Su naxa shi, ko da kuwa jama’a ba su so. Da haka ne, mulkin kama-karya ke zama da kafafunsa a Nijeriya. A baiti na 11:

(80) “Shekaru suna turawa, za a amshe mulki,
A lokacin rama da takaici, suka fara aiki,
Abin da na shuka, za ni girbe ina da aiki,
To, sai na hau tunani, shin wa za na ba wa mulki,
Mai handama da babakere, shi za ni ba wa mulki,
Tunda wani ya sauka, ya ba ni, tilas in qyale mulki,
Lallai ina da aiki, a lokacin na shiga uquba.”

Ya daxa fayyace yadda shuwagabanni ke tunanin yadda za su kasance idan babu mulki, domin sun san, sun bar baya da qura. Sai su shiga halin qaqa-ni-ka-yi, kamar yadda ya bayyana. A baiti na 12:

(81) “Abinci ban iya ci da yawa, kullum sai tunani,
Na gaza barci da daddare, kullum sai tunani,
Hawan jini da olsa, a lokacin suka mamaye ni,
Zuciya da vargon jiki, a lokacin sun yi rauni,
Aka ce da ni, saura kwana huxu a mamaye ni,
Ji nake kamar an, albishirin mutuwa gare ni,
Mulki babu daxi, ga shi nan ya zame uquba.”

Irin abin da ke wakana ya bayyana, na duk wanda ka xora a kan mulki, za a so ya yi yadda ake so, amma a kan samu wasu, su bijire, su qi yin yadda ake so. Daga qarshe, reshe ya juya da mujiya. A baiti na 13:

(82) "Wanda ya kama mulki, na ba shi sharuxxa bai riqa ba,
Ya ga ban da qarfi, ya ce bai yarda da ni ba,
Na kafa hukuma, baya can, in ba ku manta ba,
Yanzu ga hukuma, ita za ta ban musiba,
Wanda ni na kama da gaskiya, yanzu fa shi ya karva,
Yanzu ga shi nan, shi ne fa yake ban azaba,
Ka ga ma nadama, na kasance cikin musiba."

Ya bayyana abin da ke faruwa ga mahukunta bayan miqa mulki, ya nuna cewa talakawa na gudunsu, har daga baya su riqa nadama kan yadda suka aiwatar da mulki. A baiti na 14:

(83) "A lokacin da na yi nadama, kowa ya guje ni,
Wanda na bai wa muqamai, don mulki suka so ni,
Talaka tun cikin mulki ya guje ni,
Don saboda ba tsoron Allah, da tausayi gare ni,
Yanzu ga shi mulki ya qare, sai dai tsanani,
Talaka in ya gan ni, jifa ce yake gare ni,
Mulki babu daxi, ga shi ya zame musiba."

Cikin waqar *Rigar 'Yanci*, AbdulAziz Ningi ya ci gaba da kira ga al'umma da su bijire wa mulkin Gwamnatin Nijeriya, wanda ya nuna a matsayi na rashin adalci. Don haka, ba gudu, ba ja da baya, dole a yi yadda al'umma ke so. A baiti na 17:

(84) "Yau kaf cikin duniya, ko da a Turanci,
Shin ko da mai ba da, kyautar ransa har zuci,
Don daxaxawar waninsa, da nasa na qunci,
Juyi a Nijeriya, yau ba mu yin sakkaci,
Ko za a maishe mu toka, namu sai ya yi."

Wa'azi ya xan gabatar ga mahukunta, yana sanar da su nauyin da ke bisa kansu, yana kuma nuna masu aikin da ke gabansu. Ya nuna jama'a dai babu ruwansu. A baiti na 18:

(85) "Mu ba wakilai ba ne, mu ba jakadu ba,
Ba shuwagabanni ba ne, mu ba sarakai ba,
Mutuwarmu ko yau ta zo, mu ba mu tsoro ba,
Su ne, suke qinta, don sun san da horo ba,
Amma suke cin haqqinmu da dukiya nauyi."

Sannan ya ci gaba da wayar da kan jama'a da ilmantar da su haqqinsu dake kan shuwagabanninsu. Ya nuna akwai damar a yi masu biyayya, a ba wa mutum martabar da Allah Ya ba sa, amma ba a ce yi wa wani shugaba bauta ba, ko a ji tsoronsa fiye da Mahalicci, don kwaxayi. Yin hakan ya sava wa dokar Islama. Baiti na 19:

(86) "Bai xan adam martaba, bai zam da laifi ba,
Amma ka bauta masa, ba a ba ka dama ba,
Tsoronsa tamkar Maqagi, bai da rana ba,
Bai bar abin duk da bai, ya halatta kai mar ba,
Don son abin duniya, ka kauce ayoyi."

A cikin waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba,* Ningi ya ci gaba da ankarar da al'umma varnar da shuwagabanni ke aikatawa, musamman na wancan lokaci. Ba wani abin kirki suke yi ba. Don ya nuna varnar da yake yi, ta fi gyaran yawa. Idan an yi karo na uku kuwa, al'amarin sai dai Allah kawai. Baiti na 21:

(87) "To, a xau duka aikinka, a xau varnarka a auna su,
To, abin da ka vavvata, ya zarce wa'yanda ka gyara su,
Ko ban tava boko ba, mutum bai ce mani sususu,
To, a tara bayanina, a kan haka ban rasa hujja ba."

Ya bayyana cewa akwai wasu gwamnoni da suka goyi bayan ta zarce, suna nuna wa jama'a su yarda da tsarin, shi ne mawaqin ya xauke su a matsayin shashashu, don masifar al'amarin ta wuce misali. A baitin na 22:

(88) "Da akwai wasu gwamnoni sun sanya ta zarce cikin huhu,
Sun je su jihohinsu, sun ruxi wa'yansu da huhuhu,
To, suna masu ihu wai, ta zarce kai ka ji shashashu,
Ai rashin ilmi ne duk, domin ba su hangi bala'in ba."

Ya isar da saqo zuwa ga mahukunta cewa mulkin fa ba gado ba ne, jujjuyawa ake yi, da ba a yin haka, da su ma ba su samu ba. Don haka, babu maganar ta zarce, sai dai a zarce lahira. Ba su adalci, bare jama'a su ji kunyarsu. A baiti na 23:

(89) "In ban da ana sauka, a bai wa waxansu su xana su,
Ba za ku yi mulkin ba, bare ku mayar mu kamar kumba,
To, babu ta zarcewa, idan ba dai a kiyoma ba,
Ba ku tsai da amana ba, to, mu ko ba za mu ji kunya ba."

Bai gaza ba, ya ci gaba da sanar muqarraban ta zarce, cewa tsarin nan dai da aka saba, kuma aka sani, shi jama'a ke so a ci gaba. Idan kuwa ba a yi hakan ba, al'umma za su yarda na tsarin ta zarce ba. Don haka, a je zuwa, xan halak ka fasa. A baiti na 24:

(90) "Wa'adinmu na da na nan, idan ka yi sau biyu shi kenan,
Ba a dagula tsarin ba, ka ce mana ba ka cikin wancan,
In ba ka cikin wancan, to mu kuwa ba mu cikin wannan,
To, idan ba ka fasa ba, mu ma ba mu yarda mu qyale ba."

Haka, a waqar *Baubawan Burmi,* ta Aminu Ala, 'yan amshi sun taya shi koke kan aibobin da mahukunta ke tafkawa, inda suke nuna Allah Na nan, Zai yi maganin komai.

(91) "Ala mai faxxakarwa,
Daina kukan kokawa,
Allah Ne Yake sakawa,
Sannan Shi Ke cirewa,
In Ya so Zai canzawa,
Ba mai ikon hanawa."

A cikin waqar *Hawaye,* Haruna Aliyu Ningi ya zayyana rashin abin qwarai, abin kirki a Nijeriya. Ya nuna cewa qasashen da ba su kai Nijeriya ba, wasu ma an sa masu takunkumi, ga rashin kwanciyar hankali, amm duk sun xarar wa Nijeriya a komai da komai. Shi ne yake cewa me ya kawo hakan ne. Ya ce hakan a baiti na 12:

(92) "Wasu sun rabe ma amma duk sun wuce mu,
Wasu na ta yaqi, amma har sun xara mu,
Wasu har da takunkumin ma sun wuce mu,
Shin me yake faruwa Nijeriyata, iye."

Ya yi qoqarin sanar da mutanen Nijeriya matsalar qasarsu, inda ya nuna cewa abin da ke damun Nijeriya ba qaramin al'amari ba ne. Da wuya ma ta yi tsawon rai a ganinsa. A baiti na 14:

(93) "Amsarki na san ta ba sai kin faxa ba,
Ciwon da ke cin ki ba qarami ba ne ba,
Ranar da zai so ki ban ga tana zuwa ba,
Ni kam ina jin da qyar in za ki rayu, iye."

Ya ci gaba da bayyana matsalolin da Nijeriya ke fuskanta, don rashin shuwagabanni adalai. Ya nuna kwarafshan shi ne babbar matsalar Nijeriya, shi ya kawo tavarvarewar komai a qasar nan. A baiti na 15:

(94) "Mamarmu Nijeriya ciwo take yi,
Shin polio ko diyabetis take yi,
Sida take, koko dai kwalara take yi,
Ai fa corruption ina jin shi take yi, iye."

A waqar *Mafarkin Mulki I* Jalatu ya nuna qyamarsa ga mulkin da ke wakana, inda ya faxa wa jama'a cewa mafarkin mulki ya yi, ba mulkin ba ne da gaske. Ga shi kuma bai yi adalci ba. Ya nuna cewa ya kwanta da yunwa ne, shi ya sa hakan ta faru, a baiti na 15:

(95) “Kar ku manta cewa cikin mafarki na naxa mulki,
A lokacin na kwanta cikina fa, babu girki,
Ga shi ba maqota, ba mata, da za su ba ni girki,
Sai na hau tunani, shin a ina, za ni samu girki,
Sai na kama barci, tunda babu inda zan ci girki,
Sai na kama mulki a mafarki, kuma ban da kirki,
Kafin na kwanta bacci, sai da na sha baqar uquba.”

Ya kammala waqar, yana mai qara tunasar da al’umma cewa mulkin da ya gudanar ba da gaskiya ba ne, ya kuma qara nuna qyamarsa a fili, da kuma fatan Allah Ya taimaka a fita daga qangin wahala. A baiti na 16:

(96) “Kafin na bar mafarki, sauro ne ya mamaye ni,
Kiran sallah ne, na jiyo muryar ladani,
Sai na xauki buta, a lokacin na samu sukuni,
Nai alwalla da jam’in salla wanda babu muni,
Nai istigfari ga Rabbana don Ya yafe ni,
Ya cire man zunuban da ban sani, da wanda nas sani,
Allah Ka taimake mu, Ka raba mu da baqar uquba.”

A waqar *Mafarkin Mulki II,* kuwa ya kammala waqar da nuna yadda sauran muqarrabai na Gwamnati kamar sarakuna, da kwamishinoni, da sanatoci da sauran jama’a baki xaya ke bijire wa manyan idan tura ta kai bango. Sai su qi amincewa da duk wani tsari nasu, ba su yi masu fatan alhairi, kowa canji yake so. A baiti na 11:

(97) “Mai murxiya ya ce min ta kife,
Sanatoci suna so ta kife,
Qusoshina suna so ta kife,
Sarakunan qasa suna so ta kife,
Talakawa sun fi so ta kife,
Talakawa sun fi so ta kife,
Tunda ina ba su wahala a kan mulki.”

A waqar *Rigar ‘Yanci* ta AbdulAziz Ningi, ya ci gaba da ilmantar da mutane kan matsayin shuwagabanni a wurinsu, inda ya nuna jama’a su kasance masu biyayya a gare su, idan sun

zamanto masu gaskiya da riqon amana. Idan kuwa suka sava wa dokokin Allah, dole ne a bijire masu. Shi ne Ningi ya bayyana a baiti na 20:

(98) "Ladabi, biyayya da kyau, in ba rashin gaskiya,
Za kai wa babban mutum, mai son faxar gaskiya,
Ra'ayinka ko naka ne, ba mai yi ma danniya,
In shugaba dole ne, in yai rashin gaskiya,
Ko shi yake ci da kai, ka canza hanyoyi."

Bai daina kira ba ga xaukacin al'ummar Nijeriya, yana ankarar da su, su lura, su gane, kada a sake amincewa da tsarin danniya da yin yadda aka ga dama, musamman yin murxiyar zave. Ya ce a fito a yi bore, a nuna an san 'yancin kai. A baiti na 21:

(99) "Jama'a ku zo nai kira, ra'ayinmu sai mun yi,
Don me a Nijeriya, za a mai da mu bayi,
Bana ba mu qaunar naxi, kuma lokaci ya yi,
Duk wanda zai murxe zave, mu qona tayoyi,
Shi ne dimurkixiyyar, damarmu sai mun yi."

Ya nuna ba za a hana jama'a tofa albarkacin bakinsu ba, matuqar an zalunce su. Wanda aka zalunta dole ya koka. Wanda ya yi kuskure kuwa, tilas a gyara masa, a sanar da shi kuskurensa. A baiti na 22:

(100) "Ba yadda za ai kashi, bai zam kamar gyara,
Wadda an yi mai zalu kam, tilas ya kai qara,
Duk wadda yai kuskure, tilas a mar gyara,
An xaura aure, waliyyai na jiran gara,
Wasu sun tsaya kan kwana, an toshe hanyoyi."

A waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*, Haruna Aliyu Ningi, ya ci gaba da tunzurar da mutan Nijeriya, yana farfaganda, yana qoqarin sauya masu ra'ayi, su farga da zaluncin mahukunta da nufinsu na makirci da qulle-qullen gaba tsakanin qabilun da al'ummomin Nijeriya. Sai ya yi kira ga 'yan Nijeriya, da a lura da haka, a zama da haxin kai. A baiti na 27:

(101) “In za su yi makirci, wutar fitina suka kunnawa,
Da faxa ba qabilanci, da na addinai suka hurawa,
To, muna kashe kayi su, tsarinsu kawai suka gyarawa,
Mu fahimta mu bar gaba, in kun qi ba za mu ci riba ba.”

Bai fasa cewa kada ta zarce ba, duk ya san za ta yi wa wasu daxi ba. Ya nuna rashin amincewarsa, kuma dagewa kan manufar ba za a yarda a canza tsarin ba. Da kuma tunasar da shugabanni cewa, ba a kan haka aka zave su ba. A baiti na 28:

(102) “Na san wasu ba su son, mu ce ba mu yarda ta zarce ba,
Ce hakan kuwa tilas ne, a ce da mijin iya ai baba,
In dai sake tsari ne, ba za mu biye ku, ku sava ba,
In dai a ta zarcewa, da tun asali ba ku rantse ba.”

Haka kuma, ya nuna a matsayinsa na xan qasa, dole ya nuna kishinsa. Ba zai zama da irin halin shuwagabannin zamanin nan ba, masu rashin gaskiya da amana. A baiti na 29:

(103) “In zan yi gadara ai, dole in yi da qasar nan ne,
In zan gwada kishina, to za ni gwada wa qasar nan ne,
Har ban tava mulki ba, in kare qasarmu farilla ne,
Ba zan ci amana ba, ba zan biye masu ta zarce ba.”

AbdulAziz Ningi a waqarsa *Rigar ‘Yanci,* bai gaza ba, sai da ya qara fasalta yanayin siyasar Nijeriya. Ya yi maganar cewa, duk wanda zai gyara tsarin mulki zuwa cancanta, sai ya yi shiri, shiri na musamman, tare da gagarumin yaqi, don gyara qasa baki xaya. A baiti na 23:

(104) “Yanayin dimurkixiyyar, ya canza ‘yar lale,
Duk wadda zai yai shirin, zai zo da xan qyalle,
Ko da kamar hankicif, zai zo da xan qyalle,
Don goge dattin da, da za mu zuba cikin talle,
Don gyara Nijeriya, bana lokaci ya yi.”

Ya ci gaba da faxakar da shuwagabanni, da yi masu nuni da cewa duniya fa ba madauwama ba ce, yadda suka xauka, ba haka abin yake ba. Duk yadda giyar mulki ke xibarsu, wasu sun ma yi

fiye da haka kafin su, kuma sun wuce. Yana dai nuna masu, duniya masakin kunu ce, don su sha a hankali. A baiti na 24:

(105) "Ita duniya hira ce, wasu har da tabarma,
Cin duniyar ya musu, sun xora bargo ma,
Sun shimfixa, sun baje, kar wadda zai hau ma,
Su ji suke, sun haye, sun tara mai dama,
Da can fa kamun ku yi, wasu sun riga sun yi."

A waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba,* Haruna Ningi ya ci gaba da nuna aibun ta zarce, don ba zai yi wa masu son ta zarce waqa ba, ballantana jama'a su ji, don suna qyamar tsarin. Yin hakan ba shi da riba a gare shi. A baiti na 30:

(106) "In za na yi waqata, ba zan yi wa masu ta zarce ba,
Domin kuwa al'ummar qasarmu ba za su ji waqar ba,
To, abin da suke qyama, ba zan yi ba ya zama min riba,
Kai mu faxi da ku tare, mu tashi ba zan sake hanya ba."

Ya nuna maganar ta zarce babu ita, a ma kawar da ita. Duk yadda za a yi ma, ba za a fasa adawa ba. A baiti na 31-32:

(107) "To, ku qyale ta zarce tun manya ba su fara kashedi ba,
To, idan suka fara, mu yaransu ba za mu ji shakka ba,
Mu rugurguza kowaye, bai amsa abin da ya dace ba,
Harka ta butulci ce, mu ko ba mu gaji butulci ba."

(108) "Tura ta kai bango, kun ganta amma ku haqiqance,
Wai ko da tsiya ku dai, ku sake zama a guri qwace,
Sai kun gama holoqo, da cin zarafinku a susuce,
Ko kun hana jin waqen, ba za ku hana mu adawa ba."

Ya yi maganar son kai da mahukunta ke yi. Ba su damu da mabiyansu ba, sai lokacin zave ya zo, hankali ya tashi, a ximauce, a ji kunya. A baiti na 35:

(109) "Son kanku kuke sosai, ba kwa kula wanda kuke mulka,
Sai kun ji dirin ganga, an ce kun yi kusan sauka,
Duk sai ku dubulbulce, ku fara abinku kamar hauka,
Ya za a yi ne nema, a ce ba za ku ji kunya ba."

Haka a waqar *Rigar 'Yanci,* AbdulAziz Ningi ya qara zayyana halin mahukunta, ya nuna yadda suke son kansu, ba su qaunar su ga, ko su ji wani yana neman irin muqaminsu, sun manta komai na Allah. A baiti na 25:

(110) "Su ji suke sun buge, hagu har zuwa dama,
Kuma ba su qaunar a ce, wani ma yana nema,
Wata ran da ku za a je, roqonsu alfarma,
Don lokacin ba ku yi, kun tsufa ga girma,
Allah Yake ba mutum, in lokaci ya yi."

Ya ci gaba da yin gargaxi da nasiha ga shuwagabanni, cewa fa an yi dubu kafinsu, wasu sun yi zamani sun wuce, sun kuma kyautatawa al'umma. Sai tunawa da su, da fatan alhairi a gare su. Shi yake nuna gara ma su, sun aikata aikin hairan, don shi ya fi gare su. A baiti na 26:

(111) "In ba a xauke gula, ku ma ba kwa hau ba,
Na gabanku da sun riqe, ku ma ba kwa zo ba,
Sun fi kuma kyautatawa, ba varayi ba,
Kuma ba su qyashi da qetar qulla gaba ba,
Yau ga shi duk sun tafi, sauranku awowi."

A waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*, Haruna Aliyu Ningi ya ci gaba da isar da saqo zuwa ga manyan qasa kai tsaye cewa a bar maganar ta zarce, ya bar mulkin an gaji da shi haka nan. Ya sauka kawai, canji ake so. A baiti na 36-37:

(112) "Tsuntsun tsuru tsurunku qasarmu ashe muka ba zave,
Mun ba shi ta zarce da, amma bana dole mu mar zobe,
Ko ya iya aikin ma, ya a je shi ya huta a xan kurve,
Ya a je mana mulkin nan, domin ba mu yarda ta zarce ba."
(113) "Ko kun iya aikinmu, irin haka dole ta vata ku,
Ku bari wa waxansu su yi, domin kuwa kun gama aikinku,
Magana ta ta zarce ce, ta sa jama'a suka kushe ku,
Ai ko a kiyoma ne, waxansu ba za su qi canji ba."

Qara nuna bijirewarsa ga tsarin ta zarce, babu gudu, ba ja da baya. Komai za a yi ba za a yarda a zarce ba. A baiti na 38-39:

(114) “Ki jani mu je ganga, Haru in barbaza baitina,
In biyo ta qasar nan kaf, domin in gwada masu ‘yancina,
Duk wanda ya tanka min, in vangare kansa da dutsena,
Ko biyo ni mu ce Olu, mu kam ba mu yarda ta zarce ba.”

(115) “In ka cire gwamna don ya ce ba su yarda ta zarce ba,
Ka qwace muqami nai, amma ka sani ba ka zarce ba,
Ko ka baza tsari NASS, ba za ya saka ku, ku zarce ba,
In su suka qyale ku, mu kam ba mu yarda mu qyale ba.”

A waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi,* Ningi ya yi kira ga Hausa Fulani gaba xaya, yana nuna masu matsayinsu a idon shuwagabanninsu. Yaya ba su neman jama’a, sai in wuya ta zo. A baiti na 14:

(116) “Zan yi kira na Fulani da niyya,
Don yanzu mu aka qyale a baya,
Sai za ta vaci ake mana gayya,
Mu ko, mu zo mu, mu rarraxe juna.”

Ya bayyana muhimmancin waqarsa, duk da ya san ba za ta yi wa wasu daxi ba. Amma idan aka dubi al’amarin da idon basira, za a gane muhimmancinsa. A baiti na 15:

(117) “Ce waqa nakan yi da niyya da qarfi,
Wa’yansu sukan ji kalamin da zafi,
Amma idan nazarinka da zurfi,
Za ka fahimci salama a batuna.”

Ya ci gaba da bayyana laifukan mahukuntan, da kuma nuna son kansu kawai suke yi. Ya nuna yadda suke qyamar mutane, sai in wuya ta zo, sannan ake ganinsu. Da sun ci moriyar ganga, su yar da kwaurenta. A baiti na 17:

(118) “Ba za ka gan su a qauye ba nan ma,
Sai dai idan quri’a za su nema,
In kun saka masu, sun samu dama,
Da za su saka ku a wayyo ina ma.”

A cikin waqar *Rigar 'Yanci,* AbdulAziz Ningi ya yi gargaxi, yana mai nuna girman Allah da buwayarSa, ta yadda yake yi wa mutum ni'imomi, idan Ya so kuma ya karva. Ya nuna komai dai na Allah ne. Ya ce a baiti na 27:

(119) "Huwa Rabbi Mai zamani, ba yadda bai yi ba,
Ranar zuwa duniya, zir babu wando ba,
Wani na gani, sai a qarshe zai makance ba,
Wani ko yana ji, a qarshe bai da kunne ba,
Yanayin zaman duniya, an ba da ayoyi."

Ya kammala waqar, da nuna darajar da Allah Ya yi wa mutum. Sai ya sake komawa a kan manufarsa, yanuna mulkin Nijeriya na son gyara sosai, gyaran kuma dole ne, don lokaci ya yi. A baiti na 28:

(120) "Amma mutum martaba, a cikin halittu ma,
Ko da zaman duniya, an ba da ayoyi,
Yatsunka kwai qanqane, kuma har da mai girma,
Don ci da kai, sha da kai, ma dole mui fama,
Gyaran dimurkixiyyar, bana lokaci ya yi."

A waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi,* Ningi ya bayyana wa jama'a irin shuwabannin da ya kamata su zava. Ya nuna kada a zavi masu varin kuxi, don ba na kirki ba ne. Ba za su amfana jama'a da komai ba. Sai varna kawai. A baiti na 18:

(121) "Wanda ya zo shi siyasa da kurxi,
To, kar ku yarda da shi bai da daxi,
Zai zo da masu zalama da kauxi,
Su za su ke maku kunnin ashana."

Ya bayyana yadda mahukuntan ke damawa da cin karensu babu babbaka. Su wadata kansu da iyalensu, su manta da al'ummar da suka zave su. A baiti na 19:

(122) "Qauye idan ka ga yayi da danga,

Shi ko gidansa da kyau ga katanga,
Sai ka ga wani gidan babu salga,
Shi ko a nasa masan, sai ka kwana."

Sannan ya yi kira ga dukkan jama'a cewa kada a zavi azzulaman shuwagabanni komai quncin da ake ciki. Ya nuna a kawar da kwaxayi, a bar su da kayansu. Akwai hanyoyin samu da dama. A baiti na 23:

(123) "Duk wahala da talauci ku gane,
Kada su sa ku, ku bi su ku manne,
In dai kana maganar arziqi ne,
Qyale su, je ka, ka samu a gona."

A cikin waqar *Hawaye* Haruna Ningi ya fito wa mutanen qasar nan matsaloli da cututtukan qasar waxanda ke hana ta ci gaba. Ya ce akwai cin hanci da rashawa, ga rikicin addini da na qabilanci. Ga kuma karya dokokin qasa da su manyan ke yi. Su ke yin dokar, su kuma hau kanta su karya ta. A baiti na 16:

(124) "Rashawa tana nan, da cin hanci yana nan,
Rikicin qabila da addina yana nan,
Ga cin amana da son kayi yana nan,
Ga karya dokar qasa, gun masu doka, iye."

Bai gaza ba dai, ya qara zayyano matsalolin qasar, yana nuna yadda ake yin gurvatacciyar siyasa, ta ta'addanci, ba rigar 'yanci ake sa wa ba. Ga sace-sacen jama'a, an mayar da rayuka kamar na qwari. Ga cututtuka ba a kula da lafiyar mutane. To, yanzu 'yan Nijeriya murna za a yi, ko kuwa kukan matsalolin da ke damun mutane. A baiti na 17:

(125) "Kuma ga siyasar ta'addanci tana nan,
Ga sace-sacen mutane ba a bari ba,
Cututtuka barkatai kuma ba a kula ba,
Murna kike mama, ko kuka kike yi, iye."

Haruna Ningi a waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba*, ya yi magana kai tsaye zuwa ga uban qasa, ya qara nuna rashin goyon bayansa kan ta zarce. Ya bayyana makircinsu na son vata jam'iyya. A baiti na 40:

(126) "To, ki ja mu, mu je ganga, domin mu kawar da Obasanjo,
Ko za a yi girki na, ai dole mu rusa faxar Ojo,
Ba su bar jam'iyya ba, sun sa ta qilu da rawar banjo,
Maganar da nake yanzu, har yau ba su rarraba kayi ba."

Ya daxa nuni ga shugaba, yana qara jaddada cewa babu maganar ta zarce, qasa baki xaya babu mai goyon baya, daga 'yan Kudu, har na Arewa xin. Kuma shi kaxai ba zai iya zartarwa ba. A baiti na 42:

(127) "Tsoho haquri ne dai, sai ka yi, ka daina baqar gaba,
To, abin da ka quqqulla, ba zai tafi yanda ka shirya ba,
To, mutan kudu ba sa so, arewa kakaf ba mu yarje ba,
Ai hannu xaya ba zai xau, abin da yake rufe qofa ba."

Ya bayyana cewa duk wanda ke son ta zarce, ko ma waye, komai muqaminsa, a tsige shi daga muqamin nasa. A baiti na 43:

(128) "Duk wanda ya sanya hannu harka ta, ta zarce nuna shi,
Imma a wakili ne, imma Sanata ne a tsige shi,
Ko da kuwa Gwamna ne, ku bi shi gidansa ku turke shi,
Mun fara ganin doka, a kansu ba za ta yi aiki ba."

Mawaqin ya nuna yadda mahukunta ke karya dokokin qasa, ga shi suke tsarawa, kuma su karya su, musamman a kan tsarin ta zarce. Sai maganar inda ta zarce ta samo asali, da ya bayyana daga Kano, ta wurin wasu hamshaqai. A baiti na 44-45:

(129) "Su za su yi wo doka, su za su bi kanta su taka ta,
In kotu ta ce ga shi, su share batunta su karya ta,
Ta yanke hukunci yau, an ce mata gobe ta qaryanta,
Sun xau shari'a wasa, in dai ba ta yarda su zarce ba."

(130) “Ni na ji ta zarcen ma, an ce a Kano aka soma ta,
Da akwai wasu hamshaqai, wa’yanda suke wa kuxi bauta,
Hujjarsu ta jari ce, sun ba da kuxi aka soma ta,
To, da ku da Kanon ga ku, don ko ba su yarda ta zarce ba.”

Su ma Alarammomi da Fastoci, bai bar su a baya ba, sai da ya qwalla kira a gare su, yana mai jan hankalinsu, suna gani za a qaddamar da ta zarce. Sai ya nuna su ma su ba da ta su gudummuwar, su yi addu’ar rushe ta zarce. A baiti na 46:

(132) “Ina Alarammomi, ina addu’arku ta juya ne,
To, ina kuna Fastoci, ina addu’arku ta sauya ne,
To, wutar fitina ga ta, kuna kallonta, kuna zaune,
Ko kun ci kuxi ne ne, ba za ku haxa su da Allah ba.”

Jami’an tsaro ma bai bar su a baya ba, sai ya yi kira a gare su, yana nuna masu varnar da ake yi, suna gani, amma ba sa cewa komai. Ya kuma faxakar da su, halin-ko-in-kula da Gwamnati ke nunawa a kansu, musamman idan sun aje aiki. A baiti an 47:

(133) “Sai soja da ‘yan sanda, su ne suka yarda ku kare su,
Sun vata qasar nan kaf, kuna kallo kuka qyale su,
In za mu fito mu faxa, su sa ku kashe mu, ku kare su,
Ku gama, ku yi ritaya, ba za su biya ku na fansho ba.”

Ya ci gaba da zayyana manufar ta zarce, tare da suranta halin masu son ta zarcen. Ya nuna cewa da sun ci moriyar ganga, sai su yarda kwaurenta, shi ne ya kafa hujja da kes xin Tafa Balogun. A baiti na 48:

(134) “Sun xauki mutum ganga, da sun ci rabonsa su ya da shi,
Tsarinsu ya su ne rak, in ba ka cikinsu, su ma qyashi,
Ku ga Tafa Balogun dai, ku xau kes xinsa ku duba shi,
In bai isa aya ba, ba za ku fahimci ta zarce ba.”

Ningi ya fito da tsananin qiyayyarsa a fili, don ya yi kira zuwa ga bore da tawaye ga shugaba Obasanjo, har ya nuna zai sadaukar da rayuwarsa, zai jagoranci tawayen, don ya yi kira ga duka ‘yan Nijeriya da fito, a nuna qiyayya. A baiti na 49:

(135) “Ku faxa wa Obasanjo in ji ni Haruna ya bar ture,
Na saddaqa rayina in jagoranci a mar bore,
Zan cewa qasar nan kaf, cikin kowanne irin yare,
Ku fito mu jajirce, a kan ba mu yarda ta zarce ba.”

Bai daina bayyana manufarsa ta qin ta zarce ba, don ya ayyana cewa duk mai son ta zarce ya cancanci kisa, don ba wani abin arziqi ba ne ta zarcen. Ya nuna manyan qasashe kamar Amurka, ba su yarda tsarin ta zarce ba, sai Nijeriya a ce za a yi mana dole. Don haka, bore da bijire wa tsarin ta zarce ya zama dole. A baiti na 50-51:

(136) “Duk wanda ya zo zance na ta zarce garinku, ku jefe shi,
In ya qi ya tsere ma, dama aka ba ku, ku tsire shi,
In ya mutu shi kenan, ai ya tafi ya yi asara shi,
Domin ba mu fara ba, sannan ba mu yarda ta zarce ba.”

(137) “In ban da mutanen nan, rikici suka shirya su qulla ba,
In dai iya aiki ne, sun san ba su kayya Amurkan ba,
Ba su nemi ta zarce ba, sai ku da ba kui mana aiki ba.”
Ai dole mu ma bore, domin ba ka kai ya qasar nan ba.”

Ningi ya nuna ai ga manyan qasa na kallo ta zarcen ba ta dace ba, amma don kwaxayi, da rashin kishin kai, ba su nuna ba ta cancanta ba. Tunda haka ne, sauran jama’a su fito, qwai da kwarkwata, a bijire wa tsarin ta zarce. A baiti na 52:

(138) “Manya na siyasarmu da manyan soja suna zaune,
Duk ba ku da kishi ai, burinsu su tara kuxi tare,
To, dole qanananmu, mu kare qasarmu zaman tare,
Mu zubar da jini babba, ai gara a ce ba ta zarce ba.”

Ningi ya qara faxakar da ‘yan Nijeriya mugun nufin ta zarce cewa abin zai shafi kowa da kowa, don haka a haxa kai, kada a amince wasu ‘yan tsiraru su jefa qasa cikin bala’i. Baiti na 53:

(139) “Maganar ta qasa ce kaf, ba wai ya wa’yansu qabila ba,
Maganar haxa kayi ne, ba wai maganar wani sashe ba,
Gyaran da kuke kwaxayi, ba zai yiwu har ya yi aiki ba,
Burin wasu ba zai sa, a sanya qasarmu a yaqi ba.”

Sai ya isar da saqo zuwa ga masu ganin cewa don ba a ba shi cin hanci ba, shi ya sa ya rera wannan waqa, ya bayyana masu cewa shi babu ruwansa da irin wannan harka in dai ta ta zarce ce. A baiti na 54:

(140) “To, wa’yansu suna ce wai, ba a bani abin ihisani ba,
Na yarda da mai waqe, ba zai qi abin ihisani ba,
Amma ihsanin in ba za ya raba shi da hanya ba,
Kun san fa ta zarcen nan, samsam ba ta sadu da hanya ba.”

Daga qarshe ya kammala waqar da nasiha da gargaxi zuwa ga shugaban qasa, cewa jiki magayi, kuma kowa ya qi ji, ba ya qi gani ba, a yi hankali kada allura ta tono galma. Babu maganar ta zarce. A baiti na qarshe, na 55:

(141) “Kowa ya ji shi ke nan, kowa ya qi jinmu ku shaida mar,
To, jiki magayi ne ai, ku ce na jikinsa su nuna mar,
Magana ta ta zarce dai, ya sani birki aka taka mar,
Nan zan rufe waqata, jama’a har ban gama sharhin ba.”

A cikin waqar *Hawaye* Haruna Aliyu Ningi ya sanar da Nijeriya cewa ‘yayanta ne suka sanya ta halin da take ciki, sun sake mayar da ita bauta. A lokacin mulkin mallakar an sha kashi ballantana irin wannan hali da mutanen Nijeriya suka jefa ta ciki. A baiti na 19:

(142) “ ‘Yayanki dai yanzu sun mai da ke bauta,
Bautar fari ma da ya kika sha bugunta,
Balle baqi, mai baqar aniyar mugunta,
Shi ne na ce mama ba murna kike ba.”

Ya rattabo wasu jiga-jigan ‘yan siyasar qasar nan, yana kewarsu. Yana nuna yadda suka sadaukar da rayuwarsu don ci gaban Nijeriya. Da suna da rai, da Nijeriya ba ta tsinci kanta a yanayin da take ciki ba. A baiti na 20:

(143) “Allah jiqan Gamji Sardauna iyaye,
Da Tafawa Valewa da Azikwe, iyaye,
In na tuno Murtala sai nai hawaye
Sun saddakar da ransu don Nijeriya ne, iye.”

Ya rufe waqar tare da ci gaba da zayyano hamshaqan Nijeriya, waxanda suka shuxe.Yana bayyana cewa su masu son qasa da kishinta ne, ba su nuna qabilanci. A baiti na 21:

(144) “Ba za ni mance Aminu Kano ba baba,
Da su sir Akintola shi ma bai haye ba,
‘Yan son qasa ba qabilanci suke ba,
Nan zan rufe tambarin kukan iyata, iye.”

A waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi* ya yi horo da hani da ta’addanci don kada a vata zumuncin juna. Don duk shugaban da ya ce ka yi haka, to ba shugaban qwarai ba ne, kada a zave shi. A baiti na 10:

(145) “Zan so muke tuna bayanmu cancan,
Mutum kar mu vata zumunci na tun can,
Wanda ya ce maka je sari wancan,
Kadda ka yi haka shi ne batuna.”

Ya ci gaba da nuna wa jama’a cewa idan ta’addanci shuwagabanni ke so a yi, to su yi da kansu. Su daina amfani da jama’a, alhali kuma ba su amfana masu komai. Haka suke saka mutane cikin wahala, kuma ba za su san halin da ake ciki ba, ko sun sani ba za su taimaka ba. A baiti na 11:

(146) “Shi in ya je shi, ya sara da kansa,
Ai zai fi kyau yai da kayinsa fansa,

Zai je ya saka a xaki da qusa,
Shi ko ya tai da iyali su kwana.”

Bai daina faxakar da al’umma ba, yana tunzura su, yana nuna masu laifukan shuwagabanni, yadda suke jefa mutane cikin bala’i, wanda daga baya abin zai kai su ga nadama. A baiti na 12:

(147) “Za kai abin bisa izza da girma,
Sai daga baya ka fara nadama,
Sai wanda kai masa aikin ya ce ma,
Shi ba ruwansa da wannan ta’asa.”

Ya kammala waqar da gargaxi da jan kunne, tare da jaddada manufa. A baiti na 28:

(148) “Saqon da ke gaba sai ya fi nauyi,
In dai kuka qi bayanin da nayyi,
Allah Ka ba ni sukuni da rayi,
Nan zan rufe haka sai wata rana.

## 4.12 Addini

Ire-iren waqoqin nan na zamani, sukan tavo maganar addini a fakaice, don su karkato da hankulan jama’a zuwa ga manufofinsu. Sukan yi maganar addini, suna kiran Allah don samun mafita daga halin da ake ciki. Har ma a kan samu wasu waqoqin da kacokam aka yi su da wannan manufa. Wasu kuma a xiyan baitocinsu ne suke maganar addini. Su kira Allah da ManzonSa, suna neman taimako da gaggawa. A cikin *Qamusun Hausa na Jami’ar Bayero*, an bayar da ma’anar addini cewa “Shi ne hanyar bauta wa Ubangiji”.

Addini yana da matuqar muhimmanci a rayuwar al’umma. Musamman idan aka lura da yadda ya zama hanya ta zama lafiya da samun kwanciyar hankali, walwala da jin daxi. Kuma yana tattara

al'ummomi baki xayansu, wuri xaya. Kuma yana kallonsu da siffa xaya. Babu wanda ya fi wani, sai wanda ya fi tsoron Allah.

A waqar *Baubawan Burmi,* Aminu Ala ya buxe waqar da kiran sunan Ubangiji. Ya kira sunan Allah mai girma. Wanda Allah Yake nuna mulkinSa. Ya yi hakan ne kuwa, watakila don kukan nasa na mulki ne. Ya nuna yana neman taimakon Allah da gaggawa .Ya ce a baiti na 1:

(149) "Allah Malikal Mulki,
Tu'util Mulka Mantasha'u a kan mulki.

Malikal Mulki sunan Allah ne mai girma, wanda fassararsa ke nufin (mamallakin mulki) akwai aya a cikin suratul Ali Imram, aya ta 26. Tana daga cikin ayoyin tauhidi. Tana da muhimmanci sosai, domin Allah ma na so a kira Shi da ita. Kuma Annabi SAW yana yawan faxarta. Kuma masana sun ce lokacin da aka saukar da ayar ta samu rakiyar mala'iku dubu saba'in, domin girmanta. Kuma dalilin saukarta Annabi SAW ya nemi Allah Ya sa sarkin Rome da Farisa (Iran) su zamo cikin al'ummarsa. Sai Allah Ya faxa masa haka domin ya samu natsuwa. Abu Khatim ya fitar da shi daga *Qatadah*. Ala ya kai qararsa ga Allah, don ya kira sunan Allah mai nuna mulki.

Ya ci gaba da kiran Ubangiji, yana nuna halin da ake ciki, abin na buqatar taimako. Yana suranta halin da mutanen Nijeriya ke ciki, yadda ake tafiyar da mulkinsu bisa gadara. Ya ce a baiti na 2-3:

(150) “Allah mun yi zaman dirshan,
Tamkar fitila a lokon alkuki”.

(151) “Sai a kaxa mu a raurayar,
Allah namu na buqatar jagora, iye-iye”.

Ya qara bayyana wa Ubangiji halin da ake ciki, cewa Allah Ya san abin da ke damunsa. Kuma shi kaxai zai iya maganin al’amarin. Ya ce:

(152) “Allah Ka san kukana,
Ka san hujjar zubar da hawayena”.

Haka dai ya ci gaba da kai kuka ga Allah, yana nuna Shi ke da ikon Ya yi komai. Idan Ya so Zai iya canza komai. Kamar yadda ‘yan amshi suka ce:

(153) “Ala mai faxakarwa,
Daina kukan kokawa,
Allah Ne ke sakawa,
Sannan Shi ke cirewa,
In Ya so zai canzawa,
Ba mai ikon hanawa”.

A cikin waqar *Bubukuwa* ya nemi taimakon Ubangiji, Ya yi maganin abin da ba a iyawa. Yana neman Allah Ya tsare qasar Nijeriya. Ya ce a baiti na 1:

(154) “Allahu Kai mana magani, abin da naj ji , da nag gani,
Mugun ji, mugun gani, rayuwarmu da hautsini,
Abin fa ba shi da kyan gani, abin a qyama da tsantsani,
Ya saka ni tuntuntuni, a yanzu ya sarayar da ni,
Na rasa in da za ni bi, Allahuwa, bubukuwa,
Kuna ta saukon bubukuwa, kuna gudu ba gurin zuwa”.

Wani lokaci a xiyan baitocinsu ma sukan kira Allah, suna neman taimakonSa, Ya kare qasar Nijeriya:

(155) "Rabbi Kai Ne Rahimi, tsare qasar Nijeriya".

A waqar *Xaurin Gwarmai* ma tun a amshin waqar, mawaqin ya rinqa kiran Allah, yana nuna girmansa, da qara sanar da Shi yanayin da ake ciki. Abin babu daxi. Ya ce:

(156) "Ya Ilahuna Mai girma, yau abin da dama,
Mun gaza da xaurin kamunga, har da xaurin gwarmai."

Ya ci gaba da kiran Ubangiji, yana kai kukansa, don Shi Mai yaye komai ne. Ya ce a baiti na 2:

(157) "Ubangijina har kullum Kai nake kai wa kukana,
Mai yaye hammi, gammi na taho da buqatuna,
Abin da ake a qasar nan, ya xugunzuma tunanina,
Zan faxi da baxala, an ce da ni na iya bakina".

Haka kuma, ya qara kai kuka ga Allah, yana bayyana masifun da jama'a ke ciki. Ya nuna laifin mahukunta ne na rashin adalci. Ya ce a baiti na 3:

(158) "Ubangiji masifu sun yi mana katutu,
Masifu na qirqira na neman samu zazzautu,
Katankatana ce da handama tas sa muka wahaltu,
Ubangijin al'umma Kai sauyin burtu."

'Yan amshi ma ba a bar su a baya ba, sun taimaka wajen kai qara da Allah, suna neman canji da gaggawa, sun ce:

(159) "Guguwa ta sauyin sauyi muke nema Allah,
Guguwa ta sauyin sauyi kaxawa bayinka."

Har a xiyan wani baiti na ya ce:

(160) “Ilahu Kat tsare mu da sharri na duk mai cutarwa,
Mutum da aljani sulukina tsare mu da cutarwa”.

A waqar *Ku Yi Haquri* Jibrin Jalatu ya kira Allah, ya nuna cewa Shi Ne Ubangijin kowa da komai. Don haka, mahukunta su yi tunanin mutuwa su daina abin da suke yi. Ya ce a baiti na 1:

(161) “Ya Arrahman, Ubangijin rahamar bawa,
Tu’util Mulku, Ubangijin dukkan kowa,
Ya qagi mutane da hankali, wani kuma wawa,
Abin da nake so, mu yo tunani kan mutuwa,
Ita ba ta tsoro, ba ta kula mulkin kowa,
Za mu mace de”.

Ya ci gaba da wa’azi da gargaxi ga mahukunta, a daina ha’inci, a yi mulki yadda ya kamata, don a samu sakamako mai kyau. Ya ce a baiti na 6:

(162) “A tuntuni tarkon matambaya de ikhwana,
Mai zalunci ba shi da fili aljanna,
Mai sata ba shi da fili aljanna,
Mai murxe zave, ba shi da fili aljanna,
Wasu ba su ibada, tun kan zave suka daina,
Ai nazari dai, don a lahira babu dabara”.

A cikin waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* Haruna Ningi ya buxe da sunan Allah. Ya nuna komai zai a fara, yana farawa da sunan Allah. Ya ce a baiti na 1:

(163) “Na ce bisimilla, ya Allah da Ka yo mu, mu ma bauta,
A dukkan lamari nawa, sunanka da fari na wajabta,
A cikin suratul A’alaq, a kan manzonKa Ka umurta,
Wa Nabiyyu Rasulullah, mu kam ba mu qaryata aya ba.”

Haka kuma, Ningi ya nuna cewa duk mai son ta zarce, ba mai son Allah ba ne. Ko Musulmi ne ko Kirista ne. Ya ce a baiti na 16:

(164) Duk wanda ya ce ta wuce, ku ce bai yarda da Allah ba,
To, idan a musulmi ne, bai gane dalilin sallah ba,
To, idan a kirista ne, bai san ma'anar gina coci ba,
Ai ni a mutuncina, gare su bai wuce zagi ba."

Ya yi kira ga alarammomi da fastoci, yana neman ya haxa su da Allah, ma'ana ya kai qararsu ga Allah, don ba su yi addu'ar rushe shirin ta zarce ba. Ya ce:

(165) "To, ina alarammomi, ina addu'arku ta juya ne,
To, ina kuma fastoci, ina addu'arku ta sauya ne,
To, wutar fitina ga ta, kuna kallonta, kuna zaune,
Ko kun ci kuxi ne ne, ba za ku gaxa su da Allah ba".

A cikin waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi* Haruna Ningi ya buxe waqar da kirari da yabon Ubangiji. Ya ce a baiti na 1:

(166) Ya Rabbi Mai sama Allah Gwanina,
Kai Ka halicci dare Ka yi rana,
Kai Ka halicci uwa da ubana,
Allahu ba ni basira wuce arna."

Ya yi tawassuli da darajar Manzo SAW yana neman shiriya da tsari a duk al'amurra. Ya ce a baiti na 2:

(167) "Don daraja ta Rasulu Fiyayye,
Manzon da Kai Masa sura tsayayye,
Allah Ka samu tafarki hayayye,
Ba ni tsaro a dukkan lamarina."

Ya rufe waqar da roqon Allah cewa 'yan Nijeriya su farga da sauri, don a samu mafita. Ya ce a baiti na biyun qarshe:

(168) "Allah Ka sa mu fahimta da sauri,
Mun tsinci kanmu a inda ke da tsauri,

Don dole ne mu ci kwakwa da bauri,
Kafin a gyara batun da ke gabana.”

A cikin waqar *Hawaye* Haruna Ningi ya kira Allah, yana neman taimakonSa Ya tsare qasar Nijeriya. Ya kuma kare ta daga sharrin azzalumai. Ya ce baiti na1:

(169) “Bismillahi Allahu Mai Nijeriyata,
Kai Ne Ka samarta, har ma al’ummarta,
Kuma Kai kaxai ne ka gagari mai raba ta,
Addu’a muke yi, Ka sake haxe ta sosai.”

Ya yi salati ga Manzon tsira, yana nuna irin takaicinsa na halin da Nijeriya take ciki. Ya ce a baiti na 2:

(170) “To nai salati ga Musxafa, Xaha Manzo,
Ahali, Sahabbansa, su ma masu qwazo,
Wannan qasidar da za na yi, zan ta yanzu,
Kuka take sa ni, ba murna nake ba, iye”.

A waqar *Rigar ‘Yanci* AbdulAziz Ningi, ya yi qwaqqwaran kira shi ma, yana kai kokensa a inda yake ganin za a amsa masa. Ya ce a baiti na 1:

(171) “Bismillah Ya Rabbana, Ya Jallah Sarkina,
Huwa Jallah, Ya Mai sama, Ya Mai dare, rana,
Huwa Rabbi, Kai Kai mani baiwa a farkona,
Na sake roqo ka ban ilmi a qarshena,
In sanar da Nijeriya, bana lokaci ya yi.”

A irin waqoqin nan na zamani, akwai waqar *Almajiri* da aka yi da wannan manufa ta addini kacokam. Waqar *Almajiri* waqa ce da aka yi da nufin farfaganda kan addini zuwa ga al’ummar Nijeriya. Waqar na kira ga xaukacin jama’ar Nijeriya, musamman na Arewa cewa a lura, a ga halin da almajirai suke ciki, a sa tausayi, a tallafi rayuwarsu gaba xaya.Ya fito da hoton rayuwarsa gaba xaya, ya suranta rayuwar, da rayuwa marar kyau, wanda a ganinsa ya kamata a gyara tsarin. Ya kira almajiri da dodo kamar ya ayyana cewa, “Kowa ya san abin da ke dodo.

Dodo shi ne abin da ke ba da tsoro, ko yake cin wani abu. Idan aka ce dodon mutum, wato wani abu ne wanda mutum yake jin tsoron kada ya cinye shi. To, kowa ya san mene ne tsaki, idan aka ce tsaki nan, ba ina nufin tsaki kawai ba wanda Hausawa suka sani. Tsaki wani abinci ne wanda Hausawa suka raina shi. To, shi dodo ne ga tsaki, ma'ana in ya haxu da tsaki, babu sauqi." Ya yi farfaganda sosai kan manufarsa. Tun daga amshin waqar, farfagandar ta fara bayyana, inda ya nuna matsayin almajiri, da kuma yin kira da a ji tausayin rayuwarsu duka, ya ce:

(172) "Almajiri baran malami na malam gajere dodon tsaki,
Ya al'umma mu sa tausayi a kan rayuwa ta almajiri."

Malumfashi (2004) ya tofa albarkacin bakinsa kan matsayin makarantun Islamiyya da irin yakan-bayan da boko yake masu. Ya yi maganar kisan mummuqe da ake yi wa ilmin Musulunci, yadda aka dankwafe ilmin Islamiyya, yadda Turawan mulki suka yi tasiri ga addinin Musulunci, har ya shafi ilmin Islama. Yadda yara masu ilimin Islamiyya ke fanxarewa in sun je makarantun boko. 'Wuce nan xan boko ya ga kundi'. "…Sai ga shi an wayi gari, ilmin da aka sani da tsari, da matakai iri-iri tun daga ma mai yin babbaqu da farfaru har ya zuwa alaramma, kada ma a ambaci makarantun ilimi iri daban-daban, ya zama in banda abin da ba a rasa ba, sai tulin mabarata. A duk zamanin da wani fanxararren malami ya bayyana, sai ka iske ya yi wa tsarin yankan qauna…"

Ya bayyana hanyoyin shawo kan matsalolin cewa ba dai za a yi watsi da bokon kwatakwata ba, kuma ba za a bari kare ya kashe ragon layya ba. Tunda bokon ya zama dole, ya zama qarfen qafa, a koyar da shi a Musulunce, bisa koyarwar Musulunci. A haxa bokon da Islamiyyar waje xaya. Ya nuna cewa an yi tarurruka na Musulunci kan yadda za a vullo wa ilmin boko, misali an

yi Makka a watan Maris 1997, sai a Islamabad. Sai a 1981 ka yi a Dhaka, sai Jakarta a 1992. Sakamakon waxannan tarurruka, aka fara kafa Jami'o'in Musulunci. A tasa shawarar kan yadda za a vullowa al'amarin, cewa ya yi bokon a yi masa gyara kuma a sake duba manhaja, da sake rubuta ta yadda za ta dace da aqidojin Muslunci, Ya sake cewa ba a kan manhaja kaxai da littattafai ba, yanayin koyarwar ma muhimmi ne. Malamai su zama abin koyi.

Ya buxe waqar da bayyana matsayin almajiri, yana masa kirari da nuna irin yadda rayuwarsa take gudana ba a yadda ya kamata ta kasance ba. Ya nuna yadda rayuwar ke tafiya a lalace, duk wani abin kirki ba na sa ba ne, sai dai abin da ba a so, shi ne nasa. Ya kira jama'a da cewa a tausaya wa rayuwarsu kada a gaza. A baiti na 1:

(173) "Xan almajiri da allo,
Ku xan tausaya wa qolo,
Wa za ya ba shi riga,
Wa za ya ba shi wando,
Ruwa ba shi za ya karva,
Sauran gida ya sharva,
Idan yara sun yi saura,
Don kar a kai a shara,
Abun nan mu qara lura,
Mu duba, mu qara gyara."

Daga nan sai basmalla, yana mai nuan girman Allah cewa Shi ne Ubangijin kowa da kowa. Ubangijin almajiri, da wanda ba almajiri ba. Sannan Shi ke ci da alamjiri da wanda ba almajiri ba. Haka kuma, Shi ke biyan buqatun kowa. Don haka, yana roqon Allah Ya taimaka masa wajen isar da saqo akan rayuwa ta almajiri. Ya ce a baiti na 2:

(174) "Allah Mai dare da rana, Ubangijin xan gari da baqo,
Mai ci da mai iyaye, Mai ba almajiri da qoqo,

Mannanu Jalla Rabbi, Kai Ke ba dukka masu roqo,
Na xauka hannuwana, kama min in isar da saqo,
Na lura dole mui waiwaye akan rayuwa ta almajiri."

Ya yi salati ga Manzon tsira, inda ya nuna girman darajarSa. Da kuma nuna miqa wuya ga sunnoninSa, tare da addu'ar kariya daga masifun duniya. A baiti na 3:

(175) "Ya Allah Ka yo salati, qara daxawa ga Xaha Manzo,
Manzon da Ya zarce kowa, a martaba, qoqari da qwazo,
Annabi na so Ka na yi dace, sai lamura ke ta qara wanzo,
TurbarKa na tsaya, ba ni turuwa, Sidi ba na darzo,
Tsamar da mu masifa, Ilahu tsamar da mu a kan haxxari."

Ya ci gaba da yabo ga Sahabbai da Alayen Ma'aki SAW. Ya yi kyakkyawan yabo a gare su, da nuna girman darajarsu, da jaruntakarsu. Da auliya'u da sauran malamai gaba xaya. A baiti na 4:

(176) "Allah a cikin salatinKa sanya Alaye da Sahabbai,
Kalle su ba su wasa, gun yaqi sun ka xau takubbai,
Su ne jaruman da ke wa kafirai raunuka da tabbai,
Har auliya'u masu sadaukarwar rayuka da kwabbai,
Haka na jinjina gurin malaman da ke ba mu tarbiyya ta gari."

Daga nan, sai dawo kan farfagandar manufarasa, inda ya yi kira ga jama'a cewa ga shi da sabon saqo da yake so ya bayyana, kan rayuwar almajiri wadda ke tafiya ba a bisa tsarin da ya dace ba. Don haka, zai warware, ya bayyana al'amarin don kowa ya fahimci inda aka dosa. A baiti na 5:

(177) "Jama'a yau ga ni da sabon zance, zan so ku bi ni sannu,
A kan rayuwa ta almajiri, nake son na yo bayanu,
Domin na ga ba a tsawurya tilas, sai cikin idanu,
Zan warware abawa in buxe yadda za ta tonu,
In qarqare ta, in warware ku gane abin cikin zahiri."

Ya ci gaba da fayyace wa jama'a kowaye almajiri, wato yana bayyana matsayinsa da irin yadda rayuwarsa ke tafiya ta yau da gobe. Da matsayinsa a idon al'umma baki xaya. Ya bayyana rayuwar ga ta nan dai, cikin wahala da tsanance-tsanance. A baiti na 6:

(178) "Almajiri bara shi mutan gari ke kira da qolo,
Gaishe da kai baran malami da ke kwalliya da allo,
Mai shan hura da tsami, ko ya don karin kumallo,
Mai yawo da xaura tsumma, su al'umma su dinga kallo,
Abin tausayi, abin qaiqayi, irin rayuwa ta almajiri."

Bai fasa ba, ya ci gaba da zayyana halin da almajirai suke ciki. Halin tausayi da wayyo. Komai na almajiri a wulaqance yake, a banzace. Ya bayyana rashin jin daxinsa kan yadda rayuwar ke tafiya, akwai tausayi da takaici. A baiti na 7:

(179) "Almajiri abin tausayi makwancinka za a kalla,
Sai mai shimfixar kwali, ko keso mai filo da hula,
Cinkoso, matsotso, lallai sha'anin ya saka ni qwalla,
Kai mai gardama taho leqa makarantarsu Shehu Kalla,
Wannan lamari duba, mu tausaya rayuwa ta almajiri."

Ya qara jaddada manufarsa da qara fito da hoton rayuwar almajiri. Ya bayyana rayuwar, da rayuwa ta rashin natsuwa da wadata. Shi ne ya yi kira ga jama'a da a binciki al'amarin don samun gyara. A baiti na 8:

(180) "Ga kwarkwata, qudan cizo, an turo shi yai karatu,
Fama yake da datti, ba nutsuwa in yana rubutu,
Ya je gari bara, an ci, an rage, kila ya wadatu,
In babu nutsuwa, ba wadatuwa ya ake karatu,
Kai mui nazari, mu duba, mu bincika kuma mu gyara al'amari."

Daga nan sai ya dawo kan jama'a yana nuni a gare su, yana qoqarin jawo hankalinsu da a dubi al'amarin da idon basira don samu mafita. Ya bayyana darajar almajiri, a matsayinsa na mai

karatun Qur'ani, mai neman ilmin addini. Kuma Qur'ani littafi ne mai daraja ga kowane musulmi. Saboda haka, me ye sa za a kyale masu neman ilmi daga gare sa, ba za a taimake su ba. Sai ilmin boko kaxai ake yi wa hidima. Don haka, a dawo a bi gaskiya, a taimaki rayuwa ta almajiri. A baiti na 9:

(181) "Qur'ani abin riqewa da daraja gun dukkan musulmai,
Haba mun qyale masu nema na ilmi da saninsa qazamai,
Boko ake ma bauta, a yi tsaf-tsaf don harin muqamai,
Haba al'umma mu juyo wa gaskiya don mu san karamai,
Mu dawo, mu duba al'amarin mu gyara wa namu almajiri."

Ya ci gaba da bayyana darajar almajiri, inda ya fi danganta sha'anin da musulunci, don saqon ya samu fahimtuwa da qarvuwa. Ya nuna cewa musulunci ya hana zama da qazanta, don haka, kar a bar rayuwarsa a haka. A duba yanayin da suke ciki, a nemi hanyar gyara, kada a bar su a haka. A baiti na 10:

(182) "Musulunci mu bincika yai hani mu zauna cikin qazanta,
Sannan ya ba mu 'yanci mu bi Allah mu huta da bauta,
Ma'ana kar mu xauki qasqanci, kai Allah Yana da kyauta,
Rayuwar nan irin ta almajiri, mu duba, mu daina qeta,
Mu gyara mu taimaka, kar mu bai suna tangaririya a gari."

Ya qara jaddada rashin jin daxinsa kan yadda aka yi watsi da rayuwar almajirai, ga su kuma a kan turba ta Allah, ta neman ilmin Musulunci. Wannan ne ma ya sa ake raina al'ummar musulmi, wato yadda sauran qabilu ke kallonsu kan yadda aka yi watsi da rayuwarsu. Don abin qara qarfi yake yi a ko'ina a al'ummar musulmi. A wasu qabilun kuwa, da wuya a samu almajirai. A baiti na 11:

(183) "Abin nan akwai takaici, abin yana qara ba ni tsoro,
Mun bar abin da Allah Ya ce, kamar yin hani da horo,
Mun rayuwa sasakai, maqiyanmu kullum suna hararo,
Mu ke da xaukaka, mun zamo kamar 'yan baran da qyauro,
Haba al'umma ana rena mu a kan rayuwa ta almajiri."

Ya ci gaba da nuna wa jama'a girman darajar almajirai, tunda su ke koyon Qur'ani har su zama masu koya wa wasu, malamai kenan. Don haka, ya yi kira da a riqi malaman nan da girma sosai. Kada a raina su, a kuma kyautata masu ta hanyar sadaka da kyauta. A baiti na 12:

(184) "Qur'ani mu mai da shi mai girma, kul kar mu bar shi yashe,
Malamai masu koya shi, mu riqe su da girma a kodayaushe,
Su zamanto cikin wadata, mu ba su kurxi kamar adashe,
Ma'ana sadaka da kyauta, mu rinqa yi kar mu bar su qunshe,
Haka nan shi uba ya ba malaman da ke yin kula da almajiri."

Ya juyo zuwa ga iyayen da ke turo da 'yayansu almajiranci, musamman yara 'yan qanana, waxanda ba su da wayo. Ya nuna cewa a daina kawo yara marasa wayo, don in an kawo su, ba za a san halin da suke ciki ba. Don qarshe barin neman ilmin suke yi, su shiga wata hanya ta daban. Ga kuma laifin iyaye na rashin tallafawa malamai, ya nuna taimakonsu zai zama da kyau sosai. A yi tunani, a gyara matsalolin. A baiti na13:

(185) "Duba kar ka tura yaro, xan qarami wanda bai da wayo,
A watsar cikin gari, ba uwa, uba har ya dinga wayyo,
Ba ka san ci da shanshi ba, ilmin da kake so ya dinga koyo,
Ba ka ba malaminsa ba, wata lada na yo kiranka juyo,
Uban xa da mai riqon xa, ku yi tunani ga wanga al'amari."

Sannan kuma ya yi kira ga masu hannu da shunu, yana nuna fa'idar taimako. Ya yi nuni gare su da su taimaki rayuwar almajirai, taimako na kaya da abinci, da sauran abubuwan buqata na yau da gobe, yin hakan akwai falala ba kaxan ba. A baiti na 14:

(186) "Ina yin kira ga masu kuxi, kai kuma ku sanya tausai,
Ku kai taimako wurin makarantun allo, ku ba su sosai,
A samu waxansu su kai abinci da tabarmi da matassai,
Kayan da za su sanya, a ba su sabullai da kilisai,
Lallai al'umma akwai falala cikin taimaka wa almajiri."

Haka nan kuma, ya zayyana yadda yake ganin ya dace rayuwar almajiri ta kasance. Ya nuna cewa a ci da su mai kyau, a kuma sha da su mai kyau, kamar yadda Allah SWT Ya yi umurni. Wato, a ba su irin abin da mutum zai ci, ba wanda ba ya so ba. Har ma ya nuna cewa shi zai kyautata wa almajiri, don yin yadda Allah Ya ce. A baiti na 15:

(187) "Abincin da ba mu so, kar mu ba su, Allahu Shi ka cewa,
Lantana lulbirra hatta tun fiqu, ida qarasawa,
Imma tuhibbu kenan, da ka fi so, shi kake ciyarwa,
Almajiri ka zo ga abinci mai kyau na ba ka nawa,
Irin haka ne ake so ga masu son tausaya wa almajiri."

Ya ci gaba da qarfafa cewa a kyautata rayuwar almajiri. Mu yi masu abin da za mu yi wa kanmu da 'yayanmu, misali kada a ba su sauran abinci, da sutura marar kyau da sauransu. A baiti na 16:

(188) "Babu sauran su nemi qanzo, a ba su mai kyau qwarai da gaske,
Ko xan dago-dago, xan tsaki-tsakin nan a kai shi wanke,
Sannan a ba su kaya, sui fes wanka jikinsu wanke,
Sai su bar tangaririya kan titi, nauyi ku zo mu sauke,
In mun hakan muna taimaka wa kai, taimako na almajiri."

Ya sake dawowa kan manufarsa, yana takaicin yadda rayuwar almajiri take. Ya siffanta rayuwar sosai don qara karkato da hankalin jama'a don a kyautata masu. A baiti na 17:

(189) "Almajiri bara shi mutan gari ke kira da qolo,
Gaishe da kai baran malami da ke kwalliya da allo,
Mai shan fura da tsami, ko da ya don karin kumallo,
Mai yawo da xaura tsumma, su al'umma suna ta kallo,
Abin tausayi, abin qaiqayi irin rayuwa ta almajiri."

Haka dai ya yi ta farfagandarsa. Ya yi masa addu'a da neman taimako wurin Allah SWT don rayuwar ta inganta ta kuma daidaita. A baiti na 18:

(190) "Gyara kayanka bai zama sauke mu raba in ji masu zance,
Mai son ya gane hanya, ba ya gudun masu yin kwatance,
Mai Sayyidil wara Muhamman Sani ga shi zan taqaice,
Allah Ubangiji na yi addu'a qara ba mu dace,
Allahu Jalla Kai tallafi a kan rayuwa ta almajiri."

Ya rufe waqar yana mai qara zayyana matsayin almajiri, tare da yi masa kirari, da nufin jin tausayi da jan hankalin al'umma su gane sosai da sosai. A baiti na 19:

(191) "Xan almajiri da allo,
Ku xan tausayawa qolo,
Wa za ya ba shi riga,
Wa za ya ba shi wando,
Ruwa ba shi za ya karva,
Sauran gida ya sharva,
Idan yara sun yi saura,
Don kar a kai a shara,
Abin nan mu qara lura,
Mu duba, mu qara gyara."

**4.13 Tattalin Arziqi**

Tattalin arziqi wata kalma ce da ake amfani da ita domin a nuna samun wadata, yalwa, arziqi, jin daxi da samun ababen masarufi da na more rayuwa. Kamar yadda Abdullahi bn Muhammad bn Abbas Azzahid (1998) ya bayyana a cikin littafinsa *Aja'ibul Malakut*. Wannan kuma yana faruwa ne lokacin da shuwagabanni suka yi wa talakawa adalci, suka tsare masu haqqoqinsu. Suka kuma yi raba daidai da kuxaxen qasa, ba tare da nuna bambanci ba. Domin yin hakan, shi

ke sa mutane su shiga cikin halin jin daxi da kuma walwala, da samun rayuwa mai amfani, tare da ci gaba a kowace hanya.

Arziqi yana tabbata lokacin da mutane suka zauna tare, babu rikici, babu rarraba tsakaninsu. Ba su jayayya da juna, to tabbas za su samu ci gaba da samun arziqi mai xorewa. Jama'a rahama ne, idan har mutane suka haxu wuri xaya, to Allah zai hore masu tattalin arziqi mai yawa, mai albarka. Musamman idan suna da shuwagabanni masu adalci, da kuma kiyaye wa kowa haqqinsa. Idan har shuwagabanni suka sauke nauyin dake kansu, suka ba da amanar da aka ba su ta jama'a, to za a samu yalwar arziqi. Yana daga hanyar raba arziqi da samun ci gaban tattalin arziqi, gina makarantu, kasuwanni da wuraren da za su kawo kuxin shiga.

Marubuta waqoqin farfaganda, a qoqarinsu na sauya tunanin al'umma, sukan yi maganar tattalin arziqin Nijeriya baki xaya, su bayyana wa jama'a yadda ake tafiyar da shi, ba a tsarin da ya dace ba. Suna nuna mahukuntan facaka kawai suke yi, ba sa kula haqqin talakawa. Sukan yi qoqarin kafa hujjojinsu da hakan, don su nuna wa jama'a haqiqanin gaskiyar al'amari. Irin waxannan abubuwan da suke bayyana wa na zahiri, shi ne ya sa har aka aje waqoqin a qarqashin inuwar farar farfaganda. Domin masu irin wannan farfagandar, suna bayyana haqiqanin abin da suke son bayyanawa, tare da tunkarar al'amari kai tsaye.

A qoqarin waqoqin na sauya tunanin jama'a, sukan dubi wasu abubuwa ginshiqai da suka shafi rayuwar al'umma, sai su riqa kafa hujjoji da su, suna masu jan hankali zuwa ga abin da ake buqata. Kamar yadda aka fahimta, mawaqan na fito da waxannan ginshiqan abubuwa ne don su jawo ra'ayin mutane, su sauya tunaninsu. Su qara nuna masu yanayin yadda ake mulkinsu bai

dace ba. Yin hakan na kira zuwa ga bore da tawaye, da ma abin da ya fi haka in akwai zuwa ga shuwagabanni. Za a ga yadda ra'in *Isar da Saqo* ya dubi irin wannan farfagandar don ganin yadda mawaqan suke isar da saqonsu, suke maganar tattalin arziqin qasa cikin waqoqinsu.

A waqar *Xaurin Gwarmai* ta Aminu Ala, ya rattabo ni'ima da baiwar da Allah Ya yi wa qasar Nijeriya, ya bayyana tattalin arziqin Nijeriya da ma'adanai masu dama, amma ba sarrafa su yadda ya dace, ya kawo abubuwa kamar gwalagwalai, gyaxa, rixi da makamantansu, da za a sarrafa a taimaki qasa da mutanenta, amma an bar jama'a cikin rashi, babu daxi. A baiti na 5-6:

(192) "Qasarmu akwai rana, amma qasar wasu ba rana,
Da za mu yi sola system, ilmin kimiyyar rana,
Ana maxari, sanyi, zafi, ni'ima duka a garina,
Sarkin alfarma, ni'ima ta qare a garina."

(193) "Muna da su man angurya, har da man gyaxa, man rixi,
Muna tasarifin man kwakwa, qasarmu akwai faxi,
Muna da kwaranda, gwalagwalai kar in ja ku da kauxi,
Muna tsallen baxake, abin kama da 'ya'yan kwaxi."

Ya ci gaba da zayyano albarkatun qasa kamar man fetur, qasar noma mai kyau, tama da qarafa, wanda za a yi amfani da su, a taimaki al'umma, amma xaurin gwarmai ya hana. A baiti na 7:

(194) "A qasarmu ana noma, Allah abin da ake nema,
Muna da qiragen fatun dabbobi da ake nema,
Qasarmu akwai tama da qarafa har robobi ma,
Akwai mu da ramun man fetur, amma ba dama."

A waqar *Bubukuwa* kuwa, Ala ya yi maganar tattalin arziqin Nijerya, amma bai ga laifin jama'a ba kan abin da ke aukuwa, a ganinsa laifin mahukunta ne, domin duk abin da jama'a ke yi na

rashin gaskiya kamar sata da shaye-shaye, akwai dalilin yin hakan, rashin shuwagabanni adalai, masu gaskiya, da za su tafiyar da arziqin qasa yadda ya kamata, shi ke jefa jama'a cikin masifa, har su fara xauke-xauke. A baiti na 5:

(195) "Sittin a cikin xari, lalura ta sa su bin dare,
Ashirin cikin xari, talauci ya sa su bin dare,
Talatin ta cikon xari, son zuci ya sa su bin dare,
Lidas sun kankane ma ma'adanai sun xare-xare,
Dukiya ta qasa da haqoqinta, sun kanainaye, sun maqare,
Ga isa da cikar isa da alfarma sun tattare,
Shi ya haddasa sace-sace a ko'ina tamkar ruwa."

A waqar *Mafarkin Mulki I* Jalatu ya yi tattauna kan albarkatun qasar Nijeriya. Ya yi maganar qasar noma mai kyau, da auduga, da gyaxa, da kiwo da sauran ma'adanai iri-iri da Nijeriya ke da su. Amma shuwagabannin ba su yin yadda ya kamata. Idan kuwa an samu mai kamantawa, sai an bi hanyoyin tozartarwa a gare shi. A baiti na 10:

(196) "A da, muna da noma na auduga an san da mu a duniya,
Qasarmu na da noman gyaxa, an san da mu a duniya,
Ga uwa, uba noma kiwo, an san da mu a duniya,
Kasuwanci na qasa da qasa, sun san da mu a duniya,
Da dai na fara mulki, komai sai ya sauya,
Na durqusar da gaskiya, ta rusunawa masu qarya,
Wanda ke da gaskiya, yanzu shi za ya sha azaba."

A waqar *Ku Yi Haquri* ya tavo arziqin qasa, ya nuna yadda mahukunta ke facaka da albarkatun qasa, su voye muhimman abubuwa don amfaninsu. Da kuma yadda ake fifita wasu abubuwa kamar qwallo qafa, fiye da talakan Nijeriya. A baiti na 3:

(197) "Ma'adanenmu ba a nuna wurin ajiyewa ba,
A sai da komai, ba a ba mu kuxin saidawa ba,
A wa muqamai, ba mu yarda da lamuncewa ba,

Qwallon banza ta fi muhimmanci duba,
A raya qwallo, talaka bai samu abinci ba,
Abin da ciwo, suna ganin sun yi dabara.”

A cikin waqar *Rigar ‘Yanci* AbdulAziz Ningi, ya yi maganar arziqin qasa, ya nuna akwai albarkatun qasa da dama, amma ba a yin yadda ya dace, sai fama da rashi ta ko’ina. A baiti na 15:

(198) “Kimar mutum xan-Adam, an yi ta mai girma,
Kaf, yau cikin duniya, an san mu, mun girma,
Ga dukiya kaf a yave, qasarmu kwai dama,
Yau ga shi Najeriyar, talakanmu na fama,
Domin rashin shugabanci, dole mui sanyi.”

Cikin waqar *Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba* sai Haruna Ningi ya qara magana kan tattalin arziqin Nijeriya, ya nuna ga qasa da ma’adanai amma talauci ya dami kowa, kansu kawai suka sani mahukuntan, sai masu goya masu baya. A baiti na 20:

(199) “To, idan maganar cewa arziqi na qasarmu ya xore ne,
To, ka gama yawon duniyarka, ka kasa zama zaune,
Na wajen ba su kawo ba, sannan na cikin kuma gurgu ne,
Ka tara kuxi jingim, amma ba mu daina talauci ba.”

Haka kuma, ya sake bayyana halin mahukunta don jama’a su yi qyama ga mulkinsu, don ya nuna an kwashe kuxin qasa, an voye, an bar jama’a cikin wayyo. Sannan duk wanda ya yi nufin raba kan al’ummar qasa, zai ga masifa. A baiti na 25-26:

(200) “To, kuxin da ka kwakkwashe, irin na qasarmu ka vovvoye,
Ka bar mu da nya-nya-nya, ka sanya qasarmu a nanaye,
Manufarka ta kwave ne, kowa ya rasa a yi ‘yar juye,
To, za ka ji kunya ne, idan ba ka canza dabara ba.”

(201) “Allah da Ya tara mu, Ya bar mu qasarmu guda tare,
Ya bar mu da jinsi xai, amma ya raba mu a kan yare,
Duk wanda ya daddage, sai ya raba kanmu zaman tare,
Ba zai wuce makonni kaxan, bai tad da jafa’i ba.”

Ya ci gaba da faxakar da jama’a kan manufofin ta zarce na zalunci, inda suke amfani da kuxi don su cuci jama’a, wai don ba su yarda ta zarce ba. Don haka jama’a sun farga, ba za su sake amincewa ba, komai ya biyo baya, su yi kuka da kansu. A baiti na 33-34:

(202) “Kun voye kuxi kun ce, ba za ku fitar su mu samu ba,
Don ku yi mana talala, a kan ba mu yarda ta zarce ba,
Mu mun gama qonewa, tokarku ba za ta yi illa ba,
Mun yarda ku more ku, ku ne ba ku yarda mu more ba.”

(203) “To, mun dasa aya yau, ku ma mu hana maku morewa,
In har kuka ce lallai, sai kun bi ta kanmu a zarcewa,
Komai ya biyo baya, kune asalinsa a somawa,
In kun gaza jurewa, oho ba mu damu ku jure ba.”

Ya sake batun arziqin qasa, ya nuna yadda shuwagabanni ke yin yadda suka ga dama, su hau da farashin komai, yadda jama’a za su tagayyara, ba su damu ba, aljihunsu kawai. A baiti na 41:

(204) “Ya rurrufe boda kaf, don kar jama’a su sayo sufuri,
Don kar mu ci shinkafa, sai dai mu tsaya a tikar gari,
Ya xaxxaga mayin ma, ya sanya qasarmu cikin bori,
Maganarmu ta fetur ma, a yau ba mu gane ministan ba.”

A cikin waqar *Hawaye* kuwa Haruna Aliyu Ningi ya qara nuna wa ‘yan Nijeriya baiwar da Allah Ya ba su, don ya bayyana taswirar Nijeriya, tare da zayyana albarkatun qasa da Allah Ya

yi wa Nijeriya. Ya nuna cewa Nijeriya na da albarkatun da wasu qasashe ba su samu hakan ba, amma kuma ba a amfani da su yadda ya dace. A baiti na 3:

(205) "Nijeriya qasa ce mai mutane,
Ga koguna tsaune, ga kuma bisashe,
Albarkatu ga su nan, na dubun qasashe,
Ita ce kaxai mai irin wannan ababe, iye."

Ya kawo tarihin Nijeriya ya bayyana salsalar sunanta. Ya nuna Mango Park ne ya raxa wa Nijeriya sunanta daga harshen Ingilishi. A baiti na 4:

(206) "Sunanta Mango Park ne yas saka shi,
Nigeria ne da yaren Ingilishi,
Daga Naija kogi ya samo salsalarshi,
Ai eriyar Naija ne, Nijeriya xin, iye."

Ya ci gaba da bayyana irin ci gaba na attalin arziqi da wasu qasashen duniya suke samu a kullum, musamman ta vangaren qere-qere da harkar tsaro. Ya ce kusan duk manyan qasashe suna yin nukiliya bam don kare qasa daga hare-hare. Amma Nijeriya babu wani abin qwarai, ko wutar lantarki ta kirki babu, ballantana maganar nukiliya. A baiti na 11:

(207) "Ku ga Indiyan yanzu nukiliya suke yi,
Pakistan har China nukiliya suke yi,
Iran da Korea nukiliya suke yi,
Nijeriya babu lantarkin gwadawa, iye."

Ya nuna cewa Nijeriya dai yanzu ta girma, an yi bikin cika shekar hamsin. Ga jama'a sosai, da kamfanoni da ma'aikatu da sauran abubuwa na more rayuwa, amma sun zama hoto. A baiti na 13:

(208) “An zo bikin shekarunki na kai na hamsin,
‘Yayanki sun yi miliyan xari da hamsin,
Shin kamfanoninki sun yi xari da hamsin,
Da suke da lebur dubu hamsin kowane, iye.”

### 4.14 Zamantakewa

Zamantakewa wata kalma ce da take nufin zama wuri xaya, cikin aminci da kwanciyar hankali da kuma bai wa kowa haqqinsa ba tare da an cuta wa xaya daga ciki ba. Almajir (2006) ya bayyana zamantakewar Hausawa cewa “Zamantakewar Hausawa ta qunshi halayyar rayuwarsu da yanayin tattalin arziqinsu da ilminsu da yanayin suturunsu da mu’amalolinsu na yau da kullum dangane da muhallinsu da yanayin qasarsu kamar yadda Ingawa ya bayyana”.

Kuma yana daga kyakkyawar zamantakewa xabi’u kamar haquri, yafewa, cika alqawari da kiyaye haqqin xan-uwa da iyali da maqwabta da sauransu. Yana daga kyawon zamantakewa, rashin nuna bambanci da wariya tsakanin mutane, da kuma xaukar kowa da irin matsayinsa.

Yana daga zamantakewa kiyaye haqqin xan’uwa da tsare masa mutunci. Yana daga zamantakewa kamar yadda Imam Suyuxi ya ce “ Ka yaye wa xan-uwa baqin ciki, idan ya dame shi. Ka tausaya masa, idan ya shiga hali. Ka taimaka masa idan yana cikin matsala. Ka kuma suturta shi. Ka rufa masa asiri, idan ya yi abin kunya. Domin Allah Yana taimakon bawa, matuqar yana taimakon xan-uwansa.

Kyakkyawar zamantakewa ita ce ke kawo zaman lafiya da jin daxi, da kuma walwala, ba tare da rikici ba. Wannan shi ne tsarin da magabatanmu suka xauka, har suka zauna lafiya da junansu.

Waqoqin kan dubi yanayin zamantakewar jama'a, sai su nuna cewa rayuwar na tafiya ba a bisa tsarin da ya dace ba.

A waqar *Baubawan Burmi* ta Aminu Ala, da ya yi qoqarin ya suranta yanayin zamantakewar jama'a, tare da isar da manufarsa ta neman canji ko sauyi na tsarin jagoranci da ke wakana, a baiti na 2-3:

(209) "Allah mun yi zaman dirshan,
Tamkar fitila a lokon alkuki."

(210) "Sai a kaxa mu a raurayar,
Allah na muna buqatar jagora."

A waqar *Bubukuwa* kuwa, Aminu Ala ya buxe waqarsa da roqo ga Allah Ya yi maganin masifu da bala'in da ke faruwa a qasa, wanda ya nuna rayuwar mutane tana cikin haxari, babu kwanciyar hankali, al'amarin ya kai wani matsayi na qaqa-ni-ka-yi, kamar yadda ya bayyana a baitin farko:

(211) "Allahu Kai mana magani, abin da naj ji, da nag gani,
Mugun ji, mugun gani, rayuwarmu da hautsini,
Abin fa ba shi da kyan gani, abin a qyama da tsantsani,
Yana saka ni tuntuntuni, a yanzu ya sarayar da ni,
Na rasa inda za ni bi, Allahuwa, bubukuwa,
Kuna ta saukon bubukuwa,
Kuna gudu ba gurin zuwa."

Cikin waqar *Xaurin Gwarmai* mawaqin ya bayyana yanayin zamantakewar jama'a, har yana kai kokensa ga Allah SWT yana nuna al'amarin ya tsananta, an rasa mafita, ana cikin uquba, kamar yadda ya bayyana a amshin waqar. Ya ce:

(212) “Ya Ilahuna Mai girma, yau abin ba da ma,
Mun gaza da xaurin kamunga, har da xaurin gwarmai.”

Sannan kuma, ya ci gaba da roqon Allah kan buqatunsa na neman ya zamo maxaukaki a harkar waqa, kuma Allah Ya taimaka a samu kuvuta daga qangin da ake ciki. Yanayin da al’umma ke ciki babu daxi, a baiti na 1:

(213) “Ya Ubangiji yarda da ni Ala in zamanto jarmai,
A fagen waqa in zama sha-kwaramniya, sha-gwarmai,
Sarki Allah Ya yarda da ni, in sunce xaurin gwarmai,
Ubangijina Allah, halin kamar ya sa nay yi amai.”

Ya ci gaba da farfagandarsa, yana zayyana ra’ayinsa da isar da saqonsa ga al’umma da nufin su lura da yadda ake tafiyar da su, ana mulkin kama-karya, ana jawo masifu kala-kala, wanda a ganin mawaqin qirqiro su aka yi saboda handama da babakere na rashin tawakkali. Don haka, ana neman agaji ga Mai duka. Ya bayyana a baiti na 3:

(214) “Ubangijina masifu sun yi mana katutu,
Masifu na qirqira na neman samu, mu zazzautu,
Katankatana ce da handama ta sa muka wahaltu,
Ubangiji al’umma Kai sauyin burtu.”

A waqar *Baubawan Burmi* Ala ya sake bayyana halin da talakawan Nijeriya ke ciki, ya zayyano yadda mahukunta ke damawa da facaka da kuxin gwamnati, suna gina gidaje masu tsada, da kai ‘yayansu makarantu masu zaman kansu da sauran abubuwa irin haka. Hakan ya fito a baiti na 17-19:

(215) “Dangi a waiwaya a duba,
A makarantunmu daban ne da na ‘yayansu.”

(216) “La’akkari da abincinsu,

Kama har zuwa ruwan da suke sha su.”

(217) “Kai duba da makwancinsu,
Daga nan za ka gane mugun jagora.”

A waqar *Bubukuwa* kuwa, Ala a baiti na 6, ya yi kira ga rukunonin al’umma tun daga shuwagabanni, masu arziqi, ‘yan siyasa, malamai, kai har ma da sauran talakawa, amma ‘yan zamani kamar yadda ya kira su. Ya zayyana masu cewa abin da ake aikatawa babu inda zai kai mu, matuqar za su yi yadda suke so, al’umma ba za su ga yadda ya dace ba.

(218) “Shuwagabanni na zamani,
Masu hali na zamani,
Malamai ‘yan zamani,
‘Yan siyasar zamani,
Talakawan zamani,
Katankatanar zamani,
Ta samu saukon bubukuwa,
Bubukuwa.”x 2

A cikin waqar *Xaurin Gwarmai* ya daxa fayyace halin da ake ciki, wanda ya kira shi da halin wayyo, halin kaico, musamman idan aka kaxa kugen siyasa, rai zai zama ba a bakin komai ba, matattu ma ba a bar su ba, sai an bi su har makwancinsu an xebi wani abu daga jikinsu. Qananan yara a sace, a yanka, don cimma buqatar zave. Ya bayyana wannan takaicin nasa a baiti na 4:

(219) “Duk wuya da halin wayyo, ya samu cikin wayyo,
Mahaukata a garin nan, an ba su cikin goyo,
Mu waiwayo qananan yara, da ke yin oyoyo,
Jirajirai ana yankawa, Allah Kai sakayya,
Muqabira ana tonawa a yaye alawayyo,
A yanki mamaci da gadara, wayyo! Allah wayyo!

Cikin waqar *Bubukuwa* ‘yan amshi ke nuna cewa jama’a gaba xaya na cikin ruxu, don su kansu shuwagabannin ba su da kwanciyar hankali, don a cikin jin daxi ake cin duniyar ba, bala’in da ke

aukuwa a qasa, su ma ta wani vangare ya shafe su. Sauran jama'a ma, ba jin daxin suke yi ba, su da ake mulka cikin gadara. Wato dai, a nuna rayuwa ta tsananta ga kowa, don rashin gudanar da mulki yadda ya dace. Suka ce:

(220) "Ba ku da kwanciyar hankali,
Ba mu da kwanciyar hankali,
Ba su da kwanciyar hankali,
Mun yi rashi ba adali,
Muna saukon bubukuwa."

Haka kuma, a cikin *Baubawan Burmi* mawaqin ya qara zayyana halin da 'yan Nijeriya ke ciki, yana qara jaddada haka, tare da neman sauyi ga Allah, a baiti na 23:

(221) "Mun azabtu da qwawa,
Qarar kuka da tsuwa,
Mun shagaltu da yunwa,
Mun bishe da qishirwa,
Mun makance da sowa,
Allah Kai Ke sauyawa."

Sannan ya ci gaba da bayyana yanayin mahukunta da yadda suke tafiyar da rayuwar matasa, inda ya nuna cewa suna amfani da 'yayan mutane musamman a wajen yaqin neman zave, a yi faxace –faxace, ba tare da nasu 'yayan ba, hakan ya nuna rashin adalci ke nan. A baiti na 24-29:

(222) "Suke tarkata yaranmu,
Da makamai suna ta sarar junansu."

(223) "Inda alamar adalci,
To, mai zai hana su cakuxa 'yayansu."

(224) "Kayan maye suka ba su,
Su hau gidan mutum su faxa shi da sara."

(225) “Kuxin abinci ake ba ku,
An maishe ku sai ka ce dabbar kiwo.”

(226) “Kuxi a dumtse su a watsa,
Ku bi kuna ta wawaso har ku ji ciwo.”

(227) “Ungulu za dai fa ki koma,
Gidanki dai na tsamiya daina gadara.”

A waqar *Mafarkin Mulki I* ta Jibrin Jalatu, shi ma ya bayyana matsalolin da ‘yan Nijeriya ke fuskanta, wato buqatun da suke fatan su ga sun samu, da yadda mahukuntan ke nuna rashin damuwarsu ga abin da jama’a ke ciki. Matuqar dai su za su ji daxi, sauran al’umma kuma su sha wuya. In dai ba a bi gaskiya ba, dole a sha wahala. A baiti na 2:

(228) “Sun ce qasa musiba, ni ko musiba ba ta gabana,
Sun ce qasa bala’i, ni ko bala’i ba ya gidana,
Sun ce a kama gaskiya, ni kuma gaskiya ba ta gabana,
Sun ce a daina cin hanci, cin hanci ya zama jinin jikina,
Sun ce a daina murxiya, ni kuma murxiya na hau abuna,
Sun ce da ni tsaro, ni ko tsaro ba ya gabana,
Ban bi gaskiya ba, mutan qasata ku shiga azaba.”

A cikin waqarsa *Mafarkin Mulki II* kuwa, ya sake zayyana da kuma fito da yanayin rayuwar jama’a, wadda ya nuna a birkice, su shuwagabannin ba su damu ba, dan ba su ma san ana yi ba, jin daxinsu kansu kawai sai wanda suke so. Qasa na cikin ruxu, babu ingantattun makarantun boko da sauran abubuwa na jin daxi, ya bayyana haka a baiti na 4:

(229) “In jama’ar qasarmu ma wasi-wasi,
Sai yaqi ake ina shan A/C,
Talakawa duka ba mai sisi,
Duk makarantunmu na wasi-wasi,
Talakawanmu babu mai shan A/C,

Talakawanmu sun shige wasi-wasi,
Burina kawai a qyale ni a kan mulki.”

Bai gushe ba, sai da ya qara bayyana yanayin da al’umma ke ciki, wanda shuwagabannin ke haddasawa, su kuwa ba su ma san ana yi ba, burinsu kawai zalunci, ga murxiyar zave, da rashin kuxi, da sauran nau’in zalunci kala-kala. A baiti na 9:

(230) “Na saka zuciyarsu na yin raxaxi,
Wahala ta yi yawa qasa babu kuxi,
Sai murna nake, ina jin daxi,
In zave ya zo, na sa a yi maguxi,
Sai mulki nake, suna ba daxi,
Sai mulki nake, suna ba daxi,
Burina kawai a qyale ni a kan mulki.”

A cikin waqar *Ku Yi Haquri* Jibrin Jalatu ya nuna qyamarsa ga mulkin da ake a yi a Nijeriya, ya baza ra’ayinsa sosai wanda yake son jama’a su yarda, maimakon ya buxe waqar da basmalla kamar yadda aka saba, sai ya buxe da tarrarrabi da nuna rashin jin daxi, wanda ya bayyana zuwa wani matsayi mai ban tsoro, da tausayi. Wato, ya yi kira ga shuwagabanni da su lura da yanayin da suka sanya jama’a, akwai tausayi sosai. Ya ce:

(231) “A dinga tunani,
Akwai jin tausai,
Akwai jin tausai,
Akwai jin tsoro.”

Daga nan, sai ya ci gaba da lallashin jama’a, yana ba su haquri, a qara bisa wanda ake yi, don za a ga amfaninsa.

(232) “Jinjinar talakawa ce,
Daga Jibrin Jalatu,
Haqurin nan da muke de,
Kada mu gaza, mu qara,
Zai mana amfani can.”

Sai kuma ya yi kyakkyawan yabo ga Ubangijin kowa da komai. Da kuma gargaxi a ji tsoron Allah, don ko ba komai, akwai mutuwa, wadda za ta xauki mutum komai muqaminsa, sannan idan ba a yi aiki mai kyau ba, babu sakamako mai kyau. A baiti na 1:

(233) “Ya Arrahman, Ubangijin rahamar bawa,
Tu’util Mulku, Ubangijin rahamar kowa,
Ya qagi mutane da hankali, wani kuma wawa,
Abin da nake so, mu yo tunani kan mutuwa,
Ita ba ta tsoro, ba ta kula mulkin kowa,
Za mu mace dai, don a lahira babu dabara.”

Ya yi a maganar yadda ake zalunci ga talaka, a danne haqqinsa, idan kuma ya nuna zai nemi ‘yancinsa, a sa hukuma ta xaure sa. Mutum na gani a cuce sa, babu damar magana. Hausawa kan ce ‘A bugi mutum a hana sa kuka’. Ya ce hakan a baiti na 2:

(234) “Ana qwararka, a ce ba dama ka ji haushi,
A danne haqqinka, a ce ba dama ka ji haushi,
Da ka yo magana, a ce maza wancan kama shi,
A sa shi gidan yari babu tausai a tsare shi,
Da ya yo motsi, ku sa makami ku kashe shi,
Abin da ake yi, a gaskiya babu dabara.”

Haruna Aliyi Ningi a waqarsa ta *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi* ya yi magana zuwa ga talakawan Nijeriya, ya yi kira a gare su da su saurare shi da kunnen basira, su ajiye duk wasu lamura nasu, don zai bayyana masu halin da ake ciki, a baiti na 3:

(235) “Talaka ga ni da waqa ina so,
Ka jingine duk uzurinka ka, ka taso,
Ka zauna ka ci ji gwaxoso,
Za ka fahimci ina aka kwana.”

Haka kuma a baiti na 6, ya zayyana wa jama'a abin da shuwagabanni ke haddasawa na yanayin zamantakewa, musamman lokacin siyasa. Sun xauki jama'a wawaye, suna masu ingiza mai kantu ruwa, su kai jama'a su baro. Wato, yadda suke haddasa fitintinu, su kuwa ba za ta shafe su ba. Ya ce:

(236) "Sun sa muna kashe kanmu da sara,
Gobe ka gan mu a kotu da qara,
Su ko ba za su iya nan da yara,
Ba za ka gan su a gun da ke da rana."

Ya sake jawo hankalin jama'a da nuna masu cewa aikin banza suke yi. Idan sun mutu, sun mutu a banza, iyalensu kawai ke da asara babu ruwan wani xan siyasa. Don haka, ya gargaxi jama'a a kawar da irin wannan aqida. A baiti na 7:

(237) "Duk wanda ya mutu, ya mutu banza,
Ba wanda zai ba iyalensa gabza,
Wanda ya kashe wani ko a ziza,
Sai ya tagayyara ko da, da kwana."

Haruna Ningi kuma, a waqarsa ta *Hawaye* a qoqarinsa na bayyana halin da Nijeriya take ciki, ya kawo tarihin Nijeriya, ya nuna yadda abubuwa suka cakuxe, yanayin zamantakewar ya zama babu daxi tun ma a farko farko. A baiti na 6:

(238) "Ba su cimma buri ba, sai fitina ta sauka,
Rikici ya varke kama da ruwa na kaka,
Daga nan qasar nan, ta sauka baqar iyaka,
Wanga tarihi ne da ban sha'awar tuna shi, iye."

Haka ma a baiti na 7 ya bayyana cewa har zuwa yanzu Nijeriya na cikin halin qaqa-ni-ka-yi. Masu jin daxi a qasar kaxan ne. Duk qabilun Nijeriya ba mai cewa gwamma da akai, sai kuka da neman agaji, don yadda shuwagabanni ke wa jama'a riqon sakainar kashi. An mayar da jama'a kamar dabbobi, har gara dabba ma wani lokaci da yadda ake juya jama'a.

(239) "Daga nan ko murna ta qare, sai hawaye,
Kuka muke yi, qabila ko ta waye,
Wasu 'yan tsirarun qasar nan, wai gwanaye,
Su ne suke sarrafa mu kamar tumakai, iye."

Shi kuwa AbdulAziz Ningi a waqarsa mai suna *Rigar 'Yanci* ya bayyana yadda talakan Nijeriya ke fama da rashi ta ko'ina, ya nuna cewa wahala ta yi yawa, don haka, ba makawa, dole talaka ya tashi ya, ya nemi canji na haqqi ko ta halin qaqa. A baiti na 2:

(240) "Farkon zuwan xan-adam, ai mar raxin suna,
Bai ba dare xan-adam ko kuma raxin suna,
Ba rashi a Nijeriya ya zam kamar vauna,
Kowa gudu nai yake, domin yana rana,
Sauyi a Nijeriya bana dole sai mun yi."

Haka kuma, Jibrin Jalatu a waqar *Ku Yi Hakuri* ya zayyana halin da wannan nau'in mulki ke jefa mutane, qasa ta rikice babu kuxi, sai raki ake yi ta ko'ina. Abin dai ba a cewa komai. A baiti na 4:

(241) "Abin da na duba talaka mutum ne shi mahaqurci,
Ana mulkin shi da murxiya bisa zalunci,
Ya nemi haqqinshi, a ce da shi ya cika naci,
A bar shi da yunwa, cikin dare babu abinci,
Ya wayi gari in ya bincika babu abinci,
Abin ban tausai, za ka ji kukan 'yan yara."

Haruna Aliyu Ningi a waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi* ya nuna rashin jin daxinsa, yana ganin wautar jama'a da har ta'addanci ke shiga tsakani a kan irin waxannan mahukunta wanda ko an zave su, ba su kyautatawa kowa. Sai wulaqanta rayuwar mutane, ba su xauke ta a bakin komai ba. A baiti na 13:

(242) "Don me muke ta wulaqanta juna,
A kan wanda ba su da tsoron amana,
Wanda suke mana kamun sakaina,
Sun bar mu zaune a daji ya vauna."

Haka ma ya ci gaba da zayyana wa jama'a aibobin mahukunta ta yadda ba su kyautata rayuwar jama'arsu. Kansu kawai suka sani, sai 'yayansu. Ya nuna rashin ilmi ingantacce da wadatattun makarantu. 'yayansu kawai ke damawa, talaka kuwa shi ya sani. A baiti na 16:

(243) "Sun qi su kyautata duk makarantu,
Don kar xiyan mu su je, su yi karatu,
An bar su talle, acava, zuruntu,
Yaransu na inuwa, namu a rana."

A waqar *Mafarkin Mulki II* Jibrin Jalatu ya sake nuna yadda talakawa ke gudun shuwagabanni, idan wahala ta ishe su ta ko'ina. Sai lokacin zave, a ce su zo a yi da su, jama'a kuma su ce ba sa yi. Wato ya fito da abin da ke faruwa a lokacin ana a kan mulki, da kuma idan lokacin zave ya zo. A baiti na 10:

(244) "Wahala ma ashe tana kashe kwaxayi,
Jama'a sun jigata sun bar kwaxayi,
In zave ya zo, su ce ba sa yi,
In na ce su zo, su ce ba sa yi,
Shin wai ni yanzu yaya zan yi,
Shin wai ni yanzu yaya zan yi,
Mamuguntan qasa su mai da ni a kan mulki."

AbdulAziz Ningi kuma a waqar *Rigar 'Yanci* ya ci gaba da bayyana halin da jama'a ke ciki, halin wahala da ma bauta ga shuwagabanni, da yadda mahukuntan ke nuna jama'a ba su da wata kima da daraja a wurinsu, sai lokacin zave ya zo. Idan zaven ya wuce, sai su manta da haqqin da ke kansu. Don haka, 'yancinmu na a hannunmu, mu yi amfani da shi yadda ya kamata. Baiti na 14:

(245) "Amma mai da mu sai bara, wasu na bixar qanzo,
Ba a kusantarmu ma, sai in wuya ta zo,
Kuma ba mutum xan-adam, mai maganin qozo,
Bana ba mu bin mai abawa, mai zare ya zo,
'Yancinmu rigarmu ce, bana lokaci ya yi."

A waqar *Ku Yi Haquri* Jalatu ya bayyana halin da mahukunta ke son su ga jama'a a ciki, hali na qunci da wahala, ga rashin wadataccen ilmi, abinci da sauransu. A baiti na 5:

(246) "Yanda suke so, talaka ba zai numfasa ba,
Yanda suke so, talaka ba zai ci abinci ba,
Yanda suke so, talaka ba zai yi karatu ba,
Yanda suke so, talaka ba zai zama kowa ba,
Yanda suke so, talaka ya zauna da uquba,
Babu haxin kai, a gaskiya gara mu gyara."

AbdulAziz Ningi a waqar *Rigar 'yanci* ya qara jaddada yanayin zamantakewar jama'a, ya nuna abun dai ba a cewa komai, ceto sai Allah da malaman gari. A baiti na 16:

(247) "An sha mu man guna, bakinmu na xaci,
Matar da ke naquda, ai ba ta barci,
Duk wadda ke yin fito, gurinsa kai gacci,
Yau ga shi Najeriya, mara shi ba ya bacci,
Tsananin rashi babu kansa, tauna qwayoyi."

A waqar *Hawaye* Haruna Ningi bai fasa rattabo wa Nijeriya aibunta ba. Ya nuna yadda talauci ke damun jama'a, kuma ga babu aikin yi, sai ta'addanci na siyasa da sace-sace. Don ba su wadata kowa ba sai kansu kawai. A baiti na 18:

(248) "In babu ci ai batun murna bula ne,
Kuma ga talauci yana ta tuqar mutane,
Ba ayyukan yi, qasar duka ta gunane,
Varnar ina ji, iya su ne suke yi."

A cikin waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi* ya nuna halin-ko-in-kula da shuwagabanni ke nunawa ga jama'a. An bar al'umma cikin qunci da talauci, ga yunwa da wahalhalu na rayuwa. Har ya nuna cewa dabbobinsu sun fi jama'a daraja da mutunci a idonsu. A baiti na 20:

(250) "Kai sai ka kwana da yunwa da qunci,
Shi ko karensa yake ba abinci,
Don shi a gunsa yana da mutunci,
Kai ko ka duba ta ya ko ka kwana."

Ya ci gaba da nuna rashin kulawa ta vangaren lafiya, ba a gina asibitoci, ballantana a kawo wadatattun magunguna. Shi ne ya ce ai ya kamata jama'a su gane, su daina zavar irinsu. A baiti na 21:

(251) "Jinyarka babu ruwansu da duba,
Ba zai saya maka pengo ka sha ba,
Ga bai gina maku gun magani ba,
Ai ya kamata ku gane batuna."

Sannan kuma ya qara nuna rashin kulawarsu ta fagen ilmi, da abinci. Ga talauci ya dami kowa, sai zaman qunci da wahala da jama'a ke ciki. Ya nuna wahala dai ta yi yawa. A baiti na 22:

(252) "Sun bar mu ba ilmi ga talauci,
Ga sun rufe mana hanyar abinci,

Sun bar mu zaune a dauxa da qunci,
Sai gwara kanmu suke yi da juna.”

Haruna Aliyu Ningi a cikin waqar *Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi* ya ci gaba da zayyana wa jama’a laifukan shuwagabanni, musamman yadda kawai kansu suka sani, ba su da mu sauran al’umma ba. Sun fi so su ga jama’a cikin wahala, a wulaqance, sai dai a yi maula, sannan su bayar. Ba su da mu da kyautata rayuwar jama’a ba. A baiti na 24:

(253) “Ba za su yarda ka samu ba ka ji,
Don kar su daina ganinka a juji,
Sun maida duk lamuranmu ya kaji,
Sun xan barbaxa mana tsaba da rana.”

Haka kuma, ya qara kira ga jama’a kada a amince, a yarda da halin da suke jefa jama’a, suna ta’addanci da cin zarafin juna. Idan sun yi haka, suna qoqarin raba kanmu ne. Duk lokacin da aka samu savani tsakanin waxannan da waxancan, ana daxa samun givi kenan, sai rashin jituwa ta samu. Shi ne ya yi kira ga jama’a da su gane hakan. A baiti na 25:

(254) “Ya zamu yarda da wannan ta’asa,
Tsakaninmu na daxa givi da nisa,
Sun mai da mu akwashinsu na yasa,
Mutane ku lura, ku gane batuna.”

Bai gushe ba, ya ci gaba da faxa wa jama’a yanayin zamantakewarsu babu daxi. Yana yin hakan ta nuna laifukan mahukunta cewa jama’a na a rana, su suna a inuwa. A baiti na 26:

(255) “Ban yi musun lamarin duniya ba,
A kan duk ba za a kasance guda ba,
Amma ba zan qi a kyautata kar ba,
Duk wanda ke sama, sun masa rana.”

Sai ya yi addu'a cewa Allah SWT Ya sa jama'a su gane abin da yake son su fahimta, don ana cikin wani hali marar daxi, na wahala. Sannan a gyara al'amarin ma, sai an ci kwakwa. A baiti na 27:

(256) "Allah Ka sa mu fahimta da sauri,
Mun tsinci kanmu a inda ke da tsauri,
Don dole ne mu ci kwakwa da bauri,
Kafin mu gyara batun da ke gabana."

## 4.14 Kammalawa

Wannan babi ya kammala, bayan an yi xan taqaitaccen tarihin mawaqan da bayanin salsalar waqoqin. An yi maganar abin da ya haifar da samuwar waqoqin, tare da dalilin da ya sa aka kira su waqoqin farfaganda. Sai taqaitaccen tarihin kafuwar siyasa a Arewacin Nijeriya. Sai nason farfaganda a cikin wasu waqoqin fiyano na Hausa. An ga nau'in farfagandar da waqoqin suka rataya akai, wanda suka a ta'allaqa a inuwar farar farfaganda, wadda ke ba da damar bayyana haqiqanin gaskiyar al'amari, ga amfani da sassauqar hanya don jawo hankalin jama'a. Ba kamar baqar farfaganda ba, wadda a kan yi don a muzanta abu, a kuma vatar da tunanin mutane. Sai yadda farfaganda ta bayyana a cikin waqoqin. Sannan mun ga yadda waqoqin ke qoqarin zaburar da mutan Nijeriya, su san 'yancinsu da haqqinsu, da ma irin shuwagabannin da ya kamata su zava. Haka kuma, an ji yadda waqoqin suka yi maganar yadda ake gudanar da mulki, ma'ana yadda ake gudanar da shi bisa tsarin son rai. Waqoqin sun nuna yadda mahukunta ke yaqin neman mulki. Bayan sun samu, su watsar da jama'a, su zama 'ramin kura daga ke sai 'yayanki'. Sannan waqoqin na maganar addini, su kai kukansu ga Allah, da neman agaji da mafita.

Bayan haka, an ji yadda marubuta waxannan waqoqi ke bayyana yanayin tattalin arziqi Nijeriya. Da kuma yadda yanayin zamantakewar mutanen Nijeriya ke kasancewa. Waqoqin na nuna cewa ana facaka da arziqin qasa, ba a sarrafa shi yadda ya kamata. Mawaqan kansu kawai suka sani. Sannan suna zayyana aibobin mahukunta ta yadda ba su kyautata wa rayuwar al'umma. Waqoqin na zayyana matsalolin da Nijeriya ke fuskanta. Suna maganar yadda ake zaluncin talakawa, a danne masu haqqinsu, idan aka yi magana, a sa hukuma ta xaure mutum. Mawaqan na nuna qyamar mulkin Nijeriya.

# BABI NA BIYAR

# NAXEWA

## 5.0 Gabatarwa

A wannan babi za a yi taqaitawa a kan aikin gaba xaya. Za a bayyana yadda aka aiwatar da wannan aiki daki-daki, cikin tsai mai kyau. Sai kammalawa kan abubuwan da aka binciko da shawarwari in gantattu. Sai manazarta da rataye na waqoqin da aka yi nazari, tare da jerin tambayoyin da aka yi wa mawaqa da sauran manazarta.

## 5.1Taqaitawa

An gudanar da wannan aiki daki-daki, cikin tsari mai qayatarwa. Don haka, wannan aiki ya qunshi babi guda biyar. A babi na farko an yi bakandamiyar gabatarwa da ta yi bayanin abin da aikin ya qunsa. An bayyana manufar bincike da dalilinsa. Sai muhimmancin bincike da hasashe da kuma iyakacin bincike. Babi na biyu biya ce kan ayyukan da suka gabata masu dangantaka ta kusa da ta nesa da wannan aiki. An duba kundayen digiri na xaya, na biyu da na uku. Sai muqalu da bugaggun littattafai. An waiwayi waqoqin farfaganda xin. An bayyana samuwar waqoqin fiyano na Hausa da muhallan da ake rera waqoqin. Babi na uku ya qunshi dabaru da hanyoyin gudanar da bincike. Babi na huxu ya qunshi waxannan manyan rassa huxu da waqoqin suka yi magana. Anan aka yi bayanin yanayin gudanar da mulki da addini, sai tattalin arziqi da zaman zamantakewa na ‘yan Nijeriya kamar yadda suka bayyana a cikin waqoqin. Babi na biyar shi ne na qarshe da ya qunshi taqaitawa da abubuwan da aka gano, sai shawarwari, rataye da manazarta.

## 5.2 Kammalawa

Nazarin waqoqin Hausa, musamman masu tafiya da zamani, na da matuqar muhimmanci, domin yanaye-yanayen waqoqin da sigoginsu, shi ya sa bincike a kansu zai zama mai fa'ida sosai, musamman idan aka yi la'akari da irin saqon da suke qoqarin isarwa. A yayin nazarin irin waqoqin na farfaganda ta siyasa, an tsinkayi wani saqo da waqoqin ke son sadarwa ga mutane, an gano cewa waqoqin na qoqarin yaxa wata manufa ga zukatan 'yan Nijeriya. Wato waqoqin na neman sauya tunanin jama'a da kuma faxakar da 'yan Nijeriya su fahimci abin da ke wakana kan harkokin mulkin qasa. Da nazarin ya zurfafa, sai aka fahimci cewa saqon waqoqin, ya kai wani matsayi na nuna tawaye da bijire wa shuwagabannin Nijeriya. Haka ne ma ya sa aka kira waqoqin na farfaganda, don suna cusa wa jama'a wani ra'ayi na daban. Don haka, mawaqan kan yi qoqarin aiwatar da waqoqinsu tare da isar sa saqonninsu cikin sauqi ta yadda za a fahimce su sosai.

A wannan bincike mai suna *Farfaganda A Waqoqin Fiyano Na Hausa* an nazarci waqoqin da aka yi a zamanin nan, waxanda ake yi da kayan kixa na zamani irin su fiyano da jita, waxanda suka wanzu sakamakon cuxanyar Hausawa da Turawa da kuma shigowar fina-finan Hausa. Inda aka nazarci farfaganda a ciki. An gano cewa ana samun farfaganda a irin waqoqin nan da ake yi yanzu. Da ma ba a raba Bahaushe da rubuta waqoqi na farfaganda masu tallata jam'iyya da xan takararta. Sai binciken ya gano cewa a yanzu ba ana amfani da farfaganda domin tallata jam'iyya da kwarzanta xan takara kawai ba, ana yin farfaganda kan matsayin mulki da yadda ake gudanar da shi a Nijeriya. Ma'ana ba kamar yadda aka saba yi ba, da a kan yi farfaganda kan manufofin jam'iyya ba.

Binciken ya gano cewa farfaganda da ake yi a siyasance a cikin irin waxannan waqoqi ta jivanci wasu manyan rassa guda huxu, wato waqoqin na tattauna wasu muhimman abubuwa kamar yanayin yadda ake gudanar da mulki a Nijeriya, addini, tattalin arziqin qasa da zamantakewar jama'a.

Mawaqan na fito da hoton siyasar Nijeriya, suna maganar yanayin gudanar da mulkin , inda suke bayyana shi ba a bisa tsarin da ya dace ba. Mahukuntan ba sa alkunya. Waqoqin na fito da illolin shuwagabannin Nijeriya, tare da aibobinsu a yayin gudanar da mulki. Wato yadda ake mulkin danniya da zalunci, tare da handama da babakere. Waqoqin na bayanin yadda mahukunta ke jan zaren mulkinsu yadda ya yi masu daxi, ba su yin aiki tuquru. Suna nuna rayuwar jama'a na tafiya bisa tsarin da bai dace ba. Waqoqin na kira da a yi kishin kai, da sa tunani yayin zaven shuwagabanni, da kuma abubuwan da ke faruwa a qasa na rashin adalci da qeta. Waqoqin na fito-na-fito da hukuma.

Waqoqin na suranta mulkin Nijeriya tun daga samun mulkin, har zuwa qarshensa. Da bayyana abin da ke wakana tsakanin shuwagabanni da mabiyansu. Da abin da ke faruwa tsakanin mahukuntan da muqarransu. Da yanayin yadda ake jujjuya mulki tsakaninsu, yanayin karvi-karva da ake yi na mulkin Nijeriya. Ga halin ko-in-kula da suke nunawa ga mabiyan, bayan an gama yaqin neman zave. Suna rattabo kurakuran da mahukuntan ke tafkawa, tare ba wa jama'a haqurin xauka, da neman agaji da gaggawa. Daxin daxawa, waqoqin na fito da muhimmancin siyasa da yadda ya kamata mulkin dimokraxiyya ya kasance. Da kuma fito da matsalolin

jama'a da yadda mahukuntan ke cin karensu babu babbaka. Waqoqin na maganar siyasar kanta, suna bayyana wa jama'a yadda ake tafi da mulkinsu bai dace ba, ma'ana ana mulkinsu a hagunce. Mawaqan kan nuna gara ma mulkin mallaka da irin nau'in mulkin da ake yi yanzu. Haka kuma, suna zayyana wa jama'a irin son kai na mahukunta. Ba su damu da haqqinsu ba, ta kansu kawai suke yi, sai wanda suke so. Suna nuna wa jama'a matsayinsu a wurin shuwagabanni, sai lokacin zave ya zo, suke da muhimmanci, da ya wuce shi ke nan. Har wayau, mawaqan na kira ga jama'a da su daina jajircewa da nuna gani-kashe-ni kan mahukuntan da ba su damu da mutuncinsu ba. Suna nuna wa a daina ta'addanci tsakani, duk wanda aka kashe, an kashe banza. Mawaqan na tattauna siyasar sosai da sosai ta yadda za su karkato da hankalin mutanen qasar nan zuwa ga bore da tawaye ga gwamnatin Nijeriya.

Bayan haka, waqoqin na maganar addini a qoqarin yaxa manufofinsu. Sukan yi hakan ne inda suke kiran Allah da Manzonsa don neman agaji da mafita. Farfagandar addinin kan fara fitowa tun a farkon waqa, da suke kiran Allah da nuna girmanSa da ikonSa cewa Shi kaxai zai gyara al'amarin. Mawaqan na kiran sunan Allah a yayin da suke neman sauyi da canji na tsarin jagorancin Nijeriya. Ga kuma kyakkyawan yabo ga Ma'aiki SAW. Sannan su roqi Allah Ya qara masu baiwa da basirar tunasar da 'yan Nijerya haqqinsu. Da an tafi, an tafi sai an kira Allah da ManzonSa. Sukan kira Ubangiji sosai da sosai, musammam da kyawawan sunayenSa, sukai kokensu ga Allah na neman agaji, na ganin an samu sauyi a yanayin siyasar Nijeriya. A qoqarin mawaqan na kira ga neman canji, sukan kawar da tsoro da wata fargaba, su zayyana saqonsu sosai ya yadda jama'a za su fahimta.

A yayin maganar tattalin arziqi, suna zayyana ma'adanai da albarkar qasa da Allah Ya yi wa Nijeriya, kamar qasar noma mai kyau da damina mai albarka da sauransu. Su nuna yadda ake sarrafa shi bai dace ba. Kuma duk da waxannan ni'imomi, babu wani abin a-zo-gani da ake yi wa 'yan cikinta. Mahukuntan kansu kawai suka sani, ba sa kula kowa. Suna bayyana albarkatun qasa da za a iya sarrafawa a taimaki jama'a amma an gaza. Mawaqan na fito da irin baiwar ta arziqi da Allah SWT Ya yi wa Nijeriya ta ko'ina, a kan komai. Amma ba a yin yadda ya kamata wajen sarrafa su. Har sukan nuna wasu qasashen da Nijeriya ta fi komai kuma ta riga samun 'yanci, yanzu sun xarar mata, ba a ma haxawa. Suna hakan ne don su sauya tunanin al'umma.

Yanayin zamantakewar kamar yadda suke fitowa a cikin waqoqin babu daxi. Don waqoqin na bayyana halin wuya da kaico da ake ciki kuma mahukuntan ba su damu ba, jin daxinsu kawunansu. Buqatarsu kawai su tara kuxi a cikin gida da wajenta. Suna nuna yadda talakawa ke gudun shuwagabannin idan wahala ta ishe su, musamman lokacin zave. Waqoqin na bayyana yadda talauci ya dami kowa, an rasa yadda za a yi. Yanayin zamantakewar sukan nuna babu daxi. Babu tsaro a qasa, sata da fashi da makami sun yawaita. Ilmi babu inganci, babu wadattun makarantu. Harkar lafiya ma a baya, babu asibitoci da magunguna masu kyau. Ga ta'addanci da 419. Abun dai babu daxin ji da gani.

Duka waqoqin da aka yi nazarinsu, sun qunshi ginshiqan abubuwan nan guda huxu. Domin an gano cewa manufar waqoqin xaya don yaxa farfaganda, na qoqarin sauya tunanin jama'a zuwa ga bore da tawaye ga gwamnatin Nijeriya. An gano farfaganda ta siyasa a yanzu ta wuce kan jam'iyya ta kai wani matsayi na tunkarar wasu abubuwa kai tsaye.

An zavi waxannan waqoqi ne saboda an dubi fitattun mawaqa ne, ga su da fasaha da zalaqa ta shirya waqa, da kuma suka rayu a mabambantan wurare. Kuma waqoqin sun yi fice a ko'ina saboda tasirinsu da karvuwarsu ga jama'a. Ga shi kuma suna ba da gudunmuwa iri xaya, wajen ci gaban siyasa da mulkin dimokraxiyya a qasa. Wannan ya daxa nuna cewa adabi matsokaci ne rayuwar al'umma. Don mawaqan na tsokaci kan abubuwan da suka dame su, da sauran jama'a a cikin waqoqinsu. Waqoqin na farfaganda, suna faxin qorafin jama'a, suna bayyanawa qarara abin da ke damun jama'a. Aikin ya tabbarar da hasashen adabi hoto ne rayuwar jama'a.

A qoqarin mawaqan na tallata manufarsu, suna gargaxi ga jama'a da su hankalta, su lura da abin da ke wakana a qasa. Don suna fito da ginshiqan abubuwa ta fannin tattalin arziqi, da zamantakewar jama'a da addini ma siyasar kanta, su tattauna su, don su qara jawo hankalin jama'a da su dubi mulkin nan da idon basira, su duba dacewa ko rashinta a cikinsa, wanda suke bayyana rashin dacewar da rashin shuwagabanni adalai. Haka kuma, waqoqin na ankarar da mutanen Nijeriya, zuwa ga manufa da kuma kulawa da abin da ake son su gane.

An kuma fahimci cewa mawaqan na qoqarin qulla waqoqinsu ta hanyar zaven kalmomi da sarrafa su ta yadda kowane mawaqi yake ganin ya dace da manufofinsa. Ga amfani da adon harshe don burgewa. Sai dai wani hanzari ba gudu ba, salon tsarin wasu waqoqin ya sava da yadda aka saba a yau da kullum, akwai 'yan bambance-bambance musamman a tsarin baitoci.

Wani abin burgewa game da waxannan waqoqi shi ne, suna taimakawa wajen tsuma jama'a, su motsa su don ganin an samu sauyi a yanayin siyasar qasar nan. Duk da dai ba a samun yadda ake so, suna agazawa don jama'a na nuna rashin amincewa da goyon baya a zavuvvukan da suka gabata a Nijeriya. Har aka samu tarzoma da taqaddama a wasu sassa na qasar nan. Duk da dai ba ta canza zani ba, amma dai a ce gara da aka yi, ake kuma cikin yi a kullum, har Allah Ya sa a samu yadda ake so.

Wannan bincike ya tabbatar mana da akwai waqoqin farfaganda ta siyasa. Watakila haka ya faru, saboda damuwar da jama'a suke ciki, shi ya sa ake yawaita samuwar waqoqi masu wannan jigo. An zavi waqoqin daga mabambantan mutane da suka rayu a wurare daban-daban, don a gano irin hikimar kowane mawaqi, don mawaqan da aka zavo don nazarin ayyukansu, mawaqa ne da suka ba da gudummuwa sosai wajen samuwar waqoqin siyasa na zamani.

Waxannan waqoqin na zamani, cike suke da abin da ya shafi farfaganda zuwa ga mutanen Nijeriya kan yanayin yadda ake mulkin su, tunda waqoqin na zaburar da tunzura jama'a zuwa ga bore da tawaye. Marubutan kan fito da ginshiqan abubuwa da suka shafi rayuwar al'umma, sai su kafa hujja da su, don su sauya tunanin al'umma. Haka kuma, waqoqin na faxakar da jama'a da wayar masu da kai kan irin shuwagabannin da ya kamata su zava, da jajircewa wajen yaqin neman sauyi. Waqoqin nan, sun tabbatar da cewa 'yan Nijeriya ba sa cikin hayyacinsu, suna neman agaji daga kowace hanya.

Binciken ya yi amfani da ra'in *Isar Da Saqo* ya gano cewa manufofin mawaqan shi ne qoqarin canza tunanin mutane da jan hankalin zuwa ga bore da tawaye ga gwamnatin Nijerya. Tunda

ra'in na magana a kan manufa ta mai wani rubutu ko magana ga wata al'umma da aka yi abin domin ta, tare da buqatar ganin sakamako na canza xabi'un mutane.

### 5.3 Shawarwari

Ana fata waqoqin su zama wani tsani da masu mulki za su hau ya zamanto sun gyara mulkinsu. Don a cikin waqoqin ana faxa masu koke-koken jama'a. Kuma waqoqin na faxakarwa ne ba don nishaxi ba.

Da so samu ne, da ba haka aka tafiyar da mulkin Nijeriya ba. Da an yi shi yadda zai dace da rayuwar al'umma. Babu tantama, ci gaban kowace al'umma ya dogara ne ga shuwagabanninta waxanda suke da alhakin kula da kuma tafiyar da harkokin qasa, don samun ci gada da zaman lumana ga 'yan qasa baki xaya. Idan kuwa haka ne, ya wajaba ga shuwagabannin Nijeriya su yi qoqarin adalci da kamanta gaskiya, tare da tafiyar da sha'anin mulki yadda ya kamata.

Yana da kyau, shuwagabannin su yi qoqarin farfaxo da tattalin arziqin don amfani da kyautata rayuwar kowa. A sarrafa shi yadda ya dace. A fitar da jama'a daga halin da suke ciki. Haka kuma, su kawar da qabilanci, addini, da ma vangaranci, a inganta rayuwar jama'a.

A dubi siyasar da idon basira, a aiwatar da ita da 'yancinta. A ba wa jama'a haqqinsu da damarsu ta zaven wanda suke so, suke ganin ya cancanta ya mulke su. Yin hakan zai taimaka wajen samun zaman lafiya da jin daxi a faxin qasa baki xaya. Yanayin zamantakewar ya zama mai daxi. A wadata al'umma da abin da ya kamace su, wato abubuwan da suka wajaba qasa ta

yi wa xan qasarta, a tabbata an yi wa kowa da kowa, ba wasu ‘yan tsiraru ba. Su ma marubuta waqoqin, ya kamata a qara ba su qwarin gwiwa, ma’ana a yi masu jinjina da suke jajircewa wajen ganin an samu sauyi a siyasar Nijeriya. Kuma ya dace su ci gaba da rubuta irin waqoqin, don amfanin qasa da mutanenta. Suna faxakar da mutane, da wayar masu da kai kan harkokin mulkin dimokraxiyya. Don samuwar irin waqoqin, zai taimaka qwarai wajen kawo canji a siyasar Nijeriya. Ya kamata a cika faxar jama’a da suke cewa ‘Siyasa rigar ‘yanci’.

Ya kamata a riqa aiwatar da harkokin siyasa yadda aka tsara. Ma’ana a daina maguxin zave, wanda ya ci, kuma ya cancanta a ba shi. Sannan a kawar da cin hanci da rashawa. Shari’a a kan kowa ta faxa, ta yi aiki. A kawar da makarantu masu zaman kansu, sai na gwamnati. Kowa da kowa ya ilmanta a nan. Haka ma vangaren asibiti, kowa ya je na gwamnati. Yin hakan, ina ga zai taimaka qwarai ci gaban qasa da al’ummarta.

**Manazarta**


Abba, A. (2000). The Significance Of The Northern Element Progressive Union, (NEPU) In The Politics Of Nigeria: 1950-1960. PhD Dessertation. Department Of History, Ahmadu Bello University, Zaria.

Adedimeji, M.A. (2007). The Language of Politics In Nigeria: Conflicts And Resolution. *Fais Journal of Humanities* No.6 Vol. 3. Bayero University, Kano.

Adu'a, B.I. (2007). Fa'idoji Da Illolin Waqoqin Siyasa. Kundin Digiri Na Xaya. Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usman Xan Fodio, Sokoto.

Ajiwa, H. (1998). Rubutattun Waqoqin Siyasa A Zamanin Shirin Miqa Mulki Na Abacha. Kundin Digiri Na Xaya. Sashen Harsunan Nijeriya Da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Almajir, T. S. (2006). Zamantakewar Hausawa Matasa A Qarqashin shirin Game-Duniya. *Harshe 4,* Journal Of African Languages. Department Of Nigerian And African Languages. Ahmadu Bello University, Zaria.

Aminu, H. (1991). Enlightment And Propaganda As Theme In *Wasan Marafa.* A Seminar Paper Presented At The Department Of Nigerian And African Languages. Ahmadu Bello University, Zaria.

Amin, M.L. (1992). Poetry and Political Ideology: A Glimpse at Arewa Jumhuriya Ko Mulukiya of Sa'adu Zungur. A Seminar Paper Presented At Nigerian And African Languages. Ahmadu Bello University, Zaria.

Amin, M. L. (1993). Ra'ayin Sauyi A Waqoqin Sa'adu Zungur. *Dandalin Hikima 2* Mujallar Qungiyar Marubuta da Manazarta Waqoqin Hausa Ta Tarayya.

Amin, M. L. ( 2000) Waqoqin Jihadi A Goshin Qarni Na Ashirin Da Xaya. *Hausa Studies* Vol. II No. 2. Department Of Nigerian Languages, Usman Xanfodio University, Sokoto.

Amin, M. L. (2001). The Political Ideology Of Sa'adu Zungur As Potrayed In In Arewa Jumhuriya Ko Mulukiya. *Nigerian Educational Forum Journal Of The Institute Of Education*. No 1, Vol. 17. Ahmadu Bello University, Zaria.

Amin, M. L. (2004). Radicalism In The Poetry Of Sa'adu Zungur. *Journal Of Arts And Humanities*. No 1, Vol.1. International Research And Development Institute.

Amin, M. L. (2006). Reformism As A Theme In Hausa Religio-Political Poetry. *Journal Of African Cultural Studies* Vol.18 No. 2. A Paper Presented At The West Africa Seminar Of The Anthropology Department, University College, London.

Amin, M. L. ( 2008.) Globalization And Cultural Synchronization In Hausa: A Literary Reflection. A Seminar Paper Presented At The Department Of Nigerian And African Languages. Ahmadu Bello University, Zaria.

Amin, M.L. (2008) Popular Culture And Political Resistance In Nigeria: A Glimpse At Contemporary Hausa Music. Department Of Nigerian And African Languages. Ahmadu Bello University, Zaria.

Anifowase, R. and Enemuo, F. (ed). (1999). *The Element Of Politics*. Sam Iroanusi Publications. Lagos.

Appadorai, A. (1974). *The Substance Of Politics*. University Press. New Delhi.

*A Student Dictionary*. ( 2007). Canadian Edition. Sullivance Island. USA.

Assuyuxi, I.J. (2008). *Tarihul Khulafa.* Darul Fikir. Beirut Lebanon.

Auta, A.L. (2008). Rubutattun Waqoqin Hausa Na Faxakarwa A Qarni Na Ashirin. Kundin Digiri Na Uku. Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Baban Zara, M. H. (2010). Short Biographies Of Selected Hausa Political Poets. *FAIS Journal Of Humanities*. No.1. Vol.4. Bayero University, Kano.

Bargery, G.P. (1933). *A Hausa-English Dictionary And English-Hausa Vocabulary 2nd Edition*. Ahmadu Bello University Press, Zaria.

Barista, M.L (2011). Waqoqin Aminu Ladan Abubakar: Alan Waqa. Iya Ruwa Pulishers, Kano.

Bayero, A. Y. (2004). Rubutattun Waqoqin Nasiha: Wani Vangare Ko Kuwa Sauyi Salo A Cikin Rubutattun Waqoqin Hausa Na Wa'azi? *Algaita Journal Of Current Research In Hausa Studies*. No.3. Vol.1 Department Of Nigerian Languages. Bayero University, Kano.

Bello, A.S. (2009). Nazarin Waqar Baubawan Burmi Ta Aminu Ladan Abubakar (ALA). Takarda Da Aka Gabatar A Wurin Taron Qarawa Juna Ilmi Na Tsangayar Harsuna. Kwalejin Ilmi Ta Tarayya, Zaria.

Bello, A.S. (2011). Gudunmuwar Adabin Hausa A Fagen Ci Gaban Siyasa Da Tabbatar Da Dimokraxiyya A Najeriya: Nazarin Waqar 'Dimokraxiyya Ta Aminu Ala. Takardar Da Aka Gabatar A Taron Qarawa Juna Ilmi Na Tsangayar Harsuna. Kwalejin Ilmi Ta Tarayya, Zaria.

Berger, A.A (1995). *Cultural Criticism: A Primer Of Key Concepts. Foundation Of Popular Culture*. Sage Pulications. New Delhi.

Binta Salma, S. M. (1997). The Language Of Poetry: A Stylistic Study Of Selected Poems Of Soyinka And Osundare. M.A Thesis. Department Of English And European Languages, Bayero University, Kano.

Binta, A.S (2011). Tasirin Kayan Kixan Zamani A Kan Kaxe-Kaxen Hausawa Na Gargajiya. Kundin Digiri Na biyu. Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya Da Kimiyyar Harshe. Jami'ar Bayero, Kano.

Birniwa, A. H. (1987). Conservatism And Dissent: A Comparative Study Of NPC/NPN And NEPU/PRP Hausa Political Verse From Circa 1946-1983. Kundin Digiri Na Uku. Jami'ar Usman Xanfodio, Sokoto.

Birniwa, H. A. (2004). Siffantawa A Cikin Waqoqin Siyasa. *Xunxaye Journal Of Hausa Studies* No.1 Vol.1. Department Of Nigerian Languages. Usman Xanfodio University, Sokoto.

Birniwa, H. A. (2005). Tsintar Dame A Kala: Matsayin Karin Magana A Cikin Waqoqin Siyasa. *Xunxaye Journal Of Hausa Studies* No.2. Vol 1. Department Of Nigerian Languages. Usman Xanfodio University, Sokoto.

Birniwa, H. A. (2010). Matsayin Rubutattun Waqoqin Siyasa A Wajen Yaqin Neman Zave: Misalai Daga Jumhuriya Ta Xaya Da Ta Biyu. Takardar Da Aka Gabatar A Taron Qara Wa Juna Sani. Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Umaru Musa 'Yar'adua, Katsina.

*Britannica Concise Encyclopedia.* (2003). USA.

*Chambers 21st Century Dictionary.* (2001). Revised Edition. Allied Chambers (India) Limited, New Delhi.

Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya (2006). *Qamusun Hausa.* Jami'ar Bayero, Kano.

*Concise Oxford English Dictionary.* (2006). Eleventh Edition. Oxford University Press, India.

Crowder, M. (1962). *The Story Of Nigeria.* Faber And Faber Limited, London.

Dambo, J. B. (1999). Farfaganda A Cikin Rubutattun Waqoqin Hausa. *Hausa Studies*. No.1,Vol.1. Department Of Nigerian Languages, Usman Xanfodio, University, Sokoto.

Darah, G.G. (ed). (2008). *Radical Essays On Nigerian Literatures*. Malthouse Press Limited. Lagos.

Xangambo, A. (2008). *Xaurayar Gadon Fexe Waqa (Sabon Tsari).* Amana Publishers Limited, Zaria.

Xangulbi, A. R. (2003) Siyasa A Nijeriya: Gudunmuwar Marubuta Waqoqin Siyasa Na Hausa Ga Kafa Dimokraxiyya A Jumhuriya Ta Huxu Zango Na Farko. Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usman Xanfodio, Sokoto.

Xan'illela, A. (2010). Rubutattun Waqoqin Siyasa: Nazari A Kan Jihohin Sakkwato Da Kebbi Da Kuma Zamfara. Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usman Xanfodio, Sokoto.

Xanqwari, M. L. (2000). Ethics In Hausa Poetic Tradition: A Historical Survey. Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Harsunan Nijeriya Da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Xiso, A. H. (1997). Zambo Da Yabo A Matsayin Dabarun Jawo Hankali A Rubutattun Waqoqin Siyasa. Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Xan'asabe, K.M da Wasu, (2008). Muhimmancin Mawaqa Ga Ci Gaban Siyasar Nijeriya: Tasirin Waqar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba. *Zaria Journal Of Linguistics And Literary Studies*. No.1 Vol .2. Zaria.

*Encyclopedia Americana.* (1829). International Edition: First Published.

Danbury, Connecticut.

Falola, T. et al. (1991). *History Of Nigeria 3*: *Nigeria In The Twentieth Century.* Longman Nigeria Plc, Lagos.

Falola, T. et al. (2008). *A History Of Nigeria.* Cambridge University Press, Newyork.

Funtua, A. I. (2003). Waqoqin Siyasa Na Hausa A Jumhuriya Ta Uku: Yanaye-Yanayensu Da Sigoginsu. Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Funtua, A.I. (2011). Manufar Waqa A Siyasa: Ire-Iren Jigogin Waqoqin Siyasa Na Hausa. *Algaita Journal Of Current Research In Hausa Studies* Vol. 2 No. 1. Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero, Kano.

Furniss, G. (1995). *Ideology In Practice: Hausa Poetry As Exposition Of Values And Viewpoints.* University Press, Edinburgh.

Furniss, G. (1996). *Poetry, Prose And Popular Culture In Hausa*. Edinburgh University Press Limited, Edinburgh.

Gaya, A. M. (1998). Tsarin Mulkin Gargajiya Jiya Da Yau Musamman A Kano. Kundin Digiri Na Biyu.Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero. Kano.

Gusau, S. M. (2003). *Jagoran Nazarin Waqar Baka*. Benchmark Publishers Limited, Kano.

Gusau, S. M. (2008). *Waqoqin Baka A Qasar Hausa: Yanaye-Yanayensu Da Sigoginsu*. Benchmark Publishers Limited, Kano.

Gusau, S. M. (2008). *Dabarun Nazarin Adabin Hausa.* Benchmark Publishers Limited, Kano.

Gusau, S. M. (2010). Rawar Da Ta Kamata Marubuta Waqoqin Hausa Su Taka Ga Kyautata Rayuwar Al'umma. Takarda Wadda Aka Gabatar A Taron Bita Wadda Hukumar Bunqasa Harkokin Matasa Ta Jihar Kano Ta Shirya Wa Marubuta Da Makaxa Waqoqin Hausa A Gidan Mambayya Na Malam Aminu Kano, Kano. Daga Juma'a 19/02/2010 Zuwa Lahadi 21/02/2010.

Gusau, S.M. (2010). Hanyar Nazarin Waqar Baka Bahaushiya A Taqaice. Takarda Wadda Aka Gabatar A Taron Qara Wa Juna Ilmi Tsakanin Malamai Da Xalibai, Sashen Hausa, Jami'ar Bukar Abba Ibrahim, Damaturu, Jihar Yobe. Laraba 10/12/2010.

Gusau, S.M. (2011). Bitar Littafin Waqoqin Aminu Ladan Abubakar: Alan Waqa Na Muhammad Lawal Barista (2011). Takarda Wadda Aka Gabatar A Taron Gabatar Da Littafin Da Aka Yi A Musa Abdullahi Auditorium, Sabuwar Jami'ar Bayero, Kano. 15/01/2011.

Gusau, S.M. (2011). Ga Fili Ga Mai Doki: Wata Mahanga Ga Mawaqa Da Makaxan Hausa. Takarda Wadda Aka Gabatar A Taron Qara Wa Juna Sani Na Haxin Gwiwa Tsakanin Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano Da Hukumar Tace Finafinai Da Xab'i Ta Jihar Kano. Alhamis 07/04/2011.

Gusau, S.M. (2011). Taqaitaccen Tarke A Kan Waqar *Jami'a* Ta Aminu Ladan Abubakar. Takarda Wadda Aka Gabatar A Taron 'Waqa A Bakin Mai Ita' Wanda Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano Ta Shirya. Laraba 13/07/2011.

Gusau, S.M. (2013). Bayani Kan 'Ranar Mawaqan Hausa'. Takarda Wadda Aka Gabatar A Taron 'Ranar Mawaqan Hausa' Na Farko Wanda Aka Yi A Taskar Ala Global, Guda Abdullahi Street, Farm Centre, Near Country Mall, Kano. Talata 01/01/ 2013.

Gusau, S.M. (2013). Mizani Tsakanin Waqoqin Hausa Na Baka Da Rubutattu. Takarda Wadda Aka Gabatar A Taron Qara Wa Juna Ilmi Na Qasa Kan Harshe Da Adabi da Al'adun Hausawa Na Farko Wanda Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano Ta Shirya A Gidan Mambayya, Kano. 14-19 Ga Janairu.

Hadiza, L. A. (2000). The Soldier-Poet: A Study Of The Poetry Of General Mamman Jiya Vatsa. M.A Thesis. Department Of English Language And European Languages, Bayero University, Kano.

Hamza, M. K. (2011). Nazarin Salon Sarrafa Harshe A Waqoqin Aminuddeen Ladan Abubakar (ALA). Kundin Digiri Na Xaya. Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usman Xanfodio, Sokoto.

Hussaini, B. (2007). Haruna Aliyu Ningi Da Waqoqinsa. Kundin Digiri Na Xaya. Sashen Harsunan Nijeriya Da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

http://en.wikipedia.org/wiki/White-propaganda. (Visited 25th April, 2012).

http://en.wikipedia.org/wiki/Black-propaganda. (Visited 25th April, 2012).

http://en.wikipedia.org/wiki/Grey-propaganda. (Visited 25th April, 2012).

http://orwell.ru/library/articles/frontiers/english/e-front. (Visited 19th April, 2010)

http://tags.library.upenn.edu/project/36806. (Visited 19th April, 2010).

http://schools-wikipedia.org/wp/p/Propaganda.htm (Visited 1st April, 2011).

Ibrahim, G. I. (2009). Nazari A Kan Waqoqin Jam'iyyar PSP A Kano. Kundin Neman Babbar Diflomar Hausa Ta Gaba Da Digiri. Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Ibrahim, M. S. (1982). Rubutattun Waqoqin Hausa Kafin Zamanin Shehu Usman Xanfodio. *Harsunan Nijeriya XII*. Centre For The Study Of Nigerian Languages. Bayero University, Kano.

Ibrahim, Y. Y. (2009). Selected Political Statements On Early Muslim Leaders And The Lessons For Nigerian Elites. *Kada Journal Of Liberal Arts*. Kaduna State University, Kaduna.

Idris, Y. (2010). Waqoqin Addini Na Siyasa: Nazarin Waqoqin Emmanuel Wise Mai Molo. Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Harsunan Nijeriya Da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Imran, A.L. (2008). Jigo Da Salon Waqoqin Aminu Ala. Kundin Digiri Na Xaya. Sashen Harunan Nijeriya Da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

*International Encyclopedia Of The Social Sciences.* (1968).

Isyaku, S.M. (2007). Kwatanci Da Bambanci Tsakanin Talla Ta Hausa Da Ta Ingilishi. Kundin Digiri Na Xaya. Sashen Harsunan Nijeriya Da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Jumare, M. S. (2007). Tasirin Farfaganda A Tallar 'Yan Siyasa. Kundin Digiri Na Xaya. Sashen Harsunan Nijeriya Da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Junaidu, S. W. (2001). Jihad Poetry In Arabic, Fulfulde, And Hausa. *Fais Journal Of Humanities* No.4. Vol.1. Bayero University, Kano.

Kirk-Greene, A. et al. (1981). *Nigeria Since 1970: A Political And Economic Outline.* Hodder And Stoughton, Great Britain.

Lubabatu, M. (2007). Waqoqin Siyasa Na ANPP'. Kundin Digiri Na Xaya. Sashen Harsunan NjieriyA Da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Lasswell, H.D. (1977). *On Political Sociology.* University Of Chicago Press, Chicago.

Mannura, U. (2008). Farfaganda A Wasan Kwaikwayon Rediyo. Kundin Digiri Na Xaya. Sashen Harsunan Nijeriya Da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Mashi, M. B. (1986). Waqoqin Baka Na Siyasa: Dalilinsu Da Tasirinsu Ga Rayuwar Hausawa. Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Muhammad, D. Y. (2003). Ginuwar Salo A Waqoqin Musulunci Na Hausa Daga Qarni Na 17 Zuwa Na 20. Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Muhammad, X. (1977). Individual Talent In The Hausa Poetic Tradition: A Study Of Aqilu Aliyu And His Art. PhD Dessertation. University Of London, School Of Oriental And African Studies.

Muhammad, X. (1978) Waqa Bahaushiya. *Studies In Language And Literature In Hausa.* The First Hausa International Conference. Bayero University, Kano.

Muhammad, X. (1979). Interaction Between The Oral And The Literate Traditions Of Hausa Poetry. *Harsunan Nijeriya III*. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero, Kano.

Muhammad, X. (1981). Waqe A Zube. Muqala Da Aka Gabatar A Makon Hausa Na Qungiyar Marubuta Da Manazarta Waqoqin Hausa Don Ta'aziyyar Abubukar Imam. Jami'ar Usman Xanfodio, Sokoto.

Muhammad, J. (2006). Waqa A Matsayin Makami Na Canza Xabi'un Al'umma. Kundin Digiri Na Farko. Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usman Xan Fodio, Sokoto.

Mukhtar, I. (2006). Gudunmuwar Rubutattun Waqoqin Hausa Wajen Adana Tarihin Siyasar Nijeriya. *Algaita Journal Of Current Research In Hausa* No.4. Vol.1. Department Of Nigerian Languages Series V, Bayero University, Kano.

Malumfashi, A. I. (2004). Mun Gaji Da Qyanqyasa RanaNa Kashewa:Masharin Hawayen Xaliban Islamiyya. *Harshe 2. Jornal Of African Languages.* Sashen Harsunan Nijeriya Da Afirka. Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Musa, I. I. (2007). Nazarin Yabo Da Zambo A Rubutattun Waqoqin Siyasa Na Haruna Aliyu Ningi. Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

*New Encyclopedia Britannica*. (1768). Vol. 9 Micropedia: Ready Reference: 15th Edition. USA.

Ofoegbu, R. (1980). *Foundation Course In International Relations For African Universities.* George Allen &Unwin Limited, London.

*Random House Webster's College Dictionary*. (2001). Random House, NewYork.

Sa'id, B. (1995). The Reaction Of Hausa Poets To Western Civilisation. *Harsunan Nijeriya XVII*. Centre For The Study Of Nigerian Languages.

Bayero University, Kano.

Sarki, A. S. (1999). Tasirin Rubutattun Waqoqin Hausa Dangane Da Qoqarin Canza Xabi'u. *Jakadiya: A Journal Of Researches In African Languages And Literature* No.1. Vol.1. Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Sarvi, S.A. (2007). *Nazarin Waqen Hausa*. Samarib Publishers, Kano.

*Shorter Oxford English Dictionary On Historical Principles.* (2003). Vol. 2 Fifth Edition N-Z. Oxford University press, USA.

Speier, H. (1952). *Social Order And The Risk Of War.* George W. Stewart Publishers, New York.

Szanzo, G. H. (1940). *Theater And Propaganda.* University Texas Press, London.

*The New Age Encyclopedia* (1976). Vol.15. Lexicon Publications, USA.

*The New Book Of Knowledge.* (2006) Vol. 15 (P). Scholarstic

Library Publishing, Danbury, Connecticut.

*The New International Webster's Comprehensive Dictionary Of The English Language.* Encyclopedic Edition. Trident Press International USA.

*The 21st Century Webster's International Encyclopedia*. (2003). First Edition. Trident Press International, Columbia.

Tofa, B.O (2011) *Arewa: Daga Ina Zuwa Ina?* Clear Impression, Sharaxa, Kano.

Tsoho, M.Y. (2013) Adabi Da Harkokin Siyasa: Bijirewa A Waqar Shegiyar-Uwa Mai Kashe 'Ya'Yanta PDP Ta Haruna Aliyu Ningi. Takarda Wadda Aka Gabatar A Taron Qasa Na Farko Kan Harshe Da Adabi Da Al'adu. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Umma, A. (2011). Nazarin Adon Harshe A Wasu Rubutattun Waqoqin Siyasar

Jumhuriya Ta Uku. Takarda Da Aka Gabatar A Sashen Harsunan Nijeriya. Jami'ar Umaru Musa 'Yar'adua, Katsina.

Uchi, D. I. (1973). Party Political Activity And The TIV Revolts: 1950-1966. B.A History. Department Of History, Ahmadu Bello University, Zaria.

Wurma, A. G. (1999). Waqa Rubutacciya: Muhimman Hanyoyin Nazarinta Da Abubuwan Da Ke Vata Ta. *Jakadiya: A Journal Of Researches In African Languages And Literature* No.1 Vol.1 Department Of Nigerian And African Languages. Ahmadu Bello University, Zaria.

Wurma, A. G. (2008) Kalma Xaya Ma'ana Tuli. *Algaita: Journal Of Current ResearchesIn Hausa Studies.* Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero, Kano.

Yahaya, I.Y. (1988). *Hausa A Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa.* NNPC, Zaria.

Yahaya, (2000). Sharhi A Kan Rubutattun Waqoqin PDP. Kundin Digiri Na Xaya. Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Yakubu, A.M. (1999). *Sa'adu Zungur: An Anthology Of The Social And Political Writings Of A Nigerian Nationalist*. Nigerian Defence Academy Press, Kaduna.

Zainab, I. (2013) Gudunmuwar Mawaqan Hausa Ga Ci Gaban Arewacin Nijeriya: Nazarin Waqar 'Ajanda' Ta Haruna Aliyu Ningi. Muqala Da Aka Gabatar A Taron Qasa Na Farko A Kan Harshe, Adabi da Al'ada. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

**Hira Da:**

Aminu Ladan Abubakar ranar Juma'a 13/07/2012

Jibrin Muhammad Jalatu ranar Laraba 17/10/2012 da Litinin 22/04/2013

Haruna Aliyu Ningi ranar Lahadi 15/07/2012 da Juma'a 28/09/2012 da Lahadi 21/04/2013

AbdulAziz Abdullahi Ningi ranar Alhamis 19/07/2012

Muhammad Sani Aliyu ranar Juma'a 28/09/2012

Sanusi Anu a ranar Alhamis 18/04/2013

Hajiya Fantimoti a ranar Alhamis 18/04/2013

Farfesa Abdulqadir Xangambo a ranar Talata 23/04/2013

Ibrahim Ibrahim a ranar Talata 23/04/2013

Rabi'u Dalle a ranar Laraba 24/04/2013

Maryam Sangandale a ranar Laraba 24/04/2013

**Tambayoyin Da Aka Yi Masu**

iv. Dalilin da ya sa aka yi waxannan waqoqi?

v. Mene ne taqaitaccen tahirin mawaqi?

vi. Yaya matsayin waqoqin nan suke a gare ka?

vii. Mawaqa nawa kuke da su a garinku?

viii. Yaya kake aiwatar da waqoqin nan na fiyano?

**Rataye**

**Waqar Baubawan Burmi**

**Ta**

**Aminu Ladan Abubakar (ALA)**

Jagora: Baubawan burmi.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Baubawan burmi.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Baubawan burmi

kasassavarmu ce

kan zaven jagora, iye iye.

Amshi: Baubawan burmi

kasassavarmu ce

kan zaven jagora, iye iye.

Jagora: Allah Malikal Mulki,

Tu'util Mulka Mantasha'u akan mulki.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Allah mun yi zaman dirshan

tamkar fitila a lokon alkuki.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Sai a kaxa mu a raurayar,

Allah namu na bukatar jagora, iye iye.

Amshi: Baubawan burmi

kasassavarmu ce

kan zaven jagora, iye iye.

Jagora: Salli Alaika Rasulullah

Xan Amina ma fi tsarkin jagora.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Alihi har a sahaba

masu biyar biyar xafa gun jagora.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Mai alfarma da adala

Ahmadu hamidun fitayyen jagora, iye iye.

Amshi: Baubawan burmi

kasassavarmu ce

kan zaven jagora, iye iye.

Jagora: Allah ka san kukana

ka sanni hujjar zubar da hawayena.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Ai bauta ce tac canza

ta xauko salo da tsari mummuna.

Amshi: Iye Iye

Jagora: Mun bar mulkin mallaka,

kama-karya a yau shi muka xora, iye iye.

Amshi: Sauyin sauyi muke so,

sassaucin tausasawa.

Amshi: Ala mai faxakarwa,

daina kukan kokawa,

Allah ne ke sakawa

sannan Shi ke cirewa,

in ya so zai canzawa

ba mai ikon hanawa.

Amshi: Sauyin sauyi muke so,

sassaucin tausasawa.

Jagora: Dole in koka da tsiwa,

dubi qasar nan Arewa,

ba ilmi talakawa,

ba mu da aikin tavawa,

mun zama Jujin zubawa,

tarkacen tarkatawa.

Amshi: Baubawan burmi,

kasassavarmu ce

kan zaven jagora. Iye iye.

Jagora: Dangi a duba mani hanya,

da can da muna a mulkin mallaka.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: wahala dai aka ba bawa

amma duk tsiya abinci a ba ka.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Yanzu ko gadonmu talauci,

ai kuxarsa ta fi dukanka da gora. Iye iye.

Amshi: Baubawan burmi,

kasassavarmu ce

kan zaven jagora. Iye iye.

Jagora: Talauci shi muka gado,

jahilci ko ya zamanto rigarmu.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Ba mu da ikon yin mulki,

balle mu ciro masharin kukanmu.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: mun xore da tumasanci,

mabarata muke a hannun jagora. Iye iye.

Amshi: Baubawan burmi

Kasassavarmu

kan zaven jagora. Iye iye.

Jagora: Dangi a waiwaya a duba,

makarantunmu daban ne da na ‘yayansu.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: La’akari da abincinsu,

kama har zuwa ruwan da suke sha su.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Kai duba ga makwancinsu

daga nan zaka gane mugun jagora,iye iye.

Amshi: Baubawan burmi,

kasassavarmu ce

kan zaven jagora,iye iye.

Jagora: Sannan ba sa alkunya

da an doka tamburan nan na siyasa.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: kunya ba tsoron Allah

su yi oda ta atampar nan sosa.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Sun mammanna gumakansu,

su rarraba mu dauke su mu xaura. Iye iye.

Amshi: Sauyin sauyi muke so,

sassaucin tausasawa.

Amshi: Allah aka kai wa

qarar duk mai cutarwa,

kokena Kai Na kai wa,

shugaba mai cutawa,

ka tsare talakawa,

kai muke sujjadawa.

Amshi: Sauyin sauyi muke so,

sassaucin tausasawa.

Jagora: mun azabtu da vawa,

qara kuka da tsuwa,

mun shagaltu da yunwa,

mun dushe da qishirwa,

mun makance da tsowa,

Allah Kai ke sauyawa.

Amshi: Baubawan burmi,

kasassavarmu ce

kan zaven jagora, iye iye.

Jagora: Su ke tarkata yaranmu

da makamai suna ta saran junansu.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: In da alamar adalci,

to, me zai hana su cakuxa ‘yayansu.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Kayan maye suka ba su,

su hau gidan mutum su faxa shi da sara, iye iye.

Amshi: Baubawan burmi,

kasassavarmu ce kan zaven jagora,iye iye.

Jagora: Kuxin abinci suke ba ku

an maishe ku sai ka ce dabar kiwo.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Kuxi a dumtse su a watsa

ku bi kunna ta wawaso har ku ji ciwo.

Amhi: Iye Iye.

Jagora: Angulu za dai fa a koma,

gidanki dai na tsamiya daina gadara, iye iye.

Amshi: Baubawan burmi,

kasassavarmu ce

kan zaven jagora, iye iye.

Jagora: Allah wanga kashin mulki

ya yi kama guda da ka shin dankali.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Na samma ya danne na qasa,

in ya so numfashi babu dalili.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Jin dadinsu kawunansu,

alfalmarsu iyalensu suna kibra, iye iye.

Amshi: Baubawan burmi,

Kasassavarmu ce

kan zaven jagora, iye iye.

Jagora: Allah kai kabban iko

in qi abin gudu da fatar bakina.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Allah kai kabban hikima

in yi ragargaza da harshen bakina.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: In faxakar gun al'umma

don su yi qyamata ga mulki na gadara, iye iye.

Amshi: Baubawan burmi,

kasassavarmu ce

kan zaben jagora, iye iye.

Jagora: Dangi Aminuddin Ala

na Tudun Murtala na kwanar 'Yan gana.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Shugaban ‘yan shabbabu

mai qulafuci da vawa dangina.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Shi ne ke maku a dabo,

sai wata ran idan muna da yawan kwana, iye iye.

Amshi: Baubawan burmi,

kasassavarmu ce

kan zaven jagora, iye iye.

Jagora: Dangi Aminuddin Ala

na Tudun Murtala na kwanar ‘Yan gana.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Shugaban ‘yan shabbabu

mai qulafuci da vawa dangina.

Amshi: Iye Iye.

Jagora: Shi ne ke maku adabo,

sai wata ran idan muna da yawan kwana, iye iye.

Amshi: Baubawan burmi,

kasassavarmu ce

kan zaben jagora, iye iye.

Amshi: Baubawan burmi,

kasassavarmu ce

kan zaven jagora, iye iye.

**Waqar Bubukuwa**

**Ta**

**Aminu Ladan Abubakar (ALA)**

Jagora: Bubukuwa X4

Jagora: Gudu da ba kuvuta ashe

ya zama saukon bubukuwa X2

Jagora: Bubukuwa X2

Amshi: Gudun da ba kuvuta ashe

ya zama saukon bubukuwa X2

Jagora: Bubukuwa X2

Amshi: Gudun da ba kuvuta ashe

ya zama saukon bubukuwa

Jagora: Allahu Kai mana magani, abin da naj ji da nag gani,

Mugun ji mugun gani, rayuwarmu da hautsini,

Abin fa ba shi da kyan gani, abin a qyama da tsantsani,

Yana saka ni tuntuntuni, a yanzu ya sarayar da ni,

Na rasa inda zani bi, Allahuwa, bubukuwa,

Kuna ta saukon bubukuwa, kuna gudu ba gurin zuwa.

Amshi: Gudun da ba kuvuta ashe

ya zama saukon bubukuwa.

Jagora: Varayinmu a ban qasa, atifishiyal muka qirqiro,

'Yan dabarmu a ko'ina, atifishiyal muka qirqiro,

Masu 419 Arewa na qirqira, aka qirqiro,

Wahalar da muke ciki, ita tas saka suka bijjiro,

Na rashin shuwagabanni adalai, da rashin tsaro,

Rayukanmu kamar kiyashi, fagen kulawa ba tsaro,

Rabbi Kai ne Rahimi, tsare qasar Nijeriya.

Amshi: Gudun da ba kuvuta ashe

ya zama saukon bubukuwa.

Jagora: Gudu da ba kuvuta ashe, ashe,

Gudu da ba tsira ashe, ashe,

Gudu da kwai halaka ashe, ashe,

Gudu da ba nasara ashe, ashe,

Gara nai kwanciya da shi, da shi,

Gara nai birgima da shi, da shi,

Gara nai barci da shi, da shi,

Gara ma mutuwa da shi, da shi,

In dai dace da qaruwa,

Bubukuwa. X2

Amshi: Ba ku da kwanciyar hankali,

Ba mu da kwanciyar hankal,

Ba su da kwanciyar hankali,

Babu zama lau kan hankali,

Mun yi rashi na adali,

Muna ta saukon bubukuwa,

Bubukuwa X2

Amshi: Gudun daba kuvuta ashe,

Ya zama saukon bubukuwa.

Jagora: Abin da ya sa ni tunzuri, na dora tsuwa cikin dare,

Na kasa bacci cikin dare, ina wasi-wasi na fanxare,

Batun hukunci nai nazari, da shi ya qa'adi falken dare,

Masu mulki daga kansila, xan majalisa sun kantare,

Kwamishinoni, ciyamomi, ga gwamnoni sun fanxare,

In suka saci haqqin jama'a, babu hukunci gare-gare,

Lallai varayi suna suka tara, an yi gudu ba gurin zuwa.

Amshi: Gudun da ba kuvuta ashe,

Ya zama saukon bubukuwa.

Jagora: Sittin a cikin xari , lalura ta sa su bin dare,

Ashirin ta cikin xari, talauci ya sa su bin dare,

Talatin ta cikon xari, son zuci ya sa su bin dare,

Lidas sun kankane ma ma'adanai, sun xare xare,

Dukiya ta qasa da haqoqinta, sun kanainaye, sun maqare,

Ga isa da cikar isa da alfarma, sun tattare,

Shi ya haddasa sace sace, a ko'ina tamkar ruwa.

Amshi: Gudun da ba kubuta ashe

Ya zama saukon bubukuwa

Jagora: Shuwagabanni na zamani,

Masu hali na zamani,

Malamai 'yan zamani,

'Yan siyasar zamani,

Talakawan zamani,

Katankatanar zamani,

Ta samu saukon bubukuwa,

Bubukuwa. X2

Amshi: Gudun da ba kuvuta ashe,

Ya zama saukon bubukuwa.

Amshi: Ba ku da kwanciyar hankali,

Ba mu da kwanciyar hankali,

Ba su da kwanciyar hankali,

Babu zama lau kan hankali,

Mun yi rashi na adali,

Muna ta saukon bubukuwa,

Bubukuwa. X2

Amshi: Gudun da ba kuvuta ashe,

Ya zama saukon bubukuwa.

Jagora: Gudu da ba kuvuta ashe,

Amshi: Ya zama saukon bubukuwa.

Jagora: Gudu da ba kuvuta ashe,

Amshi: Ya zama saukon bubukuwa.

**Waqar Xaurin Gwarmai**

**Ta**

**Aminu Ladan Abubakar (ALA)**

Jagora: Ya Ilahuna Mai girma,

yau abin ba dama,

mun gaza da xaurin kamunga,

har da xaurin gwarmai X2

Amshi: Ya Ilahuna Mai girma,

yau abin ba dama,

mun gaza da xaurin kamunga,

har da xaurin gwarmai X2

Jagora: Ya Ubangiji yarda da ni Ala in zamanta jarmai,

a fagen waqa in zama sha- kwaramniya,sha-gwarmai,

Sarki Allah Ya yarda da ni sunce xaurin gwarmai,

Ubangijina Allah halin kamar ya sa na yi amai.

Amshi: Ya Ilahuna mai girma,

yau abin ba dama,

mun gaza da xaurin kamunga,

har da xaurin gwarmai.

Jagora: Ubangijina har kullum Kai nake kai wa kukuna,

Mai yaye hammi, gambi na taho da buqatuna,

abin da ake a qasar nan ya xugunzuma tunanina,

zan faxi da baxala, an ce da ni na iya bakina.

Amshi: Ya Ilahuna mai girma,

yau abin ba dama,

mun gaza da xaurin kamunga,

har da xaurin gwarmai.

Jagora: Ubangijina masifu sun yi mana katutu,

masifu na qirqira na neman samu mu zazzautu,

katankatana ce da handama ta sa muka wahaltu,

Ubangijin al'umma Kai sauyin burtu.

Amshi: Ya Ilahuna mai girma,

yau abin ba dama,

mun gaza da xaurin kamunga,

har da xaurin gwarmai.

Amshi: Guguwa ta sauyin sauyi muke nema Allah,

guguwa ta sauyin sauyi kaxawa bayinka X2

Jagora: Duk wuya da halin wayyo, ya samu cikin wayyo,

mahaukata a yau a garin nan an ba su cikin goyo,

mu waiwayo qananan yara da ke yin oyoyo,

jirajirai ana yankawa Allah kai sakayya,

muqabira ana tonawa a yaye alawayyo

a yanki mamaci da gadara,wayyo! Allah wayyo!

Amshi: Guguwa ta sauyin sauyi muke nema Allah,

guguwa ta sauyin sauyi kaxa wa bayinka.

Amshi: Nai mubaya'a gun Ala mai rushe shirin wawa,

mai kira akan a bi hanya da ba ta gantsarwa,

mai ragargaza da zalaqa da baitocin baiwa,

mai bindiga mai tanka da sautin harbawa,

Ilahu ka tsare mu da sharri na duk mai cutarwa,

mutum da aljani sulikina tsare mu cutarwa.

Amshi: Guguwa ta sauyin sauyi muke nema Allah,

guguwa ta sauyin sauyi kaxa wa bayinka.

Amshi: Ya Ilahuna mai girma yau abin ba dama,

mun gaza da xaurin kamunga,

har da xaurin gwarmai.

Jagora: Qasarmu akwai rana Allah qasar wasu ba rana,

da zamu yi sola system ilmin kimmiyar rana

ana maxari, sanyi,zafi,ni'ima duka a garina,

Sarkin alfarma ni'ima ta qare a garina.

J/A: Ya Ilahuna mai girma yau abin ba dama,

mun gaza da xaurin kamunga

har da xaurin gwarmai.

Jagora: Muna da su man angurya har da man gyaxa, man rixi,

muna tasarifin man kwakwa qasarmu akwai faxi,

muna da baranda,gwalagwalai kar in ja ka da kauxi,

muna tsallen bakaxe abin kama da 'yayan kwaxi.

Amshi: Ya Ilahuna mai girma yau abin ba dama,

mun gaza da xaurin kamunga,

har xaurin gwarmai.

Jagora: A qasarmu ana noma Allah abin da ake nema,

muna da qiragen fatun dabbobi da ake nema,

qasarmu akwai tama da qarafa har rogo baiwa,

akwai mu da ramun man fetur amma ba dama.

Amshi: Ya Ilahuna mai girma yau abin ba dama,

mun gaza da xaurin kamunga,

har da xaurin gwarmai.

Jagora: Ya Ilahuna mai girma yau abin ba dama,

mun gaza da xaurin kamunga,

har da xaurin gwarmai.

J/A: Ya Ilahuna mai girma yau abin ba dama,

mun gaza da xaurin kamun ga,

har da xaurni gwarmai.

Amshi: Mun gaza da xaurin kamunga,

har da xaurin gwarmai.Gwarmai!!

**Waqar Mafarkin Mulki I**

**Ta**

**Jibrin Jalatu**

Amshin Xango: A duniya

Amshin Baiti: Mulki Jibrin Jalatu, a gaskiya ba mu son ka qara,

Wasa kuke,

Idan ka qara mulki a gaskiya ba za mu sha ba.

Jagora: Assalam salamu jama'a da ke qasata,

Ni ne Jibril Muhammadu, inkiyata Jibir Jalatu,

Ina cikin takaici, cikin takaici,

Na kwanta barci, ina cikin takaici,

Sai nai mafarkin an ba ni mulki,

Mulki yana da daxi X 3

Jagora: Mulki yana da daxi, a yaushe zan so a ce in bar shi,

A yanzu ni nake mulki a duniya, ba a lahira ba.

Jagora: Sun ce qasa musiba, ni ko musiba ba ta gabana,

Sun ce qasa bala'i, ni ko bala'i ba ya gidana,

Sun ce a kama gaskiya, ni kuma gaskiya ba ta gabana,

Sun ce a daina cin hanci, cin hanci ya zama jinin jikina,

Sun ce a daina murxiya, ni kuma murxiya na hau abuna,

Sun ce da ni tsaro, ni ko tsaro ba ya gabana,

Ban bi gaskiya ba, mutan qasata ku shiga azaba.

Jagora: Manya iyayen qasa, su ma na vata lamarinsu,

Su za su zo gabana, a da fa ni za ni je gabansu

Ina faxi, ina tashi, har ina Allah taimake su,

Sai na sakwarkwata su, na karya qwarin da ke gurinsu,

Idan na zo da tsari, suka qi bi, zan gina asusu

Baho-bahon kuxi ne, zan tattare, in kai gabansu,

Wallahi za su bi ni, daga qarshe su shiga uquba.

Jagora: A yanzu zamanin nan, in ba a son gaskiya haqiqa,

Kome kake buqata, ka zo da toshiyar baki in ba ka,

Kafin a bincike ni, babu kowa a xaure fuska,

Idan ka nuna taurin kai, zan xau kuxi in ba ka,

Idan ka fanxare mun, zan sanya a addabe ka,

Ni in na kafa hukuma, wadda zan sa ta bincike ka,

Saboda gaskiyarka, za ta sa ka sha azaba.

Jagora: Tsaro a zamanina, a kashe kowa a kan abin shi,

Ni na ci, na yi xaxin, na kwanta ina ta nishi,

Saboda taqamata, ba mai ce da ni ka tashi,

Kun ji wahalallu, wai in wa qasarmu kishi,

Na kwashe arziqi kaf, na bar ‘yan qasa da bashi,

Wata karuwa ta ce ban kurxi, in gyara gashi,

Ko xan ten miliyan of dolas, ku kuna uquba.

Jagora: Cas’in cikin xari, na shuwagabannin addinai na riqe su,

Ya kamata shuwagabannin addinai, a je gida a gan su,

Yanzu wasu shuwagabannin addinai, kwaxayi gare su,

Idan ka kama mulki na zamani, yanzu za ka gan su,

Talaka na ta ihu, wai mi za na taimake su,

Ina da iyayen qasa, da mahukunta da ke wurinsu,

Babu yadda za ku yi, qarshe ku sha azaba.

Jagora: Ina mahukunta su ma, sun biye halina,

A gama murxiyar zaven da akai, ina gida abu na,

A gama kai qara a kotuna, ni za a ban abu na,

Ka daina gaskiya a zahiri, sai ka zo mu zauna,

In ka qi ko haqiqa, kullum kai kake a rana,

Domin a zahiri babu gaskiya, kaf a lamarina,

Gara ka zo mu zauna, in kuma ka qi, ka sha azaba.

Jagora: Na zamo kamar xakin kura, sai dai na jikina,

Ministan tsaro, ni zan naxa da kaina,

Ministan ilmi da lafiya, zan san a wurina,

Ministan kuxi, ni ne zan naxa abuna,

Ministan sufurin jiragen sama, yana wurina,

Ministan ruwa shi ma, ni zan naxa da kaina,

Idan na sanya doka, kowannensu kar ya sava.

Jagora: Ministan ma'adannen qasa qwarai, yana wurina,

Ciyaman fetur shi ma, zan sa na wurina,

Idan na tara duk gaba xayansu, zan ba su huxubana,

Arziqin qasar nan gaba xaya, mu voye kar mu nuna,

Zan ba ku fasentej mai yawa, in kun bi ra'ayina,

Wanda yaq qi bi, zan sanya hukuma, da ra'ayina,

Zan takura shi, gaskiya ta zame musiba.

Jagora: A da, muna da noma na auduga, an san da mu a duniya,

Qasarmu na da noman gyaxa, an san da mu a duniya,

Ga uwa uba noma, kiwo, an san da mu a duniya,

Kasuwanci ma qasa-qasa, sun san da mu a duniya,

Da dai na fara mulki, komai sai ya sauya,

Na durqusar da gaskiya, ta rusunawa qarya,

Wanda ke da gaskiya, yanzu shi za ya sha azaba.

Jagora: Shekaru suna turawa, za a amshe mulki,

A lokacin da rama da takaici, suka fara aiki,

Abin da duk na shuka, za ni girbe, ina da aiki,

To, sai na hau tunani, shin wa za na ba wa mulki,

Mai handama da babakere, shi za ni bai wa mulki,

Tunda wani ya sauka, ya ba ni, tilas in qyale mulki,

Lallai ina da aiki, a lokacin na shiga uquba.

Jagora: Abinci ban iya ci da yawa, kullum sai tunani,

Na gaza bacci da daddare, kullum ina tunani,

Hawan jini da olsa, a lokacin suka mamaye ni,

Zuciya da vargon jiki, a lokacin sun yi rauni,

A ka ce da ni, saura kwana huxu, a mamaye ni,

Ji nake kamar an, albishirin mutuwa gare ni,

Mulki babu daxi, ga shin an ya zame uquba.

Jagora: Wanda ya kama mulkin, na ba shi sharuxxa bai riqa ba,

Ya ga banda qarfi, ya ce bai yarda da ni ba,

Na kafa hukuma a baya, can in ba ku manta ba,

Yanzu ga hukuma, ita za ta ban musiba,

Wanda ni na kama da gaskiya, yanzu fa shi ya karva,

Yanzu ga shi nan shi ne fa, yake ban azaba,

Ka ga ma nadama, na kasance cikin musiba.

Jagora: A lokacin da na yi nadama, kowa ya guje ni,

Wanda da na bai wa muqamai, don mulki suka so ni,

Talaka ko can cikin mulkina, ya guje ni,

Don saboda ba tsoron Allah, da tausayi gare ni,

Yanzu ga shi mulki ya qare, sai dai tsanani,

Talaka in ya gan ni, jifa ce yake gare ni,

Mulki fa babu daxi, ga shi nan ya zame musiba.

Jagora: Kar ku manta cewa cikin mafarki, na xana mulki,

A lokacin fa na kwanta cikina fa, babu girki,

Ga shi ba maqota, ba mata, da za su ba ni girki,

Sai na hau tunani shin, a ina, za ni samu girki,

Sai na kama barci, tunda babu inda zan ci girki,

Sai na kama mulki a mafarki, kuma ban da kirki,

Kafin na kwanta barci, sai da na sha baxar uquba.

Jagora: Kafin na bar mafarki, sauro ne ya mamaye ni,

Kiran sallah ne, na jiyo muryar ladani,

Sai na xauki buta, a lokacin na samu sukuni,

Nai alwalla da jam'in sallah, wanda babu muni,

Nai istigifari ga Rabbana, don Ya yafe ni,

Ya cire man zunuban da ban sani, da wanda nas sani,

Allah Ka taimake mu, ka raba mu da baqar uquba.

**Waqar Mafarkin Mulki II**

**Ta**

**Jibrin Jalatu**

Amshin xango: A duniya

Amshin baiti: Ba ma fata, kuma ba daxi,

In Jibrin Jalatu zai koma kan mulki.

Jagora: Na ce Assalan salamu xin de,

Jibrilu Muhammadu ni ne de,

Laqabina Jalatu shi ne xin de,

Ku yi haquri ku magautana de,

Zan maku albishir masoyana de,

Za ku ji qarashen mafarkina de,

Wai ba sa fata, kuma ba daxi,

Ni Jibrin Jalatu zan koma kan mulki.

Jagora: Kwanton vauna, talakawana,

Shi za su yi min idan na koma kan mulki.

Jagora: Suka ce gaskiya, na ce ba zan ba,

Suka ce taimako, na ce ku tafi gaba,

Suka ce yunwa, na ce ba ku mutu ba,

Suka ce min tsaro, na ce ba ku gaji ba,

Kama-karya na sanya a gaba,

Kama-karya na sanya a gaba,

Ba ku da wanda za ya ture ni a kan mulki.

Jagora: Mahukuntan qasarmu duka ku saki jiki,

Iyayen qasa kawai su saki jiki,

Mahukunta ma duk ku saki jiki,

Shugaban addinai ku saki jiki,

Ai zalunci ina kan mulki,

Ba wani wanda za ya yi maku raki,

Komi za ai, ni ne ke kan mulki.

Jagora: In jama'ar qasarmu na wasi-wasi,

Sai yaqi a ce ina shan A/C,

Talakawa duka ba mai sisi,

Duk makarantunmu na wasi-wasi,

Talakawanmu babu mai shan A/C,

Talakawanmu sun shige wasi-wasi,

Burina kawai a qyale ni a kan mulki.

Jagora: Nai masu tarnaqin baqar wahalata,

Duka qasa na varvazo matsalata,

Qadarar ‘yan qasarmu na sace ta,

Makarantun qasarmu na lalata,

Burina kawai qasa a kashe ta,

Burina kawai qasa a kashe ta,

Sai mai cuta da zamba, zan ba mulki.

Jagora: Suka ce tausayi, na ce ba mu gamu ba,

Suka ce jin qai, na ce ba mu haxu ba,

Kuma kishin qasa, ba za ai ba,

Mulkin gaskiya, na ce ba zan ba,

Kuma mai gaskiya, ba zai hau ba,

Kuma mai gaskiya ba zai hau ba,

Sai marar gaskiya nake miqawa mulki.

Jagora: Sanatocin qasarmu na kama su

In da ba kwaxayi ni ke binsu

Suke aje matsayinsu na hau kansu

'Yayan banki na sa, na kashe su

Na yi gidaduwa kamar burinsu

Na yi gidaduwa kamar burinsu

Ba mai ce da ni ka sauko daga kan mulki.

Jagora: Nai cuta qasarmu kwando- kwando

Mamuguntar qasarmu dodo-dodo

Kullum na fito a ce ga dodo

Ni kuma na fi so a ce min dodo

Na yi qiba, na yi tumbin kwaxo

Na yi qibata kamar xan – kwaxo

Wa ye wanda za ya raina ni a kan mulki

Jagora: Na saka zuciyarsu na yin raxaxi

Sai murna nake, ina jin daxi

In zave ya zo, na sa a yi maguxi

Sai mulki nake, suna ba daxi

Sai mulki nake, suna ba daxi,

Burina kawai a qyale ni a kan mulki.

Jagora: Wahala ma ashe tana kashe kwaxayi

Jama'a sun jigata, sun bar kwaxayi

In zave ya zo, su ce ba sa yi

In na ce su zo, su ce ba ma yi

Shin wai ni yanzu, yaya zan yi

Shi wai ni yanzu yaya zan yi

Mamuguntan qasa su mai da ni a kan mulki

Jagora: Mai murxewa, ya ce min ta kife

Sanatocina suna son ta kife

Qusoshina suna so ta kife

Sarakunan qasa suna so ta kife

Talakawa sun fi so ma ta kife

Talakawa sun fi so ma ta kife,

Tunda ina ba su wahala a kan mulki.

**Waqar Ku Yi Haquri**

**Ta**

**Jibrin Jalatu**

Jagora: A dinga tunani,

Akwai jin tausai,

Akwai jin tausai,

Akwai jin tsoro.

Jagora: Jinjinar talakawa ce,

Daga Jibrin Jalatu,

Haquri nan da muke de,

Kada mu gaza, mu qara,

Zai mana amfani can.

Amshi: Jinjinar talakawa ce,

Daga Jibrin Jalatu,

Haquri nan da muke yi,

Kada mu gaza, mu qara,

Zai mana amfani can.

Jagora: Ya Arrahman, Ubangijin rahamar bawa,

Tu'utal Mulku, Ubangijin dukkan kowa,

Ya qagi mutane da hankali, wani kuma wawa,

Abin da nake so, mu yo tunani kan mutuwa,

Ita ba ta tsoro, ba ta kula mulkin kowa,

Za mu mace de.

Amshi: Za mu mace

Jagora: Za mu mace,

Kuma a lahira babu dabara.

Amshi: Jinjinar talakawa ce

Daga Jibrin Jalatu,

Haqurin nan da muke yi,

Kada mu gaza, mu qara,

Zai mana amfani can.

Jagora: Ana qwararka, a ce ba dama ka ji haushi,

A danne haqinka, a ce ba dama ka ji haushi,

Da ka yo magana, a ce maza wancan kama shi,

A sa shi gidan yari, babu tausai a tsare shi,

Da ya yo motsi, kusa makami ku kashe shi,

Abin da ake yi.

Amshi: Abin da ake

Jagora: Abin da ake yi, a gaskiya babu dabara.

Amshi: Jinjinar talakawa ce,

Daga Jibrin Jalatu,

Haqurin nan da muke yi,

Kada mu gaza, mu qara,

Zai mana amfani can.

Jagora: Ma'adanenmu, ba a nuna wurin ajiyewa ba,

A sai da komai, ba a ba mu kuxin saidawa ba,

A wa muqamai, ba mu yarda da lamuncewa ba,

Qwallon banza, ta fi mu mahimmancin duba,

A raya qwallo, talaka bai samu abinci ba,

Abin da ciwo.

Amshi: Abin da ciwo

Jagora: Abin da ciwo,

Su suna ganin sun yi dabara.

Amshi: Jinjinar talakawa ce,

Daga Jibrin Jalatu,

Haqurin nan da muke yi,

Kada mu gaza, mu qara,

Zai mana amfani can.

Jagora: Abin da na duba , talaka mutum ne shi mahaqurci,

Ana mulkin shi, da murxiya bisa zalunci,

Ya nemi haqinshi, a ce da shi, ya cika naci,

A bar shi da yunwa, cikin dare babu abinci,

Ya wayi gari in ya bincika, babu abinci,

Abin ban tausai.

Amshi: Abin ban tausai

Jagora: Abin ban tausai

Za ka ji kukan ‘yan yara.

Amshi: Jinjinar talakawa ce,

Daga Jibrin Jalatu,

Haqurin nan da muke yi,

Kada mu gaza, mu qara,

Zai mana amfani can.

Jagora: A dinga tunani,

Akwai jin tausai,

Akwai jin tausai,

Akwai jin tsoro,

Amshi: Jinjinar talakawa ce,

Daga Jibrin Jalatu,

Haqurin nan da muke yi,

Kada mu gaza, mu qara,

Zai mana amfani can.

Jagora: Yanda suke so, su talaka ba zai numfasa ba,

Yanda suke so, talaka ba zai ci abinci ba,

Yanda suke so, talaka ba zai yi karatu ba,

Yanda suke so, talaka ba zai zama kowa ba,

Yanda suke so, talaka ya zauna da uquba,

Babu haxin kai.

Amshi: Babu haxin kai

Jagora: Babu haxin kai

A gaskiya gara mu gyara.

Amshi: Jinjinar Talakawa ce

Daga Jibrin Jalatu,

Haqurin nan da muke yi,

Kada mu gaza, mu qara,

Zai mana amfani can.

Jagora: A tuntuni tarkon matambaya de ikhwana,

Mai zalunci, ba shi da fili aljanna,

Mai sata a qasa, ba shi da fili aljanna,

Mai murxe zave, ba shi da fili aljanna,

Wasu ba su ibada, tun kan zave suka daina,

Ai nazari dai.

Amshi: Ai nazari dai

Jagora: Ai nazari don a lahira babu dabara.

Amshi: Jinjinar talakawa ce,

Daga Jibrin Jalatu,

Haqurin nan da muke yi,

Kada mu gaza, mu qara,

Zai mana amfani can.

**Waqar Ba Mu Yarda Ta Zarce Ba**

**Ta**

**Haruna Aliyu Ningi**

1. Na ce ya bisimilla, ya Allah da Ka yo mu, mu Ma bauta,

   A dukkan lamari nawa, SunanKa da fari na wajabta,

   A cikin suratul A'alaq, a kan ManzonKa Ka umurta,

   Wa Nabiyyu Rasullullah, mu kam ba mu qaryata aya ba.

2. To salama, salama kaf, jama'a ta qasarmu ku saurara,

   Na zo da bayani ne, da na tattara a cikin gora,

   In ya yi ku amsa min, in bai yi ba kar ku zubar shara,

   Ku kira ni mu tattauna, wataqil ba ku gane bayanin ba.

3. Da akwai wasu gungun 'yan qasarmu abar qauna,

   Ba su yarda da Allah ba, sun mai da qasarmu kamar waina,

   Yau na xaga yatsana, ku zo a idonku in nunnuna,

   Sun vadda Abacha a da, a yanzun ma ba su qyale ba.

4. Farkon da akwai Mantau, ban mance tsiyar da ya shuka ba,

   Na biyunsu akwai Ojo, dama ba mu san shi da kishi ba,

   Sai Tom kuma and Jerry, ba wai na Fred da Quimby ba,

   Da babu tawagar nan, to da ba mu samu ta zarce ba.

5. Zan fara batun Mantau ya mance jiharsa cikin yaqe,

   Rikici suka huhhura, dubban jama'a aka yayyanke,

   Bai kai musu diyya ba, bai damu ba su aka faffarke,

   Inda a ta zarce ne, da kun ga shirin rikici babba.

6. Maganar na biyun Ojo, dama bai zo shi da hujja ba,

   In ban da rasar kunya, ta Ojo da rena qarama ba,

   Ya za a yi alhanzur, ba za mu kira shi haramun ba,

   To ku je ku ci, ba ma ci, ba za a ciyarmu masifa ba.

7. Shi Tom da ake cewa, shi ne magininta da shirya ta,

   Shi Jerry gwanin baki, shi ne aka ba shi ya yayata,

   Allah da Ya karya ta da, ta yanzun zai da xa karya ta,

Sarkin da muke roqo, ba za ya bari mu ji kunya ba.

8. Sai xan-baqi xan Kogi, shi ne suka ba jam'iyyata,

   Mune muka goya ta, shi ko aka ba shi ya karya ta,

   In ban da vatan kai ba, wa zai tafi Kongo bixar mata,

   A zamansa a fatin ma, ya ce baxi ba ta da cin zave.

9. Da akwai wani gwamna ma, muryarsa ya wanda ya sha maye,

   Dan-daudu da jar hula, yara ku kaxa masa nanaye,

   Wai shi na tazarce ne, mun gane abin da yake voye,

   Shi Ribaxu yake tsoro, ba wai haxuwa a kiyoma ba.

10. Ga sautuna jama'a da gwamnoninmu ku kai saqo,

    To ku zo sanatocinmu da refs-refs xinmu ku kai saqo,

    Ku faxa wa ministoci, su cije havarsu su kai saqo,

    Su faxa wa Obasanjo, mu kam ba mu yarda ta zarce ba.

11. To batun daxa zarcewa, a son rai ma makaruhi ce,

    Sannan a cikin tsarin mulki na qasarmu haramun ce,

    To bare kuma tursasa shi, a kan jama'armu masifa ce,

    To ku gane bayanin nan, in kun qi ba za ku ci riba ba.

12. Wai wanda ya ce a'a, kakan ce Ribaxu ya kama shi,

    In ba ya cikin gammen, ka sa maqasanka su harbe shi,

    Qarshe ko idan ya zo, mutum ba ya iya canza shi,

    Ko za ka ci namana, zan ce ba mu yarda ta zarce ba.

13. Na ce ya jama'a na qasa, Haruna na Ningi ina roqo,

    To idan jama'ar xazu, wasu suka kasa isar saqo,

To mu harhaxa kayinmu, mu sallami mai tafiya tunko,

Zamansu a mulkin nan, ba za ya zame mana hairan ba.

14. To ku kau da batun tsoro, na harbin soja da ‘yan sanda,

Wallahi qananan kaf, cikin wahala suke mun shaida,

‘Yancinmu da su ne duk, in za mu ruguntsuma sun yarda,

Ko za su yi harbin ma, ba za su yi yai mana illa ba.

15. To ku kau da batun zave, in dai ba a kyautata tsarin ba,

Sai mun yi su caccanza, sannan ba su ba mu dalili ba,

In dai muka sa tsoro, ba za mu rufe su da duka ba,

To masu ta zarcen nan, ba za mu hana su ta zarce ba.

16. Duk wanda ya ce ta wuce, ku ce bai yarda da Allah ba,

To idan a Musulmi ne, bai gane dalilin sallah ba,

To idan a Kirista ne, bai san ma’anar gina coci ba,

Ai ni a mutuncina, gare su da bai wuce zagi ba.

17. Da akwai membas, sanatas da gwamnonin da su kai wayo,

A jiharsu ana wayyo, Abuja tana masu oyoyo,

Ba su kushe ta zarce ba, ba su ce mana eh ba ta ‘yan koyo,

Duk mai haka ko waye, bai girma a kwansituwansi ba.

18. Duk wanda bar Allah, mu bar shi da wanda yake tsoro,

Amma mu sani duk ran da, za ya kira mu wurin taro,

A cikin izinin Allah, mu taru da kanmu mu mar horo,

Mu gwada masa fau-fau-fau, cewa ba mu yarda ta zarce ba.

19. To idan ta tsaro ne dai, ya san ba ya tsare rayinmu,

Hanya ba mu tsere ba, a bi mu gidanmu a yanka mu,

Ga masu tsaro jingim, duk ya qi ya bar su su kare mu,

Ga soja da ‘yan-sanda, har yau ba a bar tsare hanya ba.

20. To idan maganar cewa arziki na qasarmu ya xore ne,

To ka gama yawon duniyarka, ka kasa zama zaune,

Na wajen ba su kawo ba, sannan na cikin kuma gurgu ne,

Ka tara kuxi jingim, amma ba mu daina talauci ba.

21. To a xau duka aikinka, a xau varnarka a auna su,

To abin da ka vavvata, ya zarce wa ‘yanda ka gyara su,

Ko ban tava boko ba, mutum bai ce mini sususu,

To a tara bayanina, a kan haka ban rasa hujja ba.

22. Da akwai wasu gwamnoni sun sanya ta zarce cikin huhu,

Sun je su jihohinsu, sun ruxi wa ‘yansu da huhuhu,

To suna masu ihu wai ta zarce kai ka ji shashashu,

Ai rashin ilmi ne duk, domin ba su hangi bala’in ba.

23. In ban da ana sauka a bai wa waxansu su xana ba,

Ba za ku yi mulkin ba, bare ku mayar mu kamar kumba,

To babu ta zarcewa, idan ba dai a kiyoma ba,

Ba ku tsaida amana, ba to mu ko ba za mu ji kunya ba.

24. Wa’adinmu na da na nan, idan ka yi sau biyu shi kenan,

Ba a dagula tsarin ba, ka ce mana ba ka cikin wancan,

In ba ka cikin wancan, to mu kuwa ba mu cikin wannan,

To idan ba ka fasa ba, mu ma ba mu yarda mu qyale ba.

25. To kuxin da ka kwakkwashe, irin na qasarmu ka vovvoye,
Ka bar mu da nya-nya nya, ka sanya qasarmu a nanaye,
Manufarka ta kwave ne, kowa ya rasa a yi ‘yar juye,
To za ka ji kunya ne, idan ba ka canza dabara ba.
26. Allah da Ya tara mu, ya bar mu qasarmu guda tare,
Ya bar mu da jinsi dai, amma ya raba mu a kan yare,
Duk wanda ya daddage, sai ya raba kanmu zaman tare,
Ba zai wuce makonni kaxan, bai tadda jafa’i ba.
27. In za su yi makirci, wutar fitina suka kunnawa,
Da faxa na qabilanci, da na addini suka hurawa,
To muna kashe kayi su, tsarinsu kawai suka gyarawa,
Mu fahimta mu bar gaba, in mun qi ba za mu ci riba ba.
28. Na san wasu ba sa son, mu ce ba mu yarda ta zarce ba,
Ce hakan kuwa tilas ne, a ce da mijin iya ai baba,
In dai sake tsari ne, ba za mu biye ku, ku sava ba,
In da a ta zarcewa, da tun asali ba ku rantse ba.
29. In zan yi gadarata, ai dole in yi da qasar nan ne,
In zan gwada kishina, to za ni gwada wa qasar nan ne,
Har ban tava mulki ba, in kare qasarmu farilla ne,
Ba zan ci amana ba, ba zan biye masu ta zarce ba.
30. In za na yi waqata, ba zan yi wa masu ta zarce ba,
Domin kuwa al’ummar qasarmu ba za su ji waqar ba,
To abin da suke qyama, ba zan yi ba ya zama min riba,

Kai mu faxi da ku tare, mu tashi ba zan sake hanya ba.

31. To ku qyale ta zarce, tun manya ba su fara kashedi ba,

    To idan suka fara mu yaransu ba za mu ji shakka ba,

    Mu rugurguza ko waye, bai amsa abin da ya dace ba,

    Harka ta butulci ce, mu ko ba mu gaji butulci ba.

32. Tura ta kai bango, kun ganta amma ku haqiqance,

    Wai ko da tsiya ku, dai ku sake zama a guri  qwace,

    Sai kun gama holoqo, da cin zarafinku ta susuce,

    Ko kun hana jin waqen, ba za ku hana mu adawa ba.

33. Kun voye kuxi, kun ce ba za ku fitar su mu samu ba,

    Don ku yi mana talala, a kan ba mu yarda ta zarce ba,

    Mu mun gama qonewa, tokarku ba za ta yi illa ba,

    Mun yarda ku more ku, ku ne ba ku yarda mu more ba.

34. To mun dasa aya yau, kuma mu hana muku morewa,

    In har ku ka ce lallai sai, kun bi ta kanmu a zarcewa,

    Komai ya biyo baya, ku ne asalinsa a somawa,

    In kun gaza jurewa, oho ba mu damu ku jure ba.

35. Son kanku kuke sosai, ba kwa kula wanda kuke mulka,

    Sai kun ji dirin ganga, an ace kun yi kusan sauka,

    Duk sai ku dubulbuce, ku fara abinku kamar hauka,

    Ya za a yi ne nema, a ce ba za ku ji kunya ba.

36. Tsun-tsun-tsuru-tsutsunku qasarmu ashe muka ba zave,

    Mun ba shi ta zarce da, amma bana dole mu mar zobe,

Ko ya iya aikin ma, ya je shi ya huta a xan kurve,

Ya a je mana mulkin nan, domin ba mu yarda ta zarce ba.

37. Ko kun iya aikinmu, irin haka dole ta vata ku,

Ku bari wa waxansu su yi, domin kuwa kun gama aikinku,

Magana ta ta zarce ce, ta sa jama'a suka kushe ku,

Ai ko a kiyoma ne, waxansu ba za su qi canji ba.

38. Ki ja ni mu je ganga Haru, in rabarbaza baitina,

In biyo ta qasan nan kaf, domin in gwada musu 'yancina,

Duk wanda ya tanka min, in vangare kansa da dutsena,

Ku biyo ni mu ce Olu, mu kam ba mu yarda ku zarce ba.

39. In ka cire gwabna don ya ce, ba su yarda ta zarce ba,

Ka qwace mukami nai, amma ka sani ba ka zarce ba,

Ko ka baza tsari NASS, ba za ya saka ku, ku zarce ba,

In su suka qyale ku mu kan, ba mu yarda mu qyale ba.

40. To ki ja mu je ganga, domin mu kawar da Obasanjo,

Ko za a yi girki na, ai dole mu rusa faxar Ojo,

Ba su bar jam'iyya ba, sun sa ta qilu da rawar banjo,

Maganar da nake yanzu, har yau ba su rarraba kayi ba.

41. Ya rurrufe boda kaf, don kar jama'a su sayo sifiri,

Don kar mu ci shinkafa, sai dai mu tsaya a tikar gari,

Ya xaxxaga mayin ma, ya sanya qasarmu cikin bori,

Maganarmu ta fetur ma, a yau ba mu gane ministan ba.

42. Tsoho haquri ne dai, sai ka yi ka daina baqar gaba,

To abin da ka quqqulla, ba zai tafi yanda ka shirya ba,

To mutun kudu ba sa so, arewa kakaf ba mu yarje ba,

Ai hannu xaya ba zai xau, abin da yake rufe xaki ba

43. Duk wanda ya sanya hannu, harka ta tazarce a nuna shi,

Imma a wakilin ne, imma sanata ne a tsige shi,

Ko da kuwa gwabna ne, ku bi shi gidansa ku turke shi,

Mun fara ganin doka, a kansu ba za ta yi aiki ba

44. Su za su yiwo doka, su za su bi kanta su taka ta,

In kotu ta ce ga shi, su share batunta su karya ta,

Ta yanke hukunci yau, an ce mata gobe ta karyanta,

Sun xau shari'a wasa, in dai ba ta yarda su zarce ba.

45. Ni na ji zarcen ma, an ce a Kano aka soma ta,

Da akwai wasu hamshaqai, wa'yanda suke wa kuxi bauta,

Hujjarsu ta jari ce, sun ba da kuxi aka soma ta,

To da ku da Kanon ga ku, don ko ba su yarda ta zarce ba.

46. To ina alarammomi, ina adu'arku ta juya ne,

To ina kuma fastoci, ina addu'arku ta sauya ne,

To wutar fitina ga ta, kuna kallonta kuna zaune,

Ko kun ci kuxi ne ne, ba za ku haxa su da Allah ba?

47. Sai Soja da 'Yan-sanda, su ne suka yarda ku kare su,

Sun vata qasan nan kaf, kuna kallo kuka qyale su,

In za mu fito mu faxa, su sa ku kashe mu, ku kare su,

Ku gama ku ritaya, ba za su biya ku na fansho ba.

48. Sun xauki mutum ganga, da sun ci rabonsa sa ya da shi,
Tsarinsu ya su ne rak, in ba ka cikinsu su ma qyashi,
Ku ga Tafa Balogun dai, ku xau kes xinsa ku duba shi,
In bai isa aya ba, ba za ku fahimci ta zarce ba.

49. Ku faxa wa Obasanjo, in ji ni Haruna ya bar ture,
Na saddaqa rayina, in jagoranci a mar bore,
Zan ce wa qasan nan kaf, cikin kowanne irin yare,
Ku fito mu jajirce, a kan ba mu yarda ta zarce ba.

50. Duk wanda ya zo zance ta zarce garinku ku jefe shi,
In ya qi ya tsere ma, dama aka ba ku ku tsire shi,
In ya mutu shike nan, ai ya tafi ya yi asara shi,
Domin ba mu fara ba, sannan ba mu yarda ta zarce ba

51. In ban da mutanen nan, rikici suka shirya su qulla ba,
In dai iya aiki ne sun san, ba su kai ya Amurkan ba,
Ba su nemi ta zarce ba, sai ku da ba kui mana aiki ba,
Ai dole mu ma bore, domin ba ka kai ya qasan nan ba.

52. Manya na siyasarmu, da manyan soja suna zaune,
Duk ba su da kishi ai, burinsu su tara kuxi tare,
To dole kananan mu, mu kare qasarmu zaman tare,
Mu da zubar da jini babba, ai gara a ce ba ta zarce ba.

53. Maganar ta qasa ce kaf, ba wai ta wa'yansu qabila ba,
Maganar haxa kayi ne, ba wai maganar wani sashe ba,
Gyaran da ku ke kwaxayi, ba zai yiwu har ya yi aiki ba,

Burin wasu ba zai sa a sanya qasarmu a yaqi ba.

54. To wa'yansu sun ce wai ba a ba ni abin ihisani ba,

Na yarda da mai waqa, ba zai qi abin ihisani ba,

Amma ihisanin in ba za ya raba shi da hanya ba,

Kun san fa ta zarcen nan, sam-sam ba ta sadu da hanya ba,

55. Kowa ya ji shi kenan, kowa ya qi jin mu ku shaida mar,

To jiki magayi ne ai, ku ce na jikinsa su nuna mar,

Magana ta ta zarce dai, ya sani birki aka taka mar,

Nan zan rufe waqata, jama'a har ban gama sharhin ba".

**Waqar Kada Mu Xauki Siyasa Da Zafi**

**Ta**

**Haruna Aliyu Ningi**

Amshin Baiti: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mune a rana.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana X2

Jagora: Ya Rabbi Mai sama Allah Gwanina,

Kai Ka halicci dare, Ka yi rana,

Kai Ka halicci uwa da ubana,

Allahu ba ni basira wuce arna,

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Don daraja ta Rasulu Fiyayye,

Manzon da Kai masa sura Tsayayye,

Allah Ka samu tafarki Hayayye,

Ba ni ta tsaro a dukkan lamarina.

Amshi: Kada muxauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Talaka gani da waqa ina so,

Ka jingine duk uzurinka ka taso,

Ka zauna ka ji gwaxoso

Za ka fahimci ina aka kwana.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Kai ne ake yi wa zagi ka dawo,

Kai ne ake maka duka ka dawo,

Kai za a nemi abinka ka kawo,

Da ka ba su, sui maka kamun sakaina.

Amshi: Ka da mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Kai za a sa wa aqida a kwanya,

Wacce akai mata fenti da qarya,

Ka kasa gane gabanta da baya,

Sun bar ka kullum da ihu a rana.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Sun sa muna kashe kanmu da sara,

Gobe ka ganmu a kotu da qara,

Su ko ba za su iya nan da yara,

Ba ka ganinsu a gun da ke da rana.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Duk wanda ya mutu, ya mutu banza,

Ba wanda zai ba iyalinsa gabza,

Wanda ya kashe wani ko a ziza,

Sai ya tagayyara ko da, da kwana.

Amshi: Ka da mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Duk tsananin ra'ayi da adawa,

Kadda ka yarda su kai ka kushewa,

Duk wanda yai haka ya cika wawa,

Mai ce a kar ni saboda gwanina.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Manyanmu kaf na siyasa ku duba,

Ba za ku ji su da zagin uba ba.

Ko su yi dokin-in-doka a su ba,

Sai mu irin lamarin nan da quna.

Amshi: Ka da mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Zan so muke tuna bayanmu cancan,

Mutum kar mu vata zumunci na tun can,

Wanda ya ce maka je sari wancan,

Kadda ka yi haka, shi ne batuna.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Shi in ya je shi, ya sara da kansa,

Ai zai fi kyau yai da kayinsa fansa,

Zai je ya sa ka a xaki da qusa,

Shi ko ya tai da iyali su kwana.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Za kai abin bisa izza da girma,

Sai daga baya ka fara nadama,

Sai wanda kai masa aikin ya ce ma,

Shi ba ruwansa da wannan ta'asa.

Amshi: Kaxa mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Don me muke ta wulaqanta juna,

Akan wanda ba su da tsoron amana,

Wanda suke mana kamun sakaina,

Sun bar mu zaune a daji ya vauna.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Zan yi kira na Fulani da niyya,

Don yanzu mu aka qyale a baya,

Sai za ta vaci ake mana gayya,

Mu ko mu zo mu, mu rarraxe juna.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagoara: Ce waqa nakan yi da niyya da qarfi,

Wa'yansu sukan ji kalamin da zafi,

Amma idan nazarinka da zurfi,

Za ka fahimci salama a batuna.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Sun qi su kyautata duk makarantu,

Don kar xiyanmu su je su yi karatu,

An bar su talle, acava, zuruntu,

‘Yayansu na inuwa namu a rana.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Ba za ka gan su a qauye ba nan ma,

Sai dai idan quri’a za su nema,

In kun saka musu, son samu dama ,

Da za su saka ku, a wayyo inama.

Amshi: Kada mu xauki siysa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Wanda ya zo shi siyasa da kurxi,

To, karku yarda da shi bai da daxi,

Zai zo da masu zalama da kauxi,

Su za su ke maku kunnin ashana.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Qauye idan ka ga yayi da danga,

Shi ko gidansa da kyau ga katanga ,

Sai ka ga wani gidan babu salga,

Shi ko a nasa masan, sai ka kwana.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Kai sai ka kwana da yunwa da qunci,

Shi ko karensa yake ba abinci,

Don shi a gunsa yana da mutunci,

Kai ko ka duba ta ya ko ka kwana.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Jinyarka babu ruwansu da duba,

Ba zai saya maka pengo ka sha ba,

Ga bai gina muku gun magani ba,

Ai ya kamata ku gane batuna.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Sun bar mu ba ilmi ga talauci,

Ga sun rufe mana hanyar abinci,

Sun bar mu zaune a dauxe da qunci,

Sai gwara kanmu suke yi da juna.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa nu ne a rana.

Jagora: Duk wahala da talauci ku gane,

Kada su sa ku, ku bi su ku manne,

In dai kana maganar arziqi ne,

Qyale su je ka, ka samu a gona.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Ba za su yarda ka samu ba ka ji,

Don kar su daina ganinka a juji,

Sun mai da duk lamuranmu ya kaji,

Sun xan barbaxa mana tsaba da rana.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Ya za mu yarda da wannan ta'asa,

Tsakaninmu na daxa givi da nisa,

Sun mai da mu akwashinsu na yasa,

Mutane ku lura, ku gane batuna.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa mu ne a rana.

Jagora: Ban yi musun lamarin duniya ba,

Akan duk ba za a kasance guda ba,

Amma ba zan qi a kyautata kar ba

Duk wanda ke sama, sun masa rana.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa, mu ne a rana.

Jagora: Allah Ka sa mu fahimta da sauri,

Mun tsinci kanmu a inda ke da tsauri,

Don dole ne mu ci kwakwa da bauri,

Kafin mu gyara batun da ke gabana.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa, mune a rana.

Jagora: Saqon da ke gaba sai ya fi nauyi,

In dai kuka qi bayanin da nayyi,

Allah Ka bani sukuni da rayi,

Nan zan rufe haka sai wata rana.

Amshi: Kada mu xauki siyasa da zafi, manyanmu na inuwa, mu ne a rana.

**Waqar Hawaye**

**Ta**

**Haruna Aliyu Ningi**

Jagora: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Amshi: Nijeriya ba badurwa ce ba yanzu.

Jagora: Iye

Amshi: Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Bismillah Allahu Mai Nijeriyata,

Amshi: Iye

Jagora: Kai Ne Ka samarta, har ma al'ummarta,

Amshi: Iye

Jagora: Kuma Kai kaxai ne, Ka gagari mai raba ta,

Amshi: Iye

Jagora: Addu'a muke yi, Ka sake haxe ta sosai, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Jagora: Iye

Amshi: Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: To, nai salati ga Mustafa, Xaha Manzo,

Amshi: Iye

Jagora: Ahali Sahabbansa su ma masu qwazo,

Amshi: Iye

Jagora: Wannan qasidar da za na yi, zanta yanzu,

Amshi: Iye

Jagora: Kuka take sani ba, murna nake ba, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Jagora: Iye

Amshi: Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Nijeriya dai qasa ce mai mutane,

Amshi: Iye

Jagora: Ga koguna tsaune, ga kuma ga bisashe,

Amshi: Iye

Jagora: Albarkatu ga su nan, na dubun qasashe,

Amshi: Iye

Jagora: Ita ce kaxai mai irin wannan ababe, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Sunanta dai Mango park ne yas saka shi,

Amshi: Iye

Jagora: Nijeriya ne da yaren Ingilishi,

Amshi: Iye

Jagora: Daga Naija kogi, ya samo salsalarshi,

Amshi: Iye

Jagora: Ai Eriyar Naija ne, Nijeriya xin, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe, shin me ya faru, iye.

Jagora: An ba mu ‘yanci na mulkin kai mutane,

Amshi: Iye

Jagora: Manyanmu sun taru kowa ya yi zaune,

Amshi: Iye

Jagora: Sun tsara komai da komai, sun yi zane,

Amshi: Iye

Jagora: Sun fara aiki na ci gaba manya manya, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma yana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Basu cimma buri ba, sai fitina ta sauka,

Amshi: Iye

Jagora: Rikici ya varke, kama da ruwa na kaka,

Amshi: Iye

Jagora: Daga nan qasar nan ta sauka baqar iyaka,

Amshi: Iye

Jagora: Wan tarihi ne da ban sha'awar tuna shi, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Daga nan ko murna ta qare sai hawaye,

Amshi: Iye

Jagora: Kuka muke yi qabila ko ta waye,

Amshi: Iye

Jagora: Wasu ‘yan tsirarun qasar nan wai gwanaye,

Amshi: Iye

Jagora: Sune suke sarrafa mu kamar tumakai, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amshi: Iye

Jagora: Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Mun samu mulki a gun ‘yan mallakar da,

Amshi: Iye

Jagora: ‘Yan mallakar yanzu sun fi na da ta’adda,

Amshi: Iye

Jagora: Sun zare kishinsu, sun ce ba shakka

Amshi: Iye

Jagora: An sa tunani kuwa Nijeriyata, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Tafiya muke yi a kurmi mai itace,

Amshi: Iye

Jagora: Kuma ga dare, ga ruwa maqil a kwance,

Amshi: Iye

Jagora: Kuma ga macizan ruwa da na kan itace,

Amshi: Iye

Jagora: Ga babu mai toci ko sandar riqewa.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe, shin me ya faru, iye.

Jagora: Tafiyar da yara da manya ga su barjak,

Amshi: Iye

Jagora: Tafiya da yunwa da sanyi sun yi cancak,

Amshi: Iye

Jagora: Guzurin tuwon ma kari xaya ne kawai rak,

Amshi: Iye

Jagora: Bai san taya za mu je mu garin zuwan ba, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Ku ga Indiyan yanzu nukiliya suke yi,

Amshi: Iye

Jagora: Pakistan har China, nukiliya suke yi,

Amshi: Iye

Jagora: Iran da Korea nukiliya suke yi,

Amshi: Iye

Jagora: Nijeriya babu lantarkin gwadawa, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amshi: Iye

Jagora: Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Wasu sun rabe ma, amma duk sun wuce mu,

Amshi: Iye

Jagora: Wasu nata yaqi, a ma har sun xara mu,

Amshi: Iye

Jagora: Wasu har da takunkumin ma, sun wuce mu,

Amshi: Iye

Jagora: Shin, me yake faruwa Nijeriyata, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: An zo bikin shekarunki na kai na hamsin,

Amshi: Iye

Jagora: ‘Yayanki sun yi miliyan xari da hamsin,

Amshi: Iye

Jagora: Shin kamfanoninki sun yi xari da hamsin,

Amshi: Iye

Jagora: Da suke da lebur dubu hamsin kowane, iye

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Amsarki na san ta ba sai kin faxi ba,

Amshi: Iye

Jagora: Ciwon da ke cin ki ba qarami ba ne ba,

Amshi: Iye

Jagora: Ranar da zai so ki ban ga tana zuwa ba,

Amshi: Iye

Jagora: Ni kam ina jin da qyar in za ki rayu, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Mamarmu Nijeriya ciwo take yi,

Amshi: Iye

Jagora: Shin polio ko diyabetis take yi,

Amshi: Iye

Jagora: Sida take koko dai kwalara take yi,

Amshi: Iye

Jagora: Ai fa corruption ina jin shi take yi, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Rashawa tana nan, da cin hanci yana nan,

Amshi: Iye

Jagora: Rikicin qabila da addini yana nan,

Amshi: Iye

Jagora: Ga cin amana da son kayi suna nan,

Amshi: Iye

Jagora: Ga karya dokar qasa, gun masu doka, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin meya faru, iye.

Jagora: Kuma ga siyasar ta'addanci da zamba,

Amshi: Iye

Jagora: Ga sace-sacen mutane ba a bari ba,

Amshi: Iye

Jagora: Cututtuka barkatai kuma ba a kula ba

Amshi: Iye

Jagora: Murna kike mama, ko kuka kike yi, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: In babu ci ai batun murna bula ne,

Amshi: Iye

Jagora: Kuma ga talauci yana ta tuqar mutane,

Amshi: Iye

Jagora: Ba ayyukan yi qasar duk ta gunane,

Amshi: Iye

Jagora: Varnar ina ji, iya sune suke yi, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amshi: Iye

Jagora: Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Amshi: Iye

Jagora: Nijeriyata

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: ‘Yanyanki dai yanzu sun mai da ke bauta,

Amshi: Iye

Jagoara: Bautar fari ma da ya kika sha bugunta,

Amshi: Iye

Jagora: Balle baqi, mai baqar aniyar mugunta,

Amshi: Iye

Jagora: Shi ne na ce mama ba murna kike ba, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Allah jiqan gamji Sardauna iyaye,

Amshi: Iye

Jagora: Da Tafawa Valewa da Azikwe, iyaye,

Amshi: Iye

Jagora: In na tuno Murtala sai nai hawaye,

Amshi: Iye

Jagora: Sun saddaqar da ransu don Nijeriya ne, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Ba za ni mance Aminu Kano ba baba,

Amshi: Iye

Jagora: Da su sir Akintola, shi ma bai haye ba,

Amshi: Iye

Jagora: ‘Yan son qasa, ba qabilanci suke ba,

Amshi: Iye

Jagora: Nan zan rufe tambarin kukan iyata, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Jagora: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye.

Amshi: Nijeriya ba budurwa ce ba yanzu,

Jagora: Iye

Amshi: Amma tana rarrafe shin me ya faru, iye

**Waqar Rigar 'Yanci**

**Ta**

**AbdulAziz Abdullahi Ningi**

Amshin baiti: Rigar 'yanci siyasa, an ba ta sunan qwarai,

Amma a Najeriya, an maida mu bayi.

Amshin xango: An ba ta sunan qwarai

Jagora: Bisimillah Ya Rabbana, Ya Jallah Sarkina,

Huwa Jalla, Ya Mai sama, Ya Mai dare, rana,

Huwa Rabbi Kai, Kai mani, baiwa a farkona,

Na sake roqo Ka ban ilmi a qarshena,

In sanar da Najeriya, bana lokaci ya yi.

Jagora: Farkon zuwan xan adam, ai mai raxin suna,

Bai ba dare xan adam, ko kuma xakin kwana,

Ba rashin a Najeriya, zam kamar vauna,

Kowa gudu nai yake, domin yana rana,

Sauyi a Najeriya, bana dole sai mun yi.

Jagora: Wannan dimukraxiyar, hanyar akwai kurxiya,

Da’awarsu kullum naxi, an tara ‘yan danniya,

Kuma babu mai dauwama, ko qara kwana xaya,

Nasabanta ba dole ne, gun mai rashin gaskiya,

Za mu wanke jumhuriyar, bana mai gaji ya yi.

Jagora: Ra’ayinka qaunar mutum, damarka ce xan-uwa,

Shin wane ne zai mana, ko zai idan yawa,

Ku zubar batun jam’iyya, ba ma qawancen qawa,

Kun daina bautar gumakai, ba mu bin wawa,

Sai wanda zai taimakawa, qasarmu in ya yi.

Jagora: Sha’anin Dimukrixiyyar, an maida shi cuxi,

Fasalin a Najeriya, ya zam kamar shinge,

Wadda bai cikin kewayen, sai dai a mar qage,

Motar dimukraxiyya, tayarta na goge,

Tibinta zai bindiga, wasu wa’adi ya yi.

Jagora: Manufar dimukraxiyyar, damar faxar kowa,

‘Yancinka ne xan adam, kai ra’ayin kowa,

In ba ka so babu tilas, ko gaban kowa,

Ra’ayinka tamkar ka qone, har da ba kowa,

Duk faxarsu ba yi ba ne, ra’ayinmu, sai mun yi.

Jagora: Ku masu kaunar naxi, bana babu mun farga,

A zuba, a zava, a kar, bana za mu ja daga,

Mu suturta jumhuriyar, damarmu ce danga,

Sun kar dimukraxiyyar, a qasarmu mucinga,

Tun tarihin duniya, ba a yin buhun qoyi.

Jagora: Duk wanda yai zai bari, har wadda bai zo ba,

Kuma shugaban bai yi ma, rai dukiya, xa ba,

Ba wadda zai sa ka yin, ra’ayin da bai ma ba,

Kuma babu mai sa ka son, mutumin da bai ma ba,

Wai don yana tutiyar, ya fi ka, sai ka yi .

Jagora: Ra’ayinka ne kar ka so, wani wadda bai ma ba,

‘Yancinka ne xan-adam, ka qi wadda bai ma ba,

Damar ka zavo mutum, wadda bai ta cuta ba,

Bana kar mu zavo mutane, masu qeta ba,

Ko za a harbe mu ne, ra’ayinmu sai mun yi.

Jagora: Mun kama bauta mu nai, kuma babu tsira ba,

Ba Annabawa ba ne, kuma ba sahabbai ba,

Balle mu ce za su kai mu, zuwa ga tsira ba,

Ba wadda zai ma karatu, ba da koyo ba,

Don mi muke bin su, mui ta zama na hawi.

Jagora: Mun bi su da mun gwada, ba su bar mugunta ba,

Wasu sun bi, sun sake bi, ba su anza riga ba,

Duk wadda yai kuskure, in ba dagangan ba,

Bai sake yin kuskuren, in ba da qeta ba,

Ya za mu zave su, sun kuma maida mu bayi.

Jagora: In ba butulci ba kai, ko nuna wauta ba,

Ya zan ci naman kare, kuma ga na rago ba,

Ya mai ido zai shiga, garken makafi ba,

Sauyi muke so matasa, ban da tsoro ba,

Na arewa an kakkave mu, cikin ruwan sanyi.

Jagora: In ba da wauta ba, shirme, ko rashin kai ba,

Ya zan ta bin wadda, bai so na da hutu ba,

Kuma ba ya qaunar a ce, na canza riga ba,

Mu fito da qwai, da kwarkwatarmu, zuwa ga bore ba,

Zave a Najeriya, bana babu mai sanya.

Jagora: An mai da mu sai bara, wasu na bixar qanzo,

Ba a kusantar mu ma, sai in wuya ta zo,

Kuma ba mutum xan adam, mai maganin qozo,

Bana ba mu bin mai abawa, mai zare ya zo,

‘Yancinmu rigarmu ce, bana lokaci ya yi.

Jagora: Kimar mutum xan adam, an yi ta mai girma,

Kaf, yau cikin duniya, an san mu, mun girma,

Ga dukiya kaf, a yave, qasarmu kwai dama,

Yau ga shi Najeriyar, talakanmu na fama,

Domin rashin shugabanci, dole mui sanyi.

Jagora: An sha da mu manguna, bakinmu na xaci,

Matar da ke naquda, ai ba ta ma barci,

Duk wadda ke yin fito, gurinsa ya kai gacci,

Yau ga shi Najeriya, mara shi baya barci,

Tsananin rashi babu kansa, tauna qwayoyi.

Jagora: Yar kaf, cikin duniya ko da a Turanci,

Shi ko da mai ba da kyautar ransa har zuci,

Don daxaxawar waninsa, da nasa na qunci,

Juyi a Najeriya, yau ba mu yin sakkaci,

Ko za a maishe mu toka, namu sai ya yi.

Jagora: Mu ba wakilai ba ne, mu ba jakadu ba,

Ba shugabanni ba ne, mu ba sarakai ba,

Mutuwarmu ko yau ta zo, mu ba mu tsoro ba,

Su ne suke qin ta, don sun sanda horo ba,

Amma suke cin haqqinmu, da dukiya nauyi.

Jagora: Bai xan-adam martaba, bai zam da laifi ba,

Amma ka bauta masa, ba a ba ka dama ba,

Tsoronsa tamkar maqagi, bai da rana ba,

Bai bar abin duk da bai, ya halatta kai mar ba

Don son abin duniya, ka kauce ayoyi

Jagora: Ladabi, biyayya da kyau, in ba rashin gaskiya,

Za kai wa babban mutum, mai son faxar gaskiya,

Ra'ayinka ko naka ne, ba mai yi ma danniya,

In shugaba dole ne, in yai rashin gaskiya,

Ko shi yake ci da kai, ka canza hanyoyi.

Jagora: Jama'a ku zo nai kira, ra'ayinmu, sai mun yi,

Don me a Najeriya, za a mai da mu bayi,

Bana ba mu qaunar naxi, kuma lokaci ya yi,

Duk wanda zai murxe zave, mu qona tayoyi,

Shi ne dimukraxiyyar, damarmu sai mun yi.

Jagora: Ba yadda za ai kashi, bai zam kamar gyara,

Wadda an yi mar zalu kam, tilas ya kai qara,

Duk wadda yai kuskure, tilas a mar gyara,

An xaura aure, waliyyai na jiran gara,

Wasu sun tsaye kan kwana, an toshe hanyoyi.

Jagora: Yanayin dimukraxiyyar, ya canza'yar lale,

Duk wadda zai yai shirin, zai zo da xan falle,

Ko da kamar hankicif , zai zo xan qyalle,

Don goge dattin a da, da za mu zuba cikin talle,

Don gyara Najeriya, bana lokaci ya yi.

Jagora: Ita duniya hira ce, wasu har da tabarma,

Cin duniyar ya musu, sun xora bargo ma,

Sun shimfixa, sun baje, kar wadda zai hau ma,

Su ji suke sun haye, sun tara mai dama,

Da can fa kamun ku yi, asu sun riga sun yi.

Jagora: Su ji suke sun buge, hagu har zuwa dama,

Kuma ba su qaunar ce wani ma yana nema,

Wata ran da ku za a je roqon su alfarma,

Don lokacin ba ku yi, kun tsufa ga girma,

Allah Yake ba mutum, in lokaci ya yi.

Jagora: In ba a xauke gula, kuma ba kwa hau ba,

Na gabanku da sun riqe, kuma ba kwa zo ba,

Sun fi ku ma kyautatawa, ba varayi ba,

Kuma ba su qyashi da qetar, qulla gaba ba,

Yau ga shi duk sun tafi , sauran ku awoyi.

Jagora: Huwa Rabbi Mai zamani, ba yadda bai yi ba,

Ranar zuwa duniya, zir babu wando ba,

Wani na gani sai a qarshe, zai makance ba,

Wani ko yana ji, a qarshe bai da kunne ba,

Yanayin zaman duniya, an ba da ayoyi.

Jagora: Amma mutum martaba, a cikin halittu ma,

Ko da zaman duniya, an ba mu alfarma,

Yatsunka kwai qanqane, kuma har da mai girma,

Don ci da kai, sha da kai, ma dole mui fama,

Gyaran dimukraxiyyar, bana lokaci ya yi.

**Waqar Almajiri**

**Ta**

**Muhammad Sani Aliyu**

Jagora: Almajiri baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Amshi: Almajirin baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Jagora: Xan almajiri da allo

Amshi: Maula

Jagora: Ku xan tausayawa qolo

Amshi: Maula

Jagora: Wa za ya ba shi riga

Amshi: Maula

Jagora: Wa za ya ba shi wando

Amshi: Maula

Jagora: Ruwa ba shi za ya karva

Amshi: Maula

Jagora: Sauran gida ya sharva

Amshi: Maula

Jagora: Idan yara sun yi saura

Amshi: Maula

Jagora: Don kar a kai a shara

Amshi: Maula

Jagora: Abun nan ku qara lura

Amshi: Maula

Jagora: Mu duba, mu qara gyara

Amshi: Almajiri baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi a kan rayuwa ta almajiri.

Jagora: Allah Mai dare da rana, Ubangijin xan gari da baqo

Amshi: Maula

Jagora: Mai ci da mai iyaye, mai ba almajiri da qoqo

Amshi: Maula

Jagora: Mannanu Jallah Rabbi, Kai ke ba dukka masu roqo

Amshi: Maula

Jagora: Na xauka hannuwana, kama min in isar da saqo

Amshi: Maula

Jagora: Na lura dole mui waiwaye akan rayuwa ta almajiri

Amshi: Almariji baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Jagora: Ya Allah Ka yo salati, qara daxawa ga Xaha Manzo,

Manzon da Ya zarce kowa, a martaba, qoqari da qwazo,

Annabi na so ka na yi dace, sai lamura ke ta qara wanzo,

Turbarka na tsaya, ba ni turuwa, Sidi ba na darzo,

Tsamar da mu masifa, Ilahu tsamar da mu akan haxxari.

Amshi: Almajiri baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Jagora: Allah a cikin Salatinka sanya Alaye da Sahabbai,

Amshi: Maula

Jagora: Kalle su ba su wasa, gun yaqi sun ka xau takubbai,

Amshi: Maula

Jagora: Su ne jaruman da ke wa kafirai raunuka da tabbai,

Amshi: Maula

Jagora: Har Auliya'u masu sadaukarwar rayuwa da kwabbai,

Amshi: Maula

Jagora: Haka na jinjina gurin malaman da ke ba mu tarbiyya ta gari.

Amshi: Almajiri baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Jagora: Jama'a yau gani da sabon zance, zan so ku bi ni sannu

Amshi: Maula

Jagora: Akn rayuwa ta almajirai, nake son na yo bayanu

Amshi: Maula

Jagora: Domin na ga ba a tsawurta tilas sai cikin idanu

Amshi: Maula

Jagora: Zan warware abawa, in buxe yadda za ta tonu

Amshi: Maula

Jagora: In qarqare ta, in warware ku gane abin cikin zahiri

Jagora: Almajiri bara, shi mutun gari ke kira da qolo

Amshi: Maula

Jagora: Gaishe da kai baran malami da ke kwalliya da allo

Amshi: Maula

Jagora: Mai shan fura da tsami, ko da ya don karin kumallo

Amshi: Maula

Jagora: Mai yawo da xaura tsumma, su al'umma su dinga kallo

Amshi: Maula

Jagora: Abin tausayi, abin qaiqayi irin rayuwa ta almajiri

Amshi: Almajiri baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Jagora: Almajiri abin tausayi, makwancinka za a kalla

Amshi: Maula

Jagora: Sai mai shimfixar kwali, ko keso, mai filo da hula

Amshi: Maula

Jagora: Cinkoso, matsotso, lallai sha'anin ya saka ni qwalla

Amshi: Maula

Jagora: Kai mai gardama taho, leqa makarantar su Shehu Kalla

Amshi: Maula

Jagora: Wannan lamari mu duba, mu tausaya rayuwa ta almajiri

Amshi: Almajiri baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Jagora: Ga kwarkwata, qudan cizo, an turo shi yai karatu,

Fama yake da datti, ba natsuwa in yana karatu,

Ya je gari bara, an ci an rage, qila ya wadatu,

In babu natsuwa, ba wadatuwa ya ake karatu,

Kai mui nazari, mu duba, mu bincika, kuma mu gyara al'amari.

Amshi: Almajiri baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Jagora: Qur'ani abin riqewa da daraja gun dukkan musulmai

Amshi: Maula

Jagora: Haba mun qyake masu nema na ilmi da saninsa qazamai

Amshi: Maula

Jagora: Boko ake ma bauta, a yi tsaf-tsaf don harin muqamai

Amashi: Maula

Jagora: Haba al'umma mu juyo ma gaskiya don mu san karamai

Amshi: Maula

Jagora: Mu dawo, mu duba al'amarin, mu gyara wa namu almajiri

Amshi: Maula x3

Amshi: Almajiri baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Jagora: Musulunci mu bincika yai hani mu zauna cikin qazanta

Amshi: Maula

Jagora: Sannan ya ba mu 'yanci mu bi Allah, mu huta da bauta

Amshi: Maula

Jagora: Ma'ana kar mu xauki qasqanci, kai Allah Yana da kyauta

Amshi: Maula

Jagora: Rayuwar nan irin ta almajiri, mu duba, mu daina qeta

Amshi: Maula

Jagora: Mu gyara, mu taimaka, kar mu bai suna tangaririya a gari

Amshi: Almajiri baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Jagora: Abin nan akwai takaici, abin yana qara ba ni tsoro

Amshi: Maula

Jagora: Mun bar abin da Allah Ya ce, kamar yin hani da horo

Amshi: Maula

Jagora: Mun rayu sasakai, maqiyanmu kullum suna hararo

Amshi: Maula

Jagora: Mu ke da xaukaka, mun zamo kamar ‘yan baran da qyauro

Amshi: Maula

Jagora: Haba al’umma ana raina mu akan rayuwa ta almajiri

Amshi: Almajiri baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al’umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri

Jagora : Qur’anu mu mai da shi mai girma, kul kar mu bar shi yashe

Amshi: Maula

Jagora: Malamai masu koya shi, mu riqe su da girma a kodayaushe

Amshi: Maula

Jagora: Su zamto cikin wadata, mu ba su kurxi kamar adashe

Amshi: Maula

Jagora: Ma’ana sadaka da kyauta, mu rinqa yi kar mu bar su qunshe

Amshi: Maula

Jagora: Haka nan shi uba ya ba, malaman da ke yin kula da almajiri

Amshi: Almajiri baran malami, na malam gajere dodn tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Jagora: Duba kar ka tura yaro xan qarami, wanda bai da wayo

Amshi: Maula

Jagora: A watsar cikin gari, ba uwa, uba har ya dinga wayyo

Amshi: Maula

Jagora: Ba ka san ci da shan shi ba, ilmin da kake so ya rinqa koyo

Amshi: Maula

Jagora: Ba ka ba malaminsa ba, wata lada na yo kiranka juyo

Amshi: Maula

Jagora: Uban xa, da mai riqon xa, ku yi tunani ga wanga al'amari

Jagora: Ina yin kira ga masu kuxi, kai kuma ku sanya tausai

Amshi: Maula

Jagora: Ku kai taimako wurin makarantun allo, ku ba su sosai

Amshi: Maula

Jagora: A samu waxansu su kai abinci, da tabarmi da matassai

Amshi: Maula

Jagora: Kayan da za su sanya, a ba su sabullai da kilissai

Amshi: Maula

Jagora: Lallai al'umma akwai falala cikin taimaka wa almajiri

Amshi: Almajiri barab malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri

Jagora: Abincin da ba mu so, kar mu ba su, Allahu Shi Ka cewa

Amshi: Maula

Jagora: Lantandu lil birra hatta tun fiqu, ida qarasawa

Amshi: Maula

Jagora: Imma tuhibbu kenan, da ka fi so, shi kake ciyarwa

Amshi: Maula

Jagora: Almajiri ka zo ga abinci mai kyau, na ba ka nawa

Amshi: Maula

Jagora: Irin haka ne ake so, ga masu son tausaya wa almajiri

Amshi: Almajiri baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri

Jagora: Babu sauran su nemi qanzo, a ba su mai kyau qwarai da gaske,

Ko xan dago-dago, xan tsaki-tsaki nan akai shi wanke,

Sannan a ba su kaya, sui fes wanka jikinsu warke,

Sai su bar tangaririya kan titi, nauyi ku zo mu sauke,

In mun hakan muna taimaka wa kai, taimako na almajiri.

Amshi: Almajiri baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta lmajiri.

Jagora: Almajiri bara, shi mutan gari ke kira da qolo

Amshi: Maula

Jagora: Gaishe da kai baran malami da ke kwalliya da allo

Amshi: Maula

Jagora: Mai shan fura da tsami, ko da ya don Karin kumallo

Amshi: Maula

Jagora: Mai yawo da xaura tsumma, su al'umma su dinga kallo

Amshi: Maula

Jagora: Abin tausayi, abin qaiqayi irin rayuwa ta almajiri

Jagora: Gyara kayanka bai zama sauke mu raba, in ji masu zance

Amshi: Maula

Jagora: Mai son ya gane hanya, ba ya gudun masu yin kwatance

Amshi: Maula

Jagora: Mai sayyidil wara Muhammad Sani ga shi zan taqaice

Amshi: Maula

Jagora: Allah Ubangiji na yi addu'a qara ba mu dace

Amshi: Maula

Jagora: Allahu Jalla Kai tallafi akan rayuwa ta almajiri

Amshi: Almajiri baran malami, na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Amshi: Maula x3

Amshi: Almajiri baran malami na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Jagora: Xan almajiri da allo

Amshi: Maula

Jagora: Ku xan tausaya wa qolo

Amshi: Maula

Jagora: Wa za ya ba shi riga

Amshi: Maula

Jagora: Wa za ya ba shi wando

Amshi: Maula

Jagora: Ruwa ba shi za ya karva

Amshi: Maula

Jagora: Sauran gida ya sharva

Amshi: Maula

Jagora: Idan yara sun yi saura

Amshi: Maula

Jagora: Don kar a kai a shara

Amshi: Maula

Jagora: Abin nan ku qara lura

Amshi: Maula

Jagora: Mu duba mu qara gyara

Amshi: Almajiri baran malami na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan ta almajiri.

Jagora: Almajiri baran malami na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi akan rayuwa ta almajiri.

Amshi: Almajiri baran malami na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi a kan rayuwa ta almajiri.

Jagora: Ya al'umma mu sa tausayi a kan rayuwa ta almajiri

Amshi: Ya al'umma mu sa tausayi a kan rayuwa ta almajiri

J/A: Almajiri baran malami na malam gajere dodon tsaki,

Ya al'umma mu sa tausayi a kan rayuwa ta almajiri.